# GUDUNMUWAR SAMANJA MAZAN FAMA WAJEN BUN{ASAR WASAN KWAIKWAYO: NAZARI KAN WASU WASANNINSA.

**NA**

**RILWANU TANIMU UMAR**

**MA/ARTS/42247/2004-2005**

**MA/ARTS/9628/2009-2010**

**THE THESIS SUBMITTED TO THE POST GRADUATE SCHOOL, AHMADU BELLO UNIVERSITY, IN PARTIAL FULFILLMENT FOR THE AWARD OF M.A DEGREE IN AFRICAN LANGUAGES AND CULTURE (HAUSA)**

**DEPARTMENT OF AFRICAN LANGUAGES AND CULTURES**

**JUNE,2011**

## TAKARDAR AMINCEWA.

Wannan bincike mai taken **"GUDUMMUWAR SAMANJA MAZAN FAMA WAJEN BUN{ASAR WASAN KWAIKWAYO: NAZARI KAN WASU WASANNINSA".**

Wanda aka gudanar }ar}ashin jagorancin kulawar Prof. Dalhatu Muhammad da Dr. Magaji Tsoho Yakawada, mallaka na ne kuma gudummuwa ce ga nazarin Adabin Hausa, musamman ~angaren wasan kwaikwayo, sannan kuma, wannan bincike mai wannan taken ba a ta~a gudanar da shi ba a matakin digiri na biyu ko waninsa a fagen ilimi cikin Jami'o'in cikin gida ko na }asar waje.

Rilwanu Tanimu Umar ……………………

## CERTIFICATION

This Thesis entitled, "**GUDUMMUWAR SAMANJA MAZAN FAMA WAJEN BUN{ASAR WASAN KWAIKWAYO: NAZARI KAN WASU WASANNINSA**" by Rilwanu Tanimu Umar meets the regulations governing the award of the degree of masters of Arts in African Languages (Hausa) in the Department of African Languages and Culture, Ahmadu Bello University, Zaria, and is approved for its contribution to knowledge and literary presentation.

------------------------------- --------------------------

Prof. [alhatu Muhammad Date

Chairman, Supervisory Committee

------------------------------- --------------------------

Dr. Magaji Yakawada Tsoho Date

Member, Supervisory Committee

------------------------------- --------------------------

Dr. Muhammad L. Aminu Date

Head of Department

------------------------------- --------------------------

Prof. Adebayo A. Joshua Date

Dean, Postgraduate School

# GODIYA

Da sunan Allah ma]aukakin sarki mai kowa mai komai, dukkan godiya da yabo sun tabbata ga mai rahama mai jinkai. Tsira da amincin Allah sun tabbata ga Shugaban Halitta Jagorar Annabawa kuma za~a~~en abin halitta Annabi Muhammadu (S.A.W).

Bayan godiya ga Allah da ya ba ni ikon aiwatar da wannan binciken na fagen Ilimi, ina mi}a godiyata ga dukkannin malamaina wa]anda suka ba da tasu gudunmuwa wajen cimma nasarar wannan aikin har ya zama haka. Ina mi}a godiyata ta musamman ga jagoran kulawa da wannan aiki Prof. Dalhatu Muhammad da Dr. Magaji Tsoho Yakawada dangane da irin gagarumin gudummuwa da karfafa gwuiwar ganin cimma nasarar wannan aikin. Haka nan kuma godiya ta musamman ga shi wanda aka aiwatar da binciken a kan ayyukansa, watau, Samanja Mazan Fama (Usman Baba Pategi) dangane da irin goyon bayan da ya ba da wajen samun nasarar aikin da Mal. Musa Ibrahim na gidan Rediyon Tarayya (F.R.C.N) Kaduna wanda shi ma ya ba da tasa gudummuwar.

Godiya ta ga wa]annan mutanen Dr. Balarabe Abdullahi da Malama A'isha U. Wali da dukkanni sauran Malaman Sashen Hausa na Kwalegin Ilmi ta Tarayya da ke Zariya (F.C.E) da Abokaina da sauran 'yan uwana maza da mata dangane da irin shawarwarin da suka ba ni musamman a fagen Ilimi, da kuma wa]anda suka yi hidimar ]abba'a wannan kundin aikin nawa. Na gode. Allah ya sakawa kowa da Alherinsa Amin.

Rilwanu Tanimu Umar ……………………..

**ABSTRACT.**

This work was conducted in the field of Hausa literature, in the area of written drama that was written, played and replayed in many media houses especially the Federal Radio Corporation of Nigeria (F.R.C.N) Kaduna. The research was on a renowned actor and play write who has written and performed in many of these plays. This person is no other than the famous Samanja Mazan Fama.

In this research, some of the plays he has written and participated in, and aired to the teeming interested audience, were selected and studied in six different perspectives that affected Houseman's life. There include his education, religion, politics, culture, economy and way of living. The whole work was in five chapters. Chapter one included introduction, statement of the of the problem, objective and the significance of the research. It also included the hypothesis as well as the history of Hausa drama in redio houses and the biography of Samanja. The chapter two discussed the literature review, that is, works carried out by other authors that are related to the research topic. Chapter three looked at the contributions given by Samanja Mazan Fama in the areas of education, religion and politics in the plays he has written and acted in. in chapter four, the research studied culture, economy and togetherness from some of his selected plays. The themes of the plays were also studied. And followed by the references and the appendix that contains the list of cassettes that were used during the course of this research all in *Duniya Budurwar Wawa*.

## TSAKURE.

Wannan aikin an gudanar da shi a ~angaren Adabin Hausa, ta fuskar wasan kwaikwayo wanda aka rubuta kuma aka aiwatar, a inda aka ]auko wani gwarzon ]an wasan kuma marubucin wasan kwaikwayon da ake ya]awa a kafafen ya]a labarai musamman gidan Rediyon Tarayya (F.R.C.N) Kaduna. Wannan Gwarzon ]an wasan shi ne Samanja Mazan Fama.

A wannan binciken an ]auki wasu daga cikin wasannin da ya rubuta kuma aka aiwatar da su ga jama'a masu sha'awa da sauraron wasannin kwaikwayo aka nazarce su ta fuskoki shida da suka shafi rayuwar Hausawa kamar Ilimi da Addini da Siyasa da Al'ada da Tattalin arzi}i da kuma Zamantakewa. Wannan kundin ya }unshi Babi biyar ne. Babi na ]aya ya }unshi gabatarwa ne game da wannan aikin da dalilan gudanar da wannan binciken. Haka nan kuma a wannan babin ne aka yi bayanin manufar aiwatar da binciken da ma farfajiyan wannan binciken tare da muhimmancin gudanar da wannan binciken a fagen Adabin Hausa da irin hasashen binciken da tarihin wasan kwaikwayo a gidan rediyo da tarihin marubucin wasannin da aka gudanar da binciken, wato Samanja. Sai kuma Babi na biyu wanda a cikin sa ne aka dubi ayyukan da suka gabata masu ala}a da wannan kundin ta fuskar Adabi musamman ~angaren wasan kwaikwayon Hausa, ala}ar na iya kasancewa ta kusa ko ta nesa a fagen Adabin don sanin makaman aiki. Babi na uku ya }unshi gudummuwarsa ne ta fuskokin uku kamar Ilimi da Addini da Siyasa da aka bi wajen gudanar da wannan bincike har ya kawo ga wannan matsayin. A babi na hu]u kuwa nan ne aka gabatar da nazarin da suka shafi Al'ada da Tattalin arzi}i da Zamantakewa daga cikin wasu wasannin da ya rubuta aka aiwatar. Sannan aka yi nazarin jigon wasannin da aka aiwatar da binciken. Babi na biyar nan ne aka na]e wannan aikin da kammalawa tare da manazarta da ratayen kaset-kaset da aka

sauraresu da kuma wasannin da aka aiwatar da nazarin wajen cimma nasarar wannan binciken har ya kawo wannan matakin.

**ABUBUWAN DA KE CIKI**

Taken aiki:………………………………………………………. i

Takardar amincewa:…………………………………………. ii

Godiya:…………………………………………………………. iii

Certification:……………………………………………………… iv

Abstract:……………………………………………………….. v

Tsakure:……………………………………………………….. vi

Abubuwan da ke ciki:………………………………………. viii

**BABI NA FARKO: SHIMFI[A.**

1.0 Gabatarwa……………………………………………………. 1

1.1 Dalilan Gudanar da Binciken……………………………………. 3

1.2 Manufar Binciken……………………………………………. 4

1.3 Farfajiyar Binciken…..………………………………………. 5

1.4 Muhimmancin Binciken. ……………………………………. 6

1.5 Hasashen Bincike:…………………………………………… 7

1.6 Tarihin Wasan Kwaikwayon Rediyo:………………………… 7

1.7 Ta}aitaccen Tarihin Alhaji Usman Baba Pategi (Samanja Mazan Fama):…………………………………………………….. 9

1.8 Hanyoyin Gudanar da Bincike:………………………………13

1.9 Kammalawa:…………………………………………………….15

**BABI NA BIYU: WAIWAYEN AYYUKAN DA SUKA GABATA**

2.0 Gabatarwa:……………………………………………………..16

2.1 Ayyukan da Suka Gabata:…………………………………...16

**BABI NA UKU:GUDUMMUWARSA A FANNIN ILIMI DA ADDINI DA SIYASA.**

3.0 Gabatarwa………………………………………………… 24

3.1 Ma'anar Ilimi:…………………………………………….. 26

3.2 Muhimmacin Ilimi da Tasirinsa ga Bahaushe:……………… 26

3.3 Wasannin da Suke {unshe da Ilimi a Cikin Wasanin Duniya Budurwar Wawa:……………………………………… 26

3.4 Ma'anar Addini:……………………………………… 31

3.5 Muhimmacin Addini da Tasirinsa ga Bahaushe:……….. 31

3.6 Wasannin da Suke {unshe da Addini a Cikin Wasannin Duniya Budurwar Wawa:…………………………… 31

3.7 Ma'anar Siyasa:……………………………………….. 37

3.8 Muhimmacin Siyasa da Tasirinta ga Bahaushe:………... 37

3.9 Wasannin da Suke {unshe da Siyasa a Cikin Wasannin Duniya Budurwar Wawa:……………………………………… 37

3.10 Kammalawa:…………………………………….…. 50

**BABI NA HU[U: GUDUMMUWARSA TA FANNIN AL'ADA DA TATTALIN ARZI{I DA ZAMANTAKEWA.**

4.0 Gabatarwa:…………………………………………….. 51

4.1 Ma'anar Al'ada:………………………………………... 51

4.2 Muhimmacin Al'ada da Tasirinsa ga Bahaushe:…………... 52

4.3 Wasannin da Suke {unshe da Al'ada a cikin Wasannin Duniya Budurwar Wawa:…………………………………….. 52

4.4 Ma'anar Tattalin Arzi}i:…………………………….... 54

4.5 Muhimmacin Tattalin Arzi}i da Tasirisa ga Bahaushe:…... 54

4.6 Wasannin da Suke {unshe da Tattali Arzi}i a Cikin Wasannin Duniya Budurwar Wawa:……………………………….. 54
4.7 Ma’anar Zamantakewa:…………………………………….. 57
4.8 Muhimmacin Zamantakewa da Tasirinta ga Bahaushe:…... 58
4.9 Wasannin da Suke {unshe da Al’amuran Zamantakewa a Cikin Wasan Duniya Budurwar Wawa:……………………………58
4.2.0 Ma’anar Jigo:…………………………………………………74
4.2.1 Jigon “Kowa ya bar gida…”a Wasan Duniya Budurwar Wawa:…………………………………………………..75
4.2.3 Jigon “Mutum sai Allah” a Wasan Duniya Budurwar Wawa:……………………………………………..….77
4.2.4 Jigon “Rayuwa” a Wasan Duniya Budurwar Wawa:…………………………………...……………78
4.2.5 Jigon “Jahilci Ciwo” a Wasan Duniya Budurwar Wawa:……………………………………………..……79
4.2.6 Jigon “Mutuwar Zuciya” a Wasan Duniya Budurwar Wawa:…………………………………………………80
4.2.7 Kammalawa:…………………………………………81

**BABI NA BIYAR: NA[EWA**

5.0 Gabatarwa:…………………………………………..... 82
5.1 Abubuwan da Suka Gudana a Ta}aice:……………………… 82
5.2 Abubuwan da Aka Gano:…………………………………….. 84
5.3 Shawarwari:………………………………………………… 85
5.4 Kammalawa ……………………………………………….. 86
**MANAZARTA**……………………………………........... 88

## RATAYE NA [AYA

1. Jerin Kaset da aka Saurara:……………………………… 93

## RATAYE NA BIYYU

2. Wasannin da aka Gudanar da Bincike

(i) Wasan "Kowa ya bar gida…"a Wasan Duniya Budurwar Wawa:…………………………………………………… 97

(ii) Wasan kwaikwayon "Mutum sai Allah" a Wasan Duniya Budurwar Wawa:………………………………………… 126

(iii) Wasan kwaikwayon "Rayuwa" a Wasan Duniya Budurwar Wawa:…………………………………………………. 173

(iv) Wasan "Jahilci Ciwo" a Wasan Duniya Budurwar Wawa:... 195

(v) Wasan "Mutuwar Zuciya"a Wasan Duniya Budurwar Wawa: 215

SADAUKARWA.

## Wannan aiki na sadaukar da shi ga iyayena da iyalaina da dukkan ‘yan uwana maza da mata da abokaina

## BABI NA FARKO SHIMFI[A:

### 1.0 Gabatarwa.

Wannan bincike ya kunshi nazari ne a fagen adabin Hausa, ta fuskar wasan kwaikwayo, a inda aka nazarci ayyukan wani ]an wasa, a matsayinsa na murubucin wasan kwaikwayo, tare da ire-iren wasannin da ya rubuta. Manazarta sun yarda da wasan kwaikwayo wani yanki ne mai cin gashin kansa, kuma ginshi}i ne mai zaman kansa a rabe-raben da su ka yi na adabin Hausa, baya ga zube da wa}a. Shi kansa wasan kwaikwayon ya kasu gida biyu wato akwai, na baka, ko na gargajiya, da na zamani. Kafin a tsunduma a fagen nazari zai kyautu a ]an }yallaro wani abu daga cikin abin da masana suka ambata game da ma'anar wasan kwaikwayo.

Masana Adabi, musamman ~angaren wasan kwaikwayo, sun ba da gudummuwa da dama. Cikinsu akwai shahararren masanin nan mai suna Crow, (1983:2) wanda ya ce: "wani irin wasa ne, a inda mutane kan kwaikwayi wasu mutane ko wasu abubuwa dangane da halayensu ko irin abubuwan da suke gudanarwa. Ana yin wannan don nisha]antarwa". Su kuma masana Adabin Hausa, musamman wasan kwaikwayo ga abin da suke cewa:

Ahmad,(1985:4-5) a nasa gudummawar ya ce "shi ne, duk wata matsalar wasa da ta }umshi abu biyu, na farko dai ta zamo wasa ne, wanda yake ba gaskiya ba ne lokacin da ake abin, na biyu shi ne wasan ya zama ma}asudinsa na sake kama ne. To, wajen sake kaman nan, mai wasan, ko `yan wasan za su canza kamanninsu na yau da kullum".

Yahaya, (1986:2) ya ce: "Ko da jin sunansa ma, wasan kwaikwayo ya rigaya ya bayyana kansa. Wato akwai alamun wasa,watau abin da yake raha, akwai kuma alamun kwaikwayo, don kwatanta yadda ake yinsa, don wani

ya gani ko wa]ansu su gane kyansa ko muninsa. Wannan ma'ana da ta rataya da sunan wasan kwaikwayo, tana da ala}a da ma'anar 'drama' ko 'play', wato sunan da Turawa suka ba wasan kwaikwayo domin kalmar 'drama' ko 'play', suna nuni ne da aikata wani abu musamman ma a dandamali domin ya sa nisha]i ga masu kallonsa ko ya ]aga musu hankali, ko ya koyar da su wani abu."

Shi kuma [angambo, (1984:141) a tasa ma'anar ya ce "wasan kwaikwayo, kamar yadda sunan ya nuna, wasa ne da ake gina shi kan kwaikwayon wani labari, ko wata matsala ta rayuwa da ake son nusarwa ga jama'a. A kan aiwatar da labarin matsalar, da sauransu cikin siffar "ya}ini", wato zahiri. Za'a iya karkasa wasan kwaikwayo zuwa kamar kashi biyar, dangane da kafofin isar da sa}on ko aiwata shi kamar haka:

i. Rubutaccen Wasan kwaikwayo; wannan shi ne, wanda ake rubuta wa a littattafai don karantawa.

ii. Wasan kwaikwayo na rediyo; wanda ake watsawa a rediyo don sauraro.

iii. Na Dandamali; Wanda ake aiwatarwa a zahiri don a kalla kuma a ji.

iv. Na siliman/majigi; wanda ake mai da shi fim wanda ake nunawa a silima ko majigi ana yawo da shi wuri-wuri.

v. Wasan kwaikwayo na Talebijin; Wanda ake nunawa a gidan Talebijin.

Mai nazari na ganin a iya ba da ma'anar wasan kwaikwayo da cewa hanya ce ta isar da sa}o ko manufa a cikin aikataccen lamari na yin amfani da harshe da wasu ~angare daga cikin jiki da nufin isar da sa}o don ilmantarwa ko fa]akarwa ko nisha]antarwa, ga jama'a masu sha'awar kallon wasan kwaikwayo ko sauraronsa ko kuma karanta shi a rubuce. Mun ga ma'anar wasan kwaikwayo yadda masana su ka ambata. Bincike zai

ta'alla}a ne, ta fuskar za}ulo ayyukan wannan gwarzon ]an-wasa wan]anda ya rubuta, aka aiwatar, musamman a gidan Rediyon Tarayya na Kaduna. Haka nan kuma za a dubi ta}aitaccen tarihin rayuwarsa, da kuma yadda ya fara shiga harkar wasan kwaikwayo, da yin nazarin ire-iren wasannin da ya rubuta su a matsayinsa na fitaccen ]an-wasa, tare da yin la'akari da gudunmuwarsa wajen rubuta wasannin kwaikwayo, da ake gabatarwa a kafafen ya]a labarai musamman, Rediyo Tarayya Kaduna, (F.R.C.N) ta yin nazarin irin basirar da hikimar da Allah ya yi masa ta wajen }ir}ira da rubuta wasannin da ake gabatarwa, kusan a mako sau biyu a gidan rediyon Kaduna.

**1.1 Dalilan Gudanar da Bincike.**

Kowane abu da ]an-Adam kan yi ta fuskar ilimi, wajen gudanar da bincike yana da dalilansa. To, a nan dalilin yin wannan bincike shi ne, ganin yadda masana da manazarta da ]alibai wajen taron }ara wa juna ilimi a mataki daban-daban sun yi ta ba da tasu gudunmuwar, wajen rubuce-rubuce da dama a wannan fagen adabin Hausa musamman a ~angaren wasan kwaikwayo shi yasa na ga ya dace da in ba da tawa gudummwar, ta wani, gwarzo kuma fitaccen ]an-wasan kwaikwayo, kuma murubucin wasan kwaikwayon, da ake gabatarwa a kafafen ya]a labarai musamman, Rediyon Tarayya Kaduna, (F.R.C.N) ta yin nazarin irin basirar da hikimar, da Allah ya yi masa ta wajen }ir}ira da rubuta wasannin da ake gabatarwa, kusan a mako sau biyu a gidan rediyon Kaduna.

Wani dalilin kuma shi ne, masana da masu bincike sun yi ta ba da tasu gudummawar a wannan fage na wasan kwaikwayo, sai dai a wani ~angare ne suke ta taka tasu rawar, to amma basu zurfafa ba wajen samun wani fitaccen marubucin wasan kwaikwayo a kafar ya]a labarai, su gudanar da nazarin a kansa, da irin rawar da ya taka wajen bun}asa wannan fage na

adabin Hausa, ta kafar ya]a labarai musamma ta wajen nazarin rubutattun wasanninsa da ya rubuta wanda ake ya]awa ga jama'a masu sauraron Rediyo. Sai dai kuma kash! wasu daga cikin masu binciken irin wannan sun gudanar da nasu ta ba da gudummuwarsu musamman a wannan fage na Adabin wasan kwaikwayo, to amma ta fuskar ]auko gwarzo a matsayinsa na ]an-wasa suka yi nazarin aikace-aikacensa, ta fuskar ire-iren wasanninsa da ya aiwatar ba wanda ya rubuta ba, a matsayinsa na marubucin wasa.

Wani dalilin gudanar da wannan bincike a wannan fannin na adabin Hausa ~angaren wasan kwaikwayo da ake gabatarwa a gidajen ya]a labarai shi ne, sha'awar `wasannin da ake gudanarwa ta kowane fanni ko a Dandamali ko a Talbijin ko a Rediyo. Ballantana a yanzu da zamani ya kawo sabon salo wajen ci gaban wasannin kwaikwayo, yadda ake gudanar da shi ga jama'a a duniyar Hausawa baya ga gidajen ya]a labarai na Hukuma da masu zaman kansu, a yanzu har ana samun Kamfanonin fina-finai da ake wasannin kwaikwayon Hausa, don sayarwa al'umma a kasuwanni.

## 1.2 Manufar Bincike.

Duk wani aiki da mutum ya }uduri niyyar gudanar wa yana da manufar aiwatar da shi, musamman ta fannin ilimi. Wannan bincike zai taimaka wa masu nazari da bincike wajen nazarin shirin wasannin Samanja da na Duniya Budurwar Wawa a fagen Ilimi.

Hakanan kuma manufar wannan bincike ita ce ta gano irin gudummuwar da marubucin shirin ke ba da wa wajen bun}asar wasan kwaikwayon Hausa.

Wannan bincike zai taimaka wa ]alibai manazarta wasanin kwaikwayo cimma nasarar burinsu a fagen ko ya samar da wata kafa ta }alubalartar abin da ke cikin wurin manazarta ko masana.

Wata manufar a wannan binciken ita ce gano wasu daga cikin ire-iren wasanninsa da tasirinsu ga al'umma a rayuwarsu ta yau da kullum.

A }arshe kuma wannan bincike ina fatar ya zama tushe ko mafarin gudanar da wasu bincike ga masu son su ba da tasu gudummawar a wannan fanni na fagen Wasan Kwaikwayo.

**1.3 Farfajiyar Bincike.**

A nan, iyakar wannan bincike shi ne, sashen Hausa na Gidan Rediyo Tarayya Kaduna a ~angaren wasannin kwaikwayon Duniya Budurwar Wawa.

Daga cikin iyakar wannan bincike shi ne za~o wasu daga cikin wasannin da Usman Baba Pategi ya rubuta aka aiwatar kuma aka ya]a su ga jama'a suka saurara don nazarinsu.

Haka kuma wannan bincike zai fuskanci irin gudummuwar da Samanja Mazan Fama ke bayarwa, ta ~angaren rubuta wasan kwaikwayo da yadda yake bun}asa su, ko samun nasarar rubuta wasansa kuma a gabatar da su a kowane mako sau biyu a gidan Rediyo don ya]awa.

Duk iyakacin wannan bincike zai tsaya a kan nazarin rubuce rubucensa ne, na wasannin kwaikwayon domin }o}ari bayyana irin basiran da baiwar Ubangiji a kansa a matsayinsa na fitaccen ]an-wasa kuma marubucin wasannin Duniya Buduwar Wawa.

Haka nan kuma yana daga cikin iyakacin wannan binciken da a za~o wasu wasannin da ya rubuta aka gabatar kamar haka:

-Wasan "Kowa ya bar gida…" a Wasan Duniya Budurwar Wawa.

-Wasan "Mutum sai Allah" a wasan Duniya Budurwar Wawa.

-Wasan "Rayuwa" a Wasan Duniya Budurwar Wawa.

-Wasan "Jahilci Ciwo" a Wasan Duniya Budurwar Wawa.

-Wasan "Mutuwar Zuciya". A Wasan Duniya Budurwar Wawa

An za~o wa]annan wasannin ne da nufin su wakilci sauran wasannin da ya rubuta a wannan binciken, don a nazarce su a gano irin gudummuwarsa wajen bun}asar wasan kwaikwayon Hausa.

**1.4 Muhimmancin Bincike.**

Duk wani al'amari na duniya idan aka dube shi da idon basira musamman ta fuskar ilimi sai ka ga akwai wani muhimmin abu da zai amfanar da al'umma da suke gudanar da shi.

To ganin yadda Adabin Hausa yake da muhimmanci wajen gudanar da kusan dukkan al'amarin rayuwa al'umma ya sa aka ]auki wannan ~angare na wasan kwaikwayo kuma aka le}a aka ]auko ayyukan wannan bawan Allah don irin gudummawar da yake bayarwa wajen rubuce-rubucen wasannin kwaikwayon Hausa na gidajen Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N), a matsayinsa na marubucin wasan kwaikwayon Hausa.

Abu na gaba shi ne ganin wasan kwaikwayo kogi ne da ya mamaye kusan dukkan hanyoyin rayuwar al'umma ta yau da kullum shi ya sa ake son a taskace irin wannan gudummuwar da wannan gwarzo ya bayar ta wajen bun}asar Adabin Hausa, a rubuce ta hanyar rubuta wasannin da ake aiwatarwa domin adana su a makarantun ga nazari ko bincike a nan gaba.

Wani abu mai muhimmanci game da wannan binciken shi ne fito da hikimomi da fasahar Usman Baba Pategi da Allah ya ba shi wajen }ir}irar wasannin kwaikwayo ta yin la'akari da ma' aunin nazarin wasan kwaikwayo domin gano inda akalar salon ya karkata ta wajen jigogin misali jigon Siyasa ko zamantakewar al'umma ko don nisha]antarwa.

Haka nan kuma ina fatar ya zama tushe ko mafarin gudanar da wasu bincike ga masu son su ba da tasu gudummuwar a wannan fannin adabin wasan kwaikwayon Hausa.

**1.5 Hasashen Bincike.**

Wannan bincike na hasashen shin wasannin da ya ke rubutawa ake gabatarwa suna da goyon bayan hukuma ne ko a'a? Yana yin su ne don wata manufa ta daban da ta hukumar da ya ke wa aikin na gidan rediyon?

Ta ya ya wasannin da ya rubuta suka ba da gudummuwa wajen bun}asar wasan kwaikwayo a yanayin rayuwar jama'a?

Shin ya ba da gudummuwa ta ~angaren adabin wasan kwaikwayo kamar yadda masana su ka ambata?

Shin ana samun sauyi tsakanin rubutattun wasannin da na gargajiya a cikin rubuta wasanninsa kamar yadda masana fagen suka yi bayani a irin gudummuwarsu?

Ana hasashen gano ~angarorin da suka ba da gudummuwa a rayuwar al'umma kamar, Siyasa da Addini da Zamatakewa da kuma Tattalin Azzi}in }asa.

Duka a wannan binciken ake sa ran gano wa]annan hasashen.

**1.6 Tarihin Wasan Kwaikwayon Rediyo**

Hanyar sadarwa tana bun}asa rayuwar al'umma ta hanyoyi da dama tun kafin zuwan ba}i cikin al'ummomin }asar nan ta hanyar sadarwa ce ake sanin abin da ke faruwa cikin al'umma na alhairi ne ko kishiyansa ta hanyar gargajiya da sauyin zamani ya zo aka samu ci gaba. Rediyo na ]aya daga cikin kafar ya]a labarai da ]an Adam ya }ir}iro domin ya }ara taimakawa wajen sadarwa da kuma ilmantarwa da fa]akarwa da nisha]antarwa. Ganin yadda ilimin zamani ke bun}asa ga mutanen Arewacin Nijeriya ya sa 'yan siyasar da ke cikin mulkin ha]a]]iyar }asar mu Nijeriya suka kafa wannan gidan Rediyo a sakamakon nasarar da suka samu a cewar (Sama'ila 2006:4) Sarduna ya bu]e gidan Rediyo Tarayya Kaduna wanda ake kira da BCNN *Broadcasting Company of Northern Nigeria* da Talabiji (NTA) domin ya mamaye yankin Arewacin Nijeriya. Akwai shirye-shirye da dama da ake

gabatarwa don ilmantarwa da fa]akarwa da nisha]antarwa a wannan farin gida kafin Sardauna! An bu]e wannan Gidan Rediyo Tarayya na Kaduna ne a ranar sha biyar ga watan Maris 1962, wanda Firimiyan jihar Arewa Alhaji Ahmadu Bello, Sardaunan Sakkwato ya bu]e ya yi jawabin manufar bu]e wannan gidan rediyon da manufofi guda uku da ake bukata gidan rediyon ya yiwa mutanen Arewa. An ba shi suna BCNN *Broadcasting co-operation of Northern Nigeria.* Anan ya ce;

> *"Wannan gidan rediyon kamar sauran gidajen rediyo ana sa ran ya ilmantar ya nisha]antar ya kuma sanar. Duk da muna bukatar ko ya nisha]antar da mu, to ya zama dole a gare mu, mu bukace ku, ku ilmantar, sa'annan kuma ku sanar da mu duk abin da ke faruwa a Nijeriya da Arewa da }asar baki ]aya da kuma sauran }asashen duniya. Abin da ya sa muke mi}a wannan bukata kuwa shi ne, saboda gwamnati ta fahimci irin mahimmancin ilimi da kuma irin wannan aikin ma'aikatanku ta fuskar wayar da kan jama'a".*

Musa, (2004:18), Ya yi wannan jawabi ne a lokacin bu]e gidan rediyo da talbiji domin ya }ara jawo hankalin ma'aikatan gidan da su ri}a }ir}iro shirye-shirye masu ilmantarwa da nisha]antarwa. An samu nasarori da dama a game da manufofin kafa gidan rediyon a game da shirye-shiryen da ake gabatarwa, cikinsu har da wasannin kwaikwayo kamar wasanni irin su: Zaman Duniya Iyawa Ne da Basafce da Gundumi Fasa Kwanya da wasan Makarantar Malam Jatau na Albarkawa da Samanja Mazan Fama da wasan Duniya Budurwar Wawa. Da yake shirin wasan Duniya Budurwar Wawa na ]aya daga cikin shirye-shiyen da suka fi da]ewa a

gidan Rediyo da ake gabatarwa domin nisha]antarwa ko ilmantarwa ga masu sauraro a kowane mako sau biyu wato a gabatarar a ranar Laraba da misalin karfe uku da rabi na yamma a maimaita a ranar Asabar da dare da misali karfe takwas da rabi na dare. Wannan shirin wasan kwaikwayon Duniya Budurwar Wawa an }ir}iro shi ne a shekarar 1972, kuma marubucin wasan shi ne Usman Baba Pategi wanda aka fi sani da Samanja. Kuma shi ne mashiryi kuma marubucin wasan Samanja Mazan Fama, Ma}asudin shiri wa]annan wasanni shi ne domin fa]akarwa da ilmantarwa tare da hannunka-mai-sanda ga jama'a masu sauraren wasannin. Wasannin Samanja da na Duniya Budurwar Wawa ba su tsaya a nan ba don su kan zame abokan hira ne kuma mai gamsarwa ga mai sha'awar shirin domin yakan ta~o kusan dukkan ~angarorin harkokin rayuwar ]an Adam ta yau da kullum cikinsu da irin rayuwar sojoji ta zaman bariki.

**1.7 Takaitaccen Tarihin Alhaji Usman Baba Pategi (Samanja Mazan Fama).**

An haifi Usman Baba Pategi ne, a gidan Sarkin Pategi Alhaji Usman a cikin Jihar Kwara. Ya zo duniya ne a ranar 20/5/1942 (Ashirin ga watan Mayu a shekara ta Dubu [aya da [ari tara da Arba'in da Biyu). Allah ya yi wa mahaifinsa Sarki Usman rasuwa tun yana }arami, wanda a sanadiyyar haka ne mahaifiyarsa ta zama ita ce wu}a da nama wajen kulawa da dukkan abin da ya shafi rayuwarsa.

Samanja Mazan Fama, ya ci sunan mahaifinsa Usman ne, Sarkin Fategi wanda a sanadiyyar haka ne ake kiransa da cikakken suna, Usman Baba Pategi. Tun yana yaro }arami ya kasance mai son jama'a da son zumunci ga harka da ha}uri wanda wannan ya jawo masa farin jini wajen

jama'a da sauran yara abokai. Da]in da]awa kuma ga shi ya kasance shi ne auta a wajen mahaifinsa kuma ]a namiji.

Ga al'adar Musulmin arewa ta wajen neman ilimi a kan sa yaro a Makarantar allo, to shi ma duk da yake ]an sarki ne, an sa shi a makarantar allo tun yana yaro }arami don samun tarbiyya da ilimin addinin Musulunci. Daga nan ne aka sa shi a makarantar Elementare na garin Pategi a shekara ta 1952, yana ]an shekara goma da haihuwa bayan ya kamala karatunsa na }aramar Elementare a shekara ta 1955. Da sakamako mai kyau sai ya samu wucewa makarantar Midil da ke Ilori (Middle School of Ilori) a shekara ta 1955. Usman Baba Pategi ya kasance ]aya daga cikin ]alibai masu }o}ari da haza}a a ajinsu. Sanadiyyar haka ne ma ya kasance ]aya daga cikin ]aliban da ke wakiltar makarantarsu, wajen gasa a fannin darasin lissafi da sauransu, Tun a wannan lokacin ne Usman Baba Pategi, yake da sha'awar wasan kwaikwayo, tare da aiwatar da wasannin a makaranta.

Allah Gwani, bayan kammala Babbar Makarantar Elementare ta Ilori ne wato *midil school*, sai ya kama aiki a P.W (Public Works, Department Mechanical) a Kaduna wadda ake kira da Ministry of works, a yanzu. Daga nan sai ya koma gidan Rediyon Nijeriya, (N.B.C) da ke garin Ikko (Lagos), a 1961; daga nan sai ya bari ya dawo (R.T.K), wato Rediyo Talabijin Kaduna a sashen Harsuna. Daga nan ne fa yana cikin aikin rediyo, da ya}in basasa ya zo sai ya wuce ya shiga aikin Soja. Bayan gama ya}in basasa, sai gwanin namu ya bar aikin soja ya dawo inda ya fi wayo, wato aikin rediyo a shekara ta 1968. Usman Baba Pategi, ya kasance ]aya daga cikin 'yan wasan kwaikwayon gidan rediyo da talabijin na Kaduna a wancan lokacin, duk da yake ba shi ne mai rubuta wasannin ba.

Wasu daga cikin wasannin da ya ke fitowa sun ha]a da "Makarantar Malam Jatau na Albarkawa" na Muhammadu Ango Zariya. A wannan shirin

wasan kwaikwayo, ya kan kwaikwayi muryoyi daban-daban a cewarsa. Da kuma wasanni kamar su: “Wasan Zaman Duniya Iyawa ne” da “Wasan Wandon Taro Mazagin Fataka” da “Wasan Gundumi Fasa Kwanya” da shi da marigayi Inuwa Mazo.

Alhaji Yusuf Ladan ]an Iyan Zazzau, shi ne ke rubuta wasannin shi kuma Usman Baba Pategi, yana mataimakinsa bayan Alhaji Yusuf Ladan ya bar aikin rediyo, sai aka ba Alhaji Usman Baba Pategi ragamar shiryawa da rubuta wasannin gidan rediyon. Kasancewar haka sai ya samu gogewa da }warewa, wajen }ir}iro da kuma rubuta wasannin kwaikwayo. Samun haka ne a sashen, ga shi da }wazo da hazaka, a matsayin sa na shugabam sashen, ya sa ya fito da wasan “Samanja Mazan Fama” wanda shi ne marubucin shirin, kuma ya gabatar a rediyo da talbijin na Kaduna. An fara shirin wasan Samanja Mazan Fama da shirin Duniya Budurwar Wawa a shekara ta 1972.

Wani abin ban sha’awa ga shi Alhaji Usman Baba Pategi, ta ~angaren wasannin kwaikwayo, shi ne, shi ke }ir}iro shirin kuma ya rubuta, ya kuma fito a matsayin tauraron shirin wasan Samanja Mazan Fama wanda sanadiyyar haka ne ake kiransa da “Samanja”. Kai lallai wannan gwani ne don shi ma da kansa yana gode wa Allah, game da irin wannan baiwa da haza}a da basira da hikima da Allah ya ba shi, wanda shi ne ya ba shi damar zama fitaccen ]an wasa kuma marubucin wasannin kwaikwayo a kafafen ya]a labarai musamman na Rediyo Tarayya Kaduna.

Hirarmu da shi ba ta tsaya nan ba wanda ta gudana a ranar Lahadi 11/2/2006, a gidan Rediyon Tarayya na Kaduna lokacin da suke shirya shirin Wasan Duniya Budurwar Wawa na wannan makon. Ganin yanda ya rungumi wasan kwaikwayo, ya zama sana’a a ko da yaushe, ya sa na yi masa tambaya: Shin, Wa ya }ir}iro shirin Duniya Budurwan Wawa da ake gabatarwa a wannan gidan rediyon? Ya ce ha}i}a shi ne wanda ya }ir}iro

shirin, kuma shi ne marubucin wasan "Duniya Budurwar Wawa, wanda ake gudanarwa a gidan Rediyon Tarayya Kaduna sau biyu a mako, wato a gabatar a ranar Laraba da misalin }arfe 3:30 na yamma kuma a maimaita a ranar Asabar da }arfe 9:30 na dare wadda har yanzu a kowane mako haka ake gabatar da wasan.

A cewarsa ya kan lura da yanayin zamantakewar al'umma ne na yau da kullum, ko yadda hukuma take gudanar da rayuwar jama'arta, sai ya rubuta wasan kwaikwayo a kai don garga]i ko fa]akarwa ko don ilmantarwa ko kuma don raha ko nisha]antarwa. A ci gaba da jawabinsa, ya ce ba ya rasa abin da zai shirya ko rubuta wasansa a kai a kowane mako. To amma yana lura da abubuwa da dama wajen rubutawa da shirya wasannin kwaikwayonsa, kamar addini, don kar ya saba wa Mahaliccinsa, wato la'akari da yanda addinisa ya ba shi iyaka don kar ya wuce maka]i da rawa. Sai kuma al'adan mutanenmu Hausawa, don da Hausa yake rubutawa da shiryawa da gabatarwa, don kar ya sa~a wa yanayi da tsarin rayuwar al'ummar Hausawa. Haka kuma yana tafiya da yanayin sauyin zamani don sa}on ya samu isa ga wa]anda ake gabatar wa, wato masu sauraron wasannin don ya }ara masu armashi da jimirin sauraron wasan a lokacin da ake gabatarwa.

A 'yan wasan da suka fara gabatar da wasannin kwaikwayon da su akwai wa]annan:

- {asimu Yero
- Ibrahim Bayi (Marigayi).
- Umaru Danjuma (Kasagi na Halima).
- Haruna Danjuma (Mutuwa Dole).
- Muhammadu (Idon Mujiya).
- Marigayiya Dala Isa Bakori (Bariki).

Baya ga irin wa]annan taurarin ‘yan wasan, Samanja ya sami damar yin ma’amala da wasu ‘yan wasan na wasu gidajen ya]a labarai na rediyo da talabijin. Wannan ne ya ba shi damar }ir}iro wani wasa mai suna “Ga Fili, ga mai Doki.” Bayan ya }ir}iro kuma ya rubuta wasan sai wajen gabatar da shi aka yi ha]in gwuiwa tsakanin fitattun ‘yan wasan Kano da Kaduna da Sakkwato da Jos, aka ri}a gabatar da wasan a gidan Talabijin na duk wa]annan jihohi ga jama’a. Shirin an yi shi ne a tsakanin shekara ta 1985-1986. A hirarmu da shi a ranar 12/7/2011, ya yi mini bayani cewa matansa na aure uku ne da yara goma sha hu]u, cikinsu maza goma, mata hu]u sai kuma jikoki goma sha ]aya.

Idan aka dubi irin gudunmuwar da wannan gwarzo ya ba da wajen bun}asa adabin rubutattun wasannin kwaikwayo da shiryawa da gabatarwa, lallai za a jinjina masa a wannan fage don har yanzu yana ci gaba da rubutawa da shiryawa kuma ana gabatarwa a kafafen ya]a labarai.

**1.8 Hanyoyin Gudanar da Bincike.**

Hakika kowane aiki ko nazari ko ma bincike kafin a samu nasara, akwai hanyoyi da dama da a kan bi wajen cimma nasarar. To, domin samun nagartattun bayanai game da wannan aiki, an zabi hanyoyi da dama da za a yi amfani da su, wajen cimma nasarar wannan burin na aiwatar da wannan bincike. Wato abin da ake bu}ata ta fuskar ilimin bincike, wa]annan hanyoyi sun ha]a da:

Hanya ta farko da aka bi wajen samun ingantattun bayanai ita ce ta yin hira da tattaunawa da mashirin kuma marubucin wasannin da ake nazarinsu kai tsaye wato Usman Baba Pategi wanda ake mai la}abi da *Samanja Mazan Fama* tare da wasu ‘yan wasan kwaikwayo, wa]anda suke aiwatar da wasanni kwaikwayon bayan ya rubuta kuma aka gabatar da su a gidajen ya]a labarai musamman gidan Rediyon Tarayya na Kaduna (F.R.C.N).

Wata muhimmiyar hanya da aka bi wajen samun biyan bukatar wannan bincike ita ce ta sauraron wasu daga cikin wasannin kwaikwayon da ya rubuta kuma aka aiwatar har aka ya]a su ga masu sha'awar wasanninsa a lokutan baya. Baya ga sauraron wasannin sai aka yi }o}arin juye wasu daga cikinsu a rubuce *Transcription* don a nazarce su a wannan aikin kamar yadda za a gani a nan gaba a babi na uku da na hu]a da kuma na biyar.

Hanya ta biye da wannan ita ce. Ta duba ayyukan da suka gabata wa]anda suke da ala}a da wannan binciken da ake gudanarwa, ta nazarin wallafaffun litattafai musamman na fannin Adabin wasannin kwaikwayo don ganin irin rawar da wasanninsa ke takawa a fagen adabin Hausa da gwada mizaninsu a wannan fagen ta fuskar masana adabi wasan kwaikwayon Hausa.

Nazarin kundayen bincike na matakin ilimi daban-daban, da mujallu da ma}alu da sauran takardu na ilimi domin tantance muhimman bayanai da ake bukatar ganowa a wannan binciken kamar yanda aka yi bayaninsu a babi na biyu wato "waiwaye adon tafiya." Don samun ingantattun bayanai a wannan bincike. An yi amfani da kayan sadarwa irin na zamani kamar rediyo maikaset don tabbatar da samun kyawawan bayanai da kuma sauran hanyoyin da duk suka kamata, domin samun cikakkiyar nasara.

## 1.9 Kammalawa.

A nan ne za a kammala aikin da ke wannan Babin inda yake ]auke da abubuwa kamar haka da farko akwai gabatarwa da aka yi domin gudanar da wannan binciken da aka gudanar a kan aikin wannan fitaccen ]anwasa kuma marubucin wasan kwaikwayo da ake ya]awa a kafafen ya]a labarai ga masu sha'awar wasanninsa. Haka nan kuma a wannan Babin ne aka yi bayanin dalilan da suka sa aka gudanar da binciken da kuma manufar gudanar da bincike da farfajiyar binciken da muhimmancin wannan binciken tare da hasashen bincike da tarihin wasan kwaikwayo a rediyo tare da ta}aitaccen tarihin Alhaji Usman Baba Pategi *Samanja* don ganin an samu nasarar abin da ake bukata a binciken, Haka kuma anan ne aka yi bayanin iyakacin farfajiyar da binciken zai ta~o da wasu daga cikin za~a~~un wasannin da ya rubuta a wajen gudanardawar tare da irin muhimmancin binciken, tare da na]ewar Babin.

## BABI NA BIYU: WAIWAYEN AYYUKAN DA SUKA GABATA.

### 2.0 Gabatarwa

A wannan Babin ne za a nazarci ayyukan da suka gabaci wannan binciken wa]anda suke da ala}a ko zumunci da wannan ta fuskar Adabin wasan kwaikwayo don ganin an cimma manufar gudanar da sahihin bincike a kan ayyukan da wannan ]anwasa ya rubuta a gidan Rediyon Tarayya na Kaduna.

**2.1 Ayyukan da Suka Gabata**

A wannan fanni na adabin Hausa, manazartansa da masana irin su Yahaya, (1986) sun yarda da wasan kwaikwayo wani yanki ne mai cin gashin kansa, kuma ginshi}i ne mai zaman kansa. A kashe-kashen da suka yi na adabin Hausa, baya ga zube da wa}a kamar yadda aka yi bayani a Babin Farko. Sannan kuma ya kasu gida biyu, watau, akwai na gargajiya, da na zamani, ko rubutaccen wasan kwaikwayo. Hausawa kan ce "waiwaye adon tafiya." Haka ne. Kafin wannan binciken, an yi bincike, da dama a matakan ilimi daban-daban a kan wasan kwaikwayo, ko dai a matsayin kundin neman digiri a jami'o'i, ko kuma a wajen taron }ara wa juna ilimi da bita ko a mujallu da jaridu. Ta dalilin haka ne ya zama wajibi da a dubi irin ayyukan da manazarta, adabin Hausa, suka gabatar da wurare daban-daban domin samawa wannan bincike madogara don wasu daga cikin ire-iren wa]annan ayyuka suna da dangataka da wannan aikin ko ala}a. Haka nan kuma ala}a na iya kasancewa ta kusu ce wato ta }ut-da }ut, ko ta nesa ce wannan abu na da matu}an mahimmanci ta daliln yin haka ne zai ba da damar sanin inda aikin yasa gaba, da kuma kimarsa a wannan fage na ilimi domin samun abin dogaro.

Wannan aikin binciken zai ba da gudummawarsa ce a kan ayyukan da suka gabata, musamman wa]anda suka yi nazari a fagen adabin Hausa, ta fuskar wasan kwaikwayo. Wannan waiwayen zai fi karkata ne musamman ayyukan da suka shafi rubutaccen wasan kwaikwayon Hausa. Wannan aiki

ba zai tsaya a nan ba sai ya duba ayyukan da suke da ala}a ta kusa da ta nesa da shi. Kafin wannan akwai wasu ayyukan da suka ba da tasu gudummawar kuma kowanne ka duba za ka ga hujjarsa ko abin da ya dogara da shi ta fuskar da ya nazarci nasa fannin adabin wasan kwaikwayon, daga cikin ire-iren wa]annan gudummawar da aka bayar game da wasan kwaikwayo, cikin su akwai:

Kundayen neman digiri na ]aya da na biyu da suka ba da na su gudummawar a wannan fagen. Cikinsu akwai wa]anda suke da dangantaka da wannan aiki har ma da ma}alu da ake gabatarwa a wajen taron }arawa juna sani. Daga cikin ayyuka da aka ci karo da su sun ha]a da kundin binciken na Ibrahim, (1979) mai suna: "Yadda Wasan kwaikwayo ya Taso da Fa]a]ansa" Kwalejin Ilimi ta Sakkwato. Aikinsa ya ta'alla}a ne a kan tarihin Wasan kwaikwayon Hausawa da fa]a]ansa a }asar Hausa. Ya yi bayanin wasannin na al'ummar na gargajiya tun kafin zuwan ba}i cikinsu da ire-iren wasannin da suke aiwatarwa da yadda ya samu fa]a]a a }asar Hausa. Ala}ar wannaa binciken da wanda ake gudanarwa ita ce, duka a adabin Hasawa ne kuma a fannin wasan kwaikwayo aka gudanar. Sai kuma banbancin da ke tsakaninsu bai wuce ya gudanar da aikin sa a kan wasanin gargajiyar Hausawa ba ne, yayin da wannan ana kallon irin gudummuwar da Usman Baba Pategi ya bayar ne ta wajen bun}asar wasan kwaikwayon Hausa a gidan rediyo ta fuskar rubuta wasannin. Binciken da Dan kiri, (1980) ya gabatar da kundinsa a B.U.K mai suna, "Nazari kan wasan kwaikwayo a Hausance" shi ma ya yi nasa aikin ne ta fuskar irin Hausar da aka fi amfani da ita ce wajen gabatar da wasan kwaikwayo na gargajiyar Hausawa. Ya nazarci Hausar da 'yan wasannin gargajiya suka fi amfani da ita a lokacin gudanar da wasanninsu, yayin da wannan aikin zai kalli bun}asar wasannin ne a rubuce wanda aka gabatar a gidan rediyo. Aliyu,

(1982) ya gudanar da bincikensa a kan yadda Hausawa suka fi ba da }arfi wajen shirya wasan kwaikwayo. Sunan kundin binciken nasa shi ne "Rawar Hausawa a Wasan Kwaikwayo", a Jami'ar Sakkwato UDU. Ala}arsu ita ce ta wasan kwaikwayo bambanci kuwa ita ce ta bincikensa a kan irin rawar da al'ummar Hausawa suka taka. Mansur,L. (1985) "Dangantakar Suna da Hali a cikin Rubuttatun Wasannin Kwaikwayon Hausa", shi ya yi bayanin yadda marubuta wasannin kwaikwayo kan yi amfani da ]an wasa musamman tauraron wasan da kuma irin tasirin da suna kan yi a cikin rubutattun wasannin kwaikwayo. A wannan kuwa ana le}en iri yadda gwaninmu ya bu}asa wasanin ta hanyar rubutawa kuma a gabatar da su a gidan rediyo. Sai kundin, Malumfashi, A.I. (1985). "Asali da Bun}asar Rubutaccen Wasan Kwaikwayon Hausa", inda ya ba da nasa gudummuwar ta wajen bin diddigin tarihin rubutaccen wasan kwaikwayon Hausa. Hanyarsu ta zo ]aya da aikin da ake gudanarwa domin dukannisu a rubutattun wasanni ne sai da sun sha bamban ta wajen tarihi. Akwai kundin da Abdullahi, M.S. (1995) mai suna "Bambance-bambance da ke tsakanin wasan kwaikwayo na Hausa da gargajiya da fina-finan zamani nazari a kan jigo", Jami'ar Bayero Kano a inda ya yi bayani a kan bambanci da ke tsakanin wasannin gargajiya da na zamani wato rubutacce da kuma fina-finan zamani. Inda aka bambanta da kundin da ake gudanar da bincike a nan shi ne a nasa ya gano bambancin da ke tsakanin wa]ancan ne a yayin da wannan ake }o}ari gano irin gudummuwar bun}asa wasannin da ya rubuta ne. Akwai na Dabai, L.M. (1991), mai suna, "Kwatance Tsakanin: *Zaman Duniya Iyawa ne* da *Kul~a na Barna*" da yake dukka binciken a fagen adabin wasanni ne an bambanta ne a wajen bin hanyar gudanar da bincike domin a wannan ana son a fito da irin gudummuwar da marubucin ne ya ba da wajen bun}asa wasa. Haka kuma Pawwa, S.A. (1992) ya gudanar da aikin sa ne mai taken "Kwatanta

Littafin *Jatau na Kyallu* da *Wasan Marafa* a inda ya nazarci kamanci da bambanci da ke tsakanin wasannin biyu ya fito da su. Aikin da Sulaiman, A.I. (1992), ya gudanar a kan "Wasan *Uwar Gulma* a matsayin "Wasan Ban Tausayi" a inda ya nuna tauraruwar wasan wato Halima kamata ya yi da a tausaya mata a cikn wasan. Wannan aikin ya sake cin karo da aikin Panda I.A (1993) mai taken "Muhimmancin Wasan Kwaikwayo dangane da Ilimantar da Al'ummar Hausawa" da na Aminu, H. (1991) dukkan wa]annan ayyukan suna da ala}a da wanda ake gudanarwa amma ta fuskar rubutattun wasanin kwaikwayo.

*"Elemen of Tragedy in Hausa Literarcy Drama: A case study of Jatau Na Kyallu* and *kul~a na Barna*", in da ya yi nazarinsa a kan rubutattun littafn wasannin ta hanyar kamancinsu da bambanci da ke tsakaninsu sai kuma na, Balla, Z.Y. (1972) *"Comparing Uwar Gulma* and *Zamanin nan Namu*" A.B.U. Shi ma Aliyu M.A. (1982), ya sa wa nasa kundin suna "Matsayin Wasan Kwaikwayo a Rayuwar Hausawa", Jami'ar Sakkwato, inda ya nuna yadda Hausawa suka ]auki wasan kwaikwayo a rayuwar Bahaushe. Haka kuma Daura, H.A.(1985) a nasa bincike mai suna: "Tasirin Adabin Baka ga Rubutaccen Wasan Kwaikwayo," A.B.U, ya yi binciken sa ne, a kan yadda marubuta wasannin suke amfani da tsarin adabin baka irin su tatsunniya da almara a ya yin da suke rubuta ko shirya wasanninsu kuma bayyana irin yadda Adabin Baka ya yi tasiri a cikin rubutattun wasannin kwaikwayo ala}ar wannan aiki da wanda ake gudanarwa ita ce dukkansu ana lura ne da rubutattun wasanni sai dai wannan ba wallafanfun wasanni ba ne, na rediyo ne wanda aka aiwatar kuma aka ya]a ga masu saurare ana son a ga irin gudummuwarsu ga jama'a. Sai kuma Bello, M.(1982) ya ba kundin bincikensa suna: "Hoton Rayuwa Cikin Wasan Kwaikwayo." A aikin da ya gudanar ya ]auko rayuwa ce ta al'ummar Hausawa ta zahiri ya kwatanta ta

da ta cikin wasannin kwaikwayon Hausa. Ala}ar aikinsa da wannan ita ce dukkansu kwaikwayon rayuwar al'umma su ke yi ta zahiri amma a wasance da nufin ilmantarwa ko fa]akarwa ko garga]i a game da aikata wani aiki mai kyau ko maras kyau A.B.U. Zariya. Daga nan sai Gudummuwar Malumfashi, A.I. (1987) mai taken "A Madadin Wasan Kwaikwayo". Malamin ya bayyana mana muhimmancin wasan kwaikwayo fiye da sauran ~angarorin adabin Hausa. Kuma ya nusantar da mu irin gudummuwar da wannan fagen ke ba da wa na ilmantarwa sannan da nuna rayuwa ta zahiri a wasance. Ala}ar wannan aiki da wanda ake gudanarwa ita ce ta gano irin wa]annan abubuwan da ya ambata a cikin wasannin da Samanja ya rubuta na gidan rediyo Kaduna. Akwai wani nazari da aka yi kan "Diskin da Ridi da Kogin Ruwan Bagaja", na su Auwalu, da Gulumbe, (2000) wadda suka yi }o}arin fitar da jigogin adabin baka na tastunniyoyin biyu ta wajen nuna kamancinsu da bambancin da ke tsakaninsu duk da yake akwai bambanci tsakanin wancan aikin da wannan aikin da ake gudanarwa sai dai sun yi tarayya a fagen adabin wasan kwaikwayo. A shekarar (2001) Umar, R.T. ya gabatar da kundin bincikensa mai taken: "Tasirin ba}in Al'adu Cikin Wasannin Kwaikwayon Hausa a Zariya". A nazarin an ]auki kamfanonin shirya fina-finan Hausa a Zariya aka nazarci yadda ba}in al'adu suka yi tasiri a wajen shirya wasannin kwaikwayo a zamanance, aka yi }o}arin gano ire-iren ba}in al'adun da suka shigo wajen shirya fina-finansu don ganin fina-finan nasu sun samu kar~uwa da kasuwa ga jama'a. Ala}arsu da wannan aikin bai wuce a kan wasannin kwaikwayo ba ne na kafar ya]a labarai duk da yake wannan na rediyo ne wancan na fina-finan Hausa ne, to amma gudummuwar su ake dubawa ta wajen bun}asar wasanni.

A cikin ayyukan da suka gabata ne, aka nazarci kundin Yahaya, M.Y. (1985) mai suna,"Wasan Kwaikwayo a Gidan Rediyo Nijeriya na Kaduna",

ya yi tsokaci kan ire-iren wasanni da ake gabatarwa a gidajen Rediyo na Kaduna wanda aka nazarci ire-iren wasannin kwaikwayo da tasirinsu a gidan rediyon, zumuntar da ke tsakaninsu da wannan aikin shi ne, dukkansu a kan wasannin gidan rediyon Tarayya na Kaduna ne. Amma wannan a kan gudummuwar da Samanja ne ya bayar ta wajen rubuta wasanni a gidan rediyon. Haka shi ma Abdullah, S. (1982) taken nasa kundin shi ne "Hausa a Gidajen Rediyo da Talbijin a Najeriya" A.B.U. Ya karkata akalar nazarinsa ne a kan irin Hausar da 'yan wasan suke amfani da ita ya yin gabatar da wasanninsu a gidajen Rediyo da Talebijin na Kaduna. Zumuntar da ke tsakanin wa]annan ayyuka ita ce ta kasancewarsu a wsannin kwaikwayon gidan ya]a labarai ne aka gudanar da binciken. A kundin da Musa, H. (2004) ta gabatar mai taken, "Gudummawar Yusuf Ladan ga Wasan Kwaikwayo na Rediyo," ta yi }o}arin nuna irin gudummuwar da malam Yusuf Ladan ]an Iyan Zazzau wajen shirya wasannin kwaikwayo a rediyon tarayya na Kaduna da kuma tarihin rayuwarsa da ire-iren wasannin da ya rubuta su aka gabatar. Ala}ar da ke tsakanin wannan aikin da aka gudanar da wancan ta }ut da }ut ce domin ma iya hasashen cewa shi ne malamin Samanja a fagen rubuta wasannin kwaikwayo na gidan rediyo. Ewu, R. J.(1986) *M.A Theses "The polities of Televesion Drama in Nigeria a Case Study of N.T.A* Kaduna.

Ayyukan da suke da dangantaka ta }ut da }ut da wannan aiki sun ha]a har da na [anjuma, U.H (1998) "Salo da sarrafa harshe a wasannin Samanja" A.B.U ya karkata ne a kan wasan Samanja da irin Hausar da ]an wasan ke amfani da ita a lokacin da ya fito cikin wasan tare da sauran 'yan wasa bambancin wannan aikin da wanda aka gudanar shi ne a wancan an kalli Samanja ne a matsayin ]an wasa a wannan kuwa ana }o}arin a gano irin gudummuwarsa ne a fannin rubuta wasannin na gidan rediyon. A kundin da

Abubakar, S.S (1998) mai taken “Garga]i a Wasan Samanja”, shi ma kusan duk tafiyarsu ]aya ce da na Gular, E.Y. (1993) mai suna: *“Television Drama Advertisement and Propaganda Tendencies: A Case Study of Samanja”* Sashen Turanci A.B.U dukkansu biyun su karkata ne a kan wasannin da ya fito a matsayinsa na ]an wasa da irin sa}onnin da suke cikin wasannin. Sai kuma aikin da Hun}uyi, D.K (1992) ya yi mai taken “Rayuwa da Ayyukan Usman Baba Fategi (Samanja Mazan Fama) Musamman a kan shirin “Duniya Budurwar Wawa” da “Samanja Mazan Fama”. Ya yi bincikensa ne a kan tarihin rayuwarsa da kuma kasancewarsa fitaccen ]an Wasan Kwaikwayo. Ala}ar wannan aiki da wanda ake gudanarwa ta }ut da }ut ce don a kan fitaccen ]an wasa ]aya ne, sai dai an sha babban ta fuskar nazari, don wannan ta fuskar ayyukansa ne ta ~angaren rubutun Wasannin Kwaikwayo. Hakan ma ma}alar da aka gabatar a taron }asa na }ara wa juna sani kan nazarin Hausa a Jami’ar Usman [anfodiyo Sakkwato, mai taken “Gudummuwar Alhaji Usman Baba Pategi (Samanja) ga wasan kwaikwayon Hausa,” na Garba R. (2007). Malamar ta yi tsokaci ne a kan tarihinsa da wuraren da ya yi ayyukansa da shirya wasanninsa na Rediyo da Talbijin da gudummawarsa ga Wasan Kwaikwayon Hausa, musamman a kan shirin “Samanja Mazan Fama” da wasu daga cikin shirin “Duniya Budurwar Wawa” ta fuskar gargajiya da ilmantarwa da farfaganda da raha da yabo ko suka da aka yi a wasannin ‘Samanja’ da ‘Duniya Budurwar Wawa’. Ta yi nazari a kan shirin. “A Taimaka” da “Kowa ya Bar Gida” da kuma wasu shirin da aka yi ha]in gwuiwar ‘yan wasa misalin “Kowa ya Kwana Lafiya shi ya so” wanda ‘yan wasan Kano da Kaduna da Sakkwato da na Jos suka shirya. [anjuma U.H (1998) ya yi nazrinsa ne a kan yadda ake amfani da harshe a wasannin Samanja Mazan Fama, musamman Hausa don isar da sa}on da ake bu}ata da Abubakar, S.S. (1982) wadda na shi ya karkafa

nazarinsa a kan jigon ne da garga]i a  wasan Samanja da yanda zamantakewar barikin sojoji na yau da kullum yake gudana.

A nazarin kundin, Hun}uyi D. K, kuwa shi ya nazarci abubuwan da su masu sauraron Rediyo da Talbijin tun farkon soma shirin Samanja Mazan fama da, shirin, Duniya Budurwar Wawa ya kuma fito da tasirin wasu harsuna da ake amfani da su, kamar Turanci da Fillanci da Nufanci baya ga ainihin harshen Hausa. Duk a cikin shirin Samanja da Duniya Budurwar Wawa. Aikin yana da dangantaka ta kusa da wannan aiki ko da yake shi ya fi mai da hankalinsa ne a kan kasancewar Usman Baba Fategi a mastayinsa na ]an wasan kwaikwayo ne kuma fitaccen tauraro a wasan Samanja Mazan Fama. A hirar da aka yi da Samanja ranar 14 /6/2003, wanda jaridar *Weekly Trust* ta yi da shi a shafi na 33 ya yi bayani game da tarihin rayuwarsa da tarihin wasanninsa na Samanja da irin halin da shirin yake ciki bayan ya bar aikin gidan Rediyo da yanda ya yi ta }o}arin neman tallafi daga Kamfanoni da Gwamnatoci don a ci gaba da gabatar da Wasan Samanja kamar yanda ake yi a shekarun baya  don ya ci gaba da ilmantarwa da fa]akarwa tare da nisha]antarwa.

Shehu, (2009), ya rubuta wata ma}ala mai suna: "*Hausa Popular Culture and Poltical Discourse in Nigeria some Insights into Samanja Drama on Radio Kaduna.*" A cikin ma}alar tasa ya yi tsokaci ne a kan yadda ake amfani da Wasan Kwaikwayo wajen isar da sa}onni ga Shuwagabannin al'umma a inda ya yi la'akari da wasannin da tauraron namu ya fito a matsayinsa na ]an wasa a gidan ya]a labarai musamman Gidan Rediyon Tarayya Kaduna inda aka fi gabatar da wasanninsa. Ya ]auki wasu wasannin da tauraron ya aiwatar ne a kan yanayin rayuwar al'umma ta fuskar Siyasa da Zamantakewa a nan sai ya ]auki yanayin al'adar Hausawa na Wawan Sarki a Fadar Sarakuna ta wajen isar da sa}o a wajen Sarki cikin

barkwanci da wawanci a lokacin zaman da ake na fadanci a fadar kuma sa}on ya yi tasiri a wajen sarakunan.

A wannan aiki akwai wani gi~in da wa]ancan ba su ta~a ba wanda shi ne ake da buri cikewa ta fuskar za}ulo ire-iren ayyukan da shi wannan shahararran ]an wasa kuma marubucin wasannin kwaikwayo a ga irin basirar da fasahar da Allah ya yi masa musamman ta ~angaren rubuta wasanni a gidan Rediyo Tarayya na Kaduna. Duk da yake wasu ayyukan da suka gabata sun ta~i bangarensa amma sun fi karkata ne a matsayinsa na ]an wasan gidan rediyon, amma ba su ce komai ba ta fuskar rubuta wasa a game da wannan ]an wasan a dangane da gudummuwarsa a ~angaren rubuta wasannin kwaikwayon da ya gudanar.

**BABI NA UKU: GUDUMMUWARSA A FANNINA ILIMI DA ADDINI DA SIYASA.**

**3.0 Gabatarwa**

Masana da dama sun yi }o}arin bayyana muhimmacin wasan kwaikwayo, cikinsu har ma da masana ilimin mutuntaka (psychologist). Jonal, (1959:55) *The Use of Drama,* a cikin wannan littafi ya bayyana wasan kwaikwayo da cewa shi ne abin nan mai kawo sauyi ko da gora. Ya ci gaba da cewa "ai wasan kwaikwayo kan kawo sauyi ne kawai a fuskar rayuwar ]an Adam yana kawar da miyagun al'adu cikin al'umma akwai matu}ar muhimmanci tattare da wasan kwaikwayo kamar.

1. Yana fito da al'adun gargajiya da kuma inganta su, domin al'ummar da ke biye da su misali tsarin mulkinsu.
2. Haka kuma yana bayar da nisha]i da sanya walwala da sha}atawa ga masu kallonsa. Misali a wasu lokutan mutum kan samu kansa a halin ~acin rai da zarar ya kalli wani wasa da ya }ayatar da shi sai ka ga ya washe domin irin tasirin da wasan ya yi a kan sa.

3. Wasan kwaikwayo, kan hana mutane yin wasu abubuwa marasa kyau misali cin amana da gulma da cin dukiyar wani da kar~ar cin hanci da rashawa da sauran su.
4. Wasan kwaikwayo, ya kan sanya hasashensa ya zama gaskiya.
5. Wasan kwaikwayo, ya kan ha~aka harshen al'umma ta hanyar sarrafa harshen sa, hakan yakan koyar da 'yan wasa yadda za su iya magana a gaban jama'a.
6. Wasan kwaikwayo ya kan koyar da tarbiyya da kyawawan ]abi'u don su taso da su kamar dogaro da kai da fa]ar gaskiya da ha}uri da juriya.
7. Wasan kwaikwayo ya kan yi garga]i da hannunka mai sanda, aikata kyawawan halaye da kuma hani da miyagun ]abi'u.

Haka 'Yar Aduwa, ( 2007:22) ya ba da amfanin wasan kwaikwayo inda ya ce "wasan kwaikwayo kowane iri yana da matu}ar amfani ga jama'a (masu shirya shi da kuma masu kallo su kuma karanta shi ko sauraronsa) dangane da rayuwarsu ta yau da kullum. Ga ka]an daga cikin amfanin wasan kwaikwayo:

Wasan kwaikwayo ya na nuna fasahar al'umma da inganta ta.

Wasan kwaikwayo yana bayar da hanyar sha}atawa da sanya nisha]i a zukatan jama'a.

Wasan kwaikwayo hanya ce ta cusa tunani a zukatan jama'a da kuma koyar da su sanin ya kamata.

Wasan kwaikwayo yana da]a gyara halayen jama'a, ta hanyar nuna masu kyawawan abubuwa da al'umma take so,kuma take yin tin}aho da su,don jama'a su ]auke su da muhimmanci. Sannan kuma suna nuna wa jama'a wasu halaye munana abin }i ga al'umma da kuma yi wa jama'ar nan nasiha su guje wa wa]annan munanan abubuwa.

Wasan kwaikwayo hanya ce ta yi wa yara tarbiyya don su tashi da halaye nagari wa]anda al'umma take bu}ata.

Wasan kwaikwayo yana koyar da ilimi ga jama'a, su koyi abubuwan da ba su sani ba, su kuma ilmanta." 'Yar Aduwa, (2007:22)

Mun ga irin muhimmancin wasan kwaikwayo wanda masana da manazarta suka bayyana kuma wannan shi ya ba da damar nazarin ayyukan wannan fitaccen ]an wasa da irin gudumawar da ya bayar wajen cito jama'a da ya aikata. A wannan Babin za a tabo gudummuwar da suka shafi fagen Ilimi da Addini da Siyasa.

**3.1 Ma'anar Ilimi.**

A {amusun Hausa na Jami'ar Bayero Kano(2006:205) Ilimi shi ne: "(i) Sani, musamman na shari'a da addini. (ii) karatu na fannin kimiyya da adabi (iii) ganewa ko fahimta." Wato mutum ya san abin da bai sani ta fuskar Ilimi kuma wannan sanin ya taimake shi a rayuwarsa. Haka kuma a *Encarta Dictionaries (2009).*An fassara Ilimi da hanyar koyo da koyarwa a makaranta ko wani wuri makamancin wurin don neman Sani.

**3.2 Muhimmacin Ilimi da Tasirinsa ga Bahaushe.**

Ilimi hasken rayuwa da yake ana batu ne a kan muhimmancin ilimi da tasirinsa ga Bahaushe alal ha}ika duk wanda ya sami ilimi yakan bambanta da wanda bai da ilimin ta wajen hul]ar mu'amallar jama'a. Ilimi musamman na Addini ko na zamani ya kan fuskanci abubuwan da zai gudanar da irin sani da yake da shi. Ibrahim, (1982:88) ya nuna muhimmancin sarrafa Ilimi inda ya ce 'Idan mutum ya tara Ilimi da yawa sai ya koma gida ya kafa makarantar kansa shi ma ya zama malami sai a dinga zuwa wurinsa ]aukar karatu. Wani lokacin ma idan wani malami ya ga almajirisa ya sami Ilimi sai ya ba shi shawarar ya zauna a gida ya dinga biya wa wa]ansu. Haka kuma daga cikin irin wa]annan malamai ne a kan sami muhutai da Al}alai da kuma waziran Sarakuna".

**3.3 Wasannin da suke {unshe da Ilimi a cikin Wasanin Duniya Budurwar Wawa.**

Akwai batun Ilimi da marubucin wasan ya yi a wasansa na *'Kowa ya Bar gida*… na Duniya Budurwar Wawa a Fitowa ta ]aya" kamar a inda yake nuna muhimmancin aiki da Ilimi in mutum ya yi karatun kamar haka:

***Malam Jibo:*** ***Eh, kasan Ilimi in ka yi shi,***
***ka yi aiki da shi ma wani abu ne.***

Sai kuma inda ya sake yin nuni da amfanin yin shawara da mai ilimi

***Malam Jibo:*** ***To ban son in ja wani dogon surutu, ya mene ne bayani, ke dai ba yarinya ba ce, kin yi karatu, kwanan nan kika gama karatun lauya ]in ki, ko ba gaskiya ba, to mene ne bayani yanzu don ba na son...***

***Malam Jibo:*** ***Tunda ta yi karatu, ta san abin da take yi ita ma ya kamata ta za~i lokacin da take so, ko kuma ya take so a yi abubuwan don mu ji daga bakinta.***

***Malam Jibo:*** ***Kana ji abin da nake so in fa]a maka to ka ga sha'anin ilimi ke nan.***

***Malam Jibo:*** ***Ta yi shi to al'amarin ilimi kenan.***

A fitowa ta biyu kuma an nuna muhimmanci aiki da Ilimi ta wajen tsara magana da tunanin mai ilimi ya bambanta da wanda bai da ilimi kamar haka:

***Malam Jibo:*** ***To amma yaya in ka duba, yarinyar nan fa ta yi magana na ilimi, ta ce ita wannan }auyen, tana so ta san ainihin }auyenmu, idan aka nemo }auyen, a nan za a yi biki, a nan za a yi komai ala ba shi duk inda za'a zauna aje a zauna, shi ne nace to ai ni ma ina da wa bari in zo in same ka!***

A cikn wasan *Jahilci ciwo a fitowa ta biyar* an yi hannunka maisanda ne dangane da irin illar da jahilci kan saka mutane ciki musamman na addini, na rashin sanin hakkin zamantakewar aure da sauran mu'amalar rayuwa. Misali daga cikin wasan:

***A'isha:*** ***Na ha]a kaya na, dama shi ne ya hana ni tafiya. Ai na gaya masa ba aure ya ce sai na zauna in zan fita ya kalallame ni da da]in baki. Ni ga akwatina nan duk na zuba kayana duka a ciki.***

***Usman:*** ***Na sake ta ne?***
***Ibrahim:*** ***Ey, ka sake ta, jahilcin banza da wofi.***
***Mudi:*** ***Saki uku?***
***Ibrahim:*** ***Ey, saki uku. Kuma ya hana ta tafiya?***
***Mudi:*** ***Ai ko garin da ba ilimi ba a wannan.***
***Ibrahim:*** ***Kuma haihuwa biyu gare su bayyan saki uku***
***Mudi:*** ***Bayan saki ukun kuma suna zaune tare? To Allah shi kyauta.***

***A'isha:*** ***Idan na }aurace masa ya hauni da duka.***

A fitowa ta bakwai ya yi nuni da illar jahili a ci gaba da wasansa. Misali:

***Usman: Muna zaune lafiya da mata ta in ]an abu ya taso ya ce wai… Ya ji a gari ana cewa wai na sake ta saki uku wai mun ci gaba da zama da ita. Shi ne ya zo ya dunga yin mini hauka, kuma ni duk lokacin dana saki yarinyar nan inna huce sai in ce na dawo da ita. Sau uku, amma duk da haka wai na yi laifi saboda Allah fa?***
***Malam Shehu:*** ***Usman ina ganin ka yi gamo***
***Usman:*** ***A'a.***
***Malam shehu: Ey, ai ina jin ka yi gamo Usman. Gaskiya kai gamo, mene ne naka na cewa har sau uku ka saki matarka, kuma ka dawo da ita. Mahaukaci ne kai Usman?***
***Usman: Ey… Ashe bakinku ]aya ne.***
***Malam Shehu:*** ***Shin ya buge ka? Ai Ibrahim sakarai ne, wallahi in da ni ne sai na buge ka saboda na tabbatar baka da hankali saboda babu yadda za a yi ka saki matarka saki uku ka ce ka dawo da ita. Yaushe ne ka sake ta saki uku?***
***Usman:*** ***Abu ya riga ya da]e.***

***Malam Shehu:*** ***Subhanallahi, ya da]e yanzu yara nawa ne?***
***Usman:*** ***Guda biyu ne bayan mun yi saki uku mum haifi 'Ya'ya biyu da ita***
***Malam Shehu:*** ***Subhanallahi la'ilaha illallahu.***
***Usman: Wannan abu fa ya da]e ba yanzu ba ne kuma an ce idan ka yi abu ya da]e ana yafe wa mutum shi.***
***Malam Shehu: Usman an sa mu makaranta, ba mun girma ne kawai ba mun yi makarantar allo ko ba ka yi ba ne?***

An ci gaba da yin hannunka mai sanda da mi}ewa a nemi ilimi don gudun kar a ri}a aikata aiki cikin jahilci, a wasan a cikin fitowa ta takwas domin jahilci ciwo ne:

***Usman:*** ***Na zo ne na ro}i wani arzi}i a wurinka, saboda ka san kai abokin Baban matata ne, shi ne na ce bari na zo na gaya maka wani abu.***
***Baba sarki: Wane abu ne?***
***Usman:*** ***Dama maganar mata ta ce wata rana na ta~a mata saki uku sai muka ci gaba da zama, shi ne wai sai nake ji a gari wai muna zaman zina ne, to wai shi ne yayyena suka zo suna ta yi mini fa]a.***
***Baba sarki: Yanzu ka zo ne ka gaya mun na shiga cikin wannan haram ]in. Yanzu idan shi Uban matar taka yaji wannan saki uku, sai ya ce wa yarinyar ta tattara kayan ta takoma gidanka, dana bar }ara magana da shi har abada to ko da gaya mun haka, to ba matarka ba ce.***
***Usman:*** ***To, Baba an ce wai idan mutun ya sayi tunkiya domin gyara wai malamai suna gyara auren.***
***Baba sarki: Da tunkiyan,da kuma malamin da zai yi gyaran duk wuta za su. Baka zuwa makaranta ne? Kuma ka tafi ka bani wuri.***

A fitowa ta tara an ci gaba da fa]akarwa kamar haka:

| | |
|---|---|
| ***Usman:*** | ***Assalamu alaikum A'isha, A'isha, A'isha, (ya ji shiru) Wato ta bi maganan wannan mahaukacin ta kwashe kayan ta, A'isha ko ta shigo kicin ne? wannan abu fa ya zama da gaske ni da na ]auki abun kamar wasa, (yana mamaki).*** |
| ***Ibrahim:*** | ***Ai'sha ta bar gidan, kuma wallahi kada ka kuskure ka sake zuwa wurin da yarinyar nan take ka ji ko? Idan ka }i za mu ha]a ka da 'yan sandan shari'a tunda kai ba ka zuwa makaranta. Ina halas 'ya'yan zuriyar mu ka zo ka da]a mana su da 'ya'yan haram saboda Allah da Annabi jahilci hauka ne Usman?*** |
| ***Usman:*** | ***Yanzu dai ta tafi shi ke nan?*** |

**3.4 Ma'anar Addini**

A cikin {amusun Hausa na Jami'ar Bayero Kano (2006:3), "Addini na nufin hanyar bauta wa Ubangiji." A takaice abin nufi a nan shi ne hanyar da a kan bi wajen bauta wa Allah. Haka kuma tsani ne da ake bi domin neman biyan bukata a wajen Ubangiji.

**3.5 Muhimmacin Addini da Tasirinsa ga Bahaushe.**

Addini na da matu}ar muhimmanci da tasiri ga rayuwar Hausawa tun kafin zuwan addinin musulunci da addinin masihiya Hausawa na da addininsu na gargajiya wanda yana da tisiri a rayuwarsu tun kaka da kakanni. Har ila yau M.S.Ibrahim, (1982), ya yi tsokaci game da addinin gargajiya na Hausa ya ce 'Shi ne bautar gumaka, watau, addini gargajiya ya wanzu ne ta bin wasu hanyoyi da mutane suka }ago wa kansu ta bautar wa]ansu abubuwa don cimma biyan bukatunsu. Irin wannan bautar ta da]e }warai a duniya'. Ya }ara da cewa 'Tsafi yana ]aya daga cikin addinin gargajiya na Hausa sai dai irin wannan bauta ba wani gunki ake sassa}awa ana bauta masa ba. Amma da yake yanzu yawancin Hausawa duk sun shiga cikin addinin musulunci, raguwar wa]anda ba su shiga ba su ake kira maguzawa kuma su ne har yanzu suke bin wannan addini.

### 3.6 Wasannin da suke {unshe da Addini a cikin Wasannin Duniya Budurwar Wawa

Addini na da tasiri a dukkanin mu'amala da Hausawa ke gudanarwa ta rayuwar yau da kullum don haka ne a kowane lokaci yake danganta aiyukansa da nufin Allah, a cikin wasannin marubuci yakan sa}ala al'amura da suke nuni da haka. A wasansa na 'Kowa ya bar gida…' a fitowa ta ]aya, ya yi nuni da:

***Shafi'u:*** ***Allah Ubangiji ya ha]a mu.***

A cikin wasan fitowa ta biyu akwai danganta mu'amalla rayuwa da koyarwar addini kamar haka:

***Iroro:*** ***Wallahi duk hul]a bana so in yi ta da banufe.***

***Nda:*** ***Haka ne! ai banufe zai gaya maka gaskiya ba zai maka dungu ba, amma abin da nake so yanzu ka ba ni kamar wata uku insha Allahu idan na samo zan kawo maka shi.***

***Iroro:*** ***Ni gaskiya ba zan ba ka wata uku ba Nda zan dai iya baka sati uku ka kawo mini ku]ina, idan baka kawo mini ku]ina ba ni kuma za ka ganni gidanka da 'yan sanda na dai gaya maka gaskiya!***

***Nda:*** ***To Allah ya taimakemu, Allah ya kaimu lokacin.***

***Iroro:*** ***Amin don nabiyyu rahamati.***

***Malam Jibo:*** ***Allah ya baka yadda za ka yi!***

***Nda:*** ***To sai anjima.***

A fitowa ta hu]u akwai koyarwar addini na tausayawa tsofaffi da taimaka masu wajen gudanar da rayuwarsu da suku saba da ita kuma sun fi mu'amalla da jikokinsu. Misali:

***Yusha'u:*** ***Ji mana Adodo, yanzu wannan da ba don imani ba, ba sai mu tafi mu }yale maka kayan ka ba, muga wanda zai yi maka.***

A fitowa ta bakwai, a wasan an yi Magana don wa'azantarwa musamman ga masu halin barin asalinsu ko }auyensu su zauna a bariki su haifi yara su kuma }i nuna masu asalin zuri'ansu kamar haka:

***Baba:*** ***Abin da Allah ya baka ka Haifa a duniyar nan ta Allah.***

***Baba:*** ***Kabar ]iyan ]iyanka su san daga ina babansu ya fito wane 'yan uwan baban naku.***

***Baba:*** ***Allah ya ce 'Aljama'atu rahamati'.***

***Iroro:*** ***Allahu akbar***

***Baba:*** ***Jama'a su ne rahama***

A gudummuwarsa ta fuskar addini a wasan "Mutum sai Allah". Bincike ya fara ganin koyarwa irin ta yarda da komai daga Allah ne kuma shi ne abin godiya kamar yadda aka fara a fitowa ta ]aya kamar haka:

***Kawu:*** ***Alhamdulillahi, mun gode Allah***

Haka kuma a fitowa ta uku a wasan bayan an ba shi aikin da ya zo nema sai ya yi godiya ga Allah kamar yadda koyarwar addini ya nuna. Misali:

***Kawu:*** ***Alhamdulillahi! Na gode madallah.***

Cikin koyarwar da addini ne ya yi ya kasance komai na duniya da ]an Adam ya samu daga Allah ko ya rasa daga gare Shi ne. Ta dalilin haka ne a cikin fitowa ta shida ya yi nuni da:

***Iroro:*** ***Amman dai ina son in }ara nuna maka cewa Allah shi ya halicci bawansa kuma shi yake azurta bawansa.***

A cikin wasan da marubuci ya rubuta mai suna "Rayuwa" a fitowa ta ]aya an fara wasan ne da koyarwar da addini ta hanyar fa]akarwa da ha}uri da mai da komai na rayuwa in ya same ka daga Allah ne kamar haka:

***Usman: Ka yi ha}uri Baba. Don saboda a gaskiya Baba, abin da ka rasa Allah, in ka samu Allah. To amma ni a gaskiya Baba da wani irin hali,***

***wanda yake babu dangana, ya kamata duk abin da keke yi Baba, in ka rasa ka dinga dangana, Allah ne ya baka shi kuma ya hanaka. Irin sakon da ka yi min wurin shi wannan Alhaji Shafi'u, irin maganganun da ya fa]a min ban ji da]insu ba.***

***Alhaji Shehu: To dakata, wato ni ka ga dai kenan, ni fa]a maka kari}a dangana, ka ri}a yin komai tsakaninka da Allah. Wato shi ne ni kuma yanzu zaka ce ba ni da dangana, wato ka gane!***

A wasansa da ya rubuta mai suna: "Jahilci Ciwo", ya yi }o}arin nuna yadda addini yake da tasiri a cikin rayuwar Bahaushe musulumci dangane da yadda shari'ar zamantakewar aure da sauran mu'amallarsa kamar haka a fitowa ta ]aya:

***Kaka: Wani ne***

***Salamatu: Ai gara mutuwa da shi.***

***Kaka: Subahanallahi!***

***Salamatu: Ba wani abu ba ne sai dai tsakanin Ai'sha da mijinta domin tun tuni zaman banza suke yi, ya saketa sau ]aya, ya saketa sau biyu ya saketa sau uku, kuma suna tare. Kuma a takaice yaran biyu an haife su bayan an yi duk sakin ne.***

***Kaka: Subahanallahi!***

***Salamatu: To ina gani bai dace ba shi ya sa nace gara in zo in fa]a miki domin ranar lahira ba mu san abin da za mu ce ba.***

***Kaka: Subhanalillahi! Wannan wace irin tijara ce ]aki ba rufi an ce sai bayan an yi saki uku sannan aka sake haihuwar yaran? Lallai shege baya tsakanin saurayi da budurwa sai dai tsakanin mata na aure da mijinta. Yanzu yaran nan biyu duk bayan da aka yi sakin ne ake haifesu?***

A fitowa ta biyu cikin wasan an ci gaba da nuni da koyarwa irin ta addinin musulunci a kan zaman aure, kamar yanda shari'a ta yi umurni da haramun

ne ga ma aurata su ci gaba da zaman aure bayan saki uku ga abin da 'yan wasan ke fa]i:

***Salamatu:*** ***Baba abin da ya faru wata gagarimar Magana ce na mani ita wannan yarinyar a ta}aice dai ya yi mata saki uku, da kansa da yara uku sannan da ga baya suka haifi yara biyu to wa]annan yara biyun an haifesu ne bayan anyi saki nan uku.***

***Baba:*** ***Wato yara biyun?***

***Salamatu:*** ***Ey wato ni kuma abin sai ya kasance yana damu na har kasa barci na ke yi sai dai banci barawo, sai na gaya wa kaka, sai ta ce na zo na gaya maka ni kuma ina jin nauyin gaya maka sai ta ce in zo in gaya maka don a san abun da za a yi saboda duniya nan gidan banza ce domin idan sun kasance a haka gobe kiyama mai za su ce wa Allah?***

A fitowa ta biyar, 'yan wasan sun ci gaba da fa]akarwa game da zaman aure kamar yadda shari'a ta ce:

***Ibrahim:*** ***Allah bai tsine wa shegu ba da kuma wanda ya ajiye su?***

***Mudi:*** ***Duk tsinannu ne.***

***Ibrahim:*** ***Mutun ne ya saki matarsa saki uku bayan sakin uku nan sai suka ci gaba da zama har suka haifi yara biyu.***

***Mudi:*** ***'Ya'yan zina ne kawai wa]annan.***

Kamar yadda masana suka ba da gudummuwarsu a game da addinin da Bahaushe yake bi, mafi yawancinsu addinin musulunci suke bi, don haka al'adunsu da ]abi'unsu duk sun karkata ne ga koyarwar addinin. Addu'a, mutum ke fara yi ko ya sa a taya shi ko kuma ma ya sa wani malami yin addu'a a kan wani abin da yake nema. Don haka ma a wasansa mai suna 'Mutuwar Zuciya', a fitowa ta biyu aka yi nuni da irin halin 'yan siyasa misali:

***Shafi'u:*** ***To yanzu dai Mallam, so muke a roka mana Allah ya zamanan…***

***Mallam:*** ***Na dai fahince ku.***

***Usman:*** ***Kowa muka tunkara yasa hannu a aljihu ya ciro ku]i ya ba mu.***

***Shafi'u:*** *Yauwa, kwarai kuwa, an saba kuma abin amma…*

***Mallam:*** *To amma Shafi'u da Usman tun da Allah yayi ku ya kaddara samunku da rashinku, abin da ya yi nufin za ku samu babu wanda ya isa ya hana, babu kuma wanda zai baku abinda ba'a kaddara maku ba.*

***Shafi'u:*** *To amma ai an ce a yi addu'a ko?*

***Mallam:*** *Ei, kwarai kuwa addu'a tana da amfani kwarai da gaske*

***Shafi'u:*** *To amma na ji kana karya mana guiwa ne.*

***Mallam:*** *A' a a a, ai ita addu'a ana so ka dunga yi ne, ba sai kana cikin matsala ba.*

***Usman:*** *To yanzu dai Mallam me ake biya abin hasafi na addu'a?*

***Mallam:*** *A'a ya zan fadi? Ni nake biyan bukatan ? ai ba ni nake biyan bukatan ba. To ni dai zan gaya ma Allah don shi ne ke biyan bukata.*

***Shafi'u:*** *To ba aiki muka saka ba?*

***Mallam:*** *To in an sa ni aiki ai ba ni nake biyan bukata ba, ni iyaka ta da ku alkawarin da na ]auka naku zan gaya ma Allah don in sauke.*

***Usman:*** *Wato kai dai baka yanke abinda za a ba ka ke nan.*

***Mallam:*** *To ya zan yanke? Inda zan yanke da sai ince ku je wurin wane ya ba ku kaza.*

***Shafi'u:*** *Kwarai da gaske. Mallam amshi wannan, ba'a fa nema da sanya.*

***Mallam:*** *Kwarai da gaske, Mallam don Allah a taimaka mana.*

***Mallam:*** *A'a ba komai in Allah ya yarda ba ma ni ka]ai zan nema ba Mallam Nasiru da Mallam Bala, domin mu taru mu gaya ma Allah, duk wanda*

| | |
|---|---|
| | ***kuka tunkara ba ma gidan gwamna ba ko wane ne.*** |
| ***Shafi'u:*** | ***Kwarai Mallam Dubu dari, Dubu Dari Biyu*** |
| ***Mallam:*** | ***Har ma Dubu Dari Biyar in sha Allahu.*** |

**3.7 Ma'anar Siyasa**

A cikin littafin {amusun Hausa na Jami'ar Bayero Kano(2006:397), An kasa ma'anar siyasa har kashi hu]u.

(i) Tafiyar da al'amuran jama'a ta hanyar neman ra'ayinsu da shawarwari da su.

(ii) Rangwame musamman a ciniki.

(iii) Dabara ko wayo.

(iv) Iya hul]a da jama'a.

Ma'anar a cikin littafin *Oxford Concise Dictionary of Politics (2003:422-423)* shi ne, Manufofi da ya shafi sha'anin rayuwar yana iya kasancewa ta kowace hul]a ko na tsakanin mace da namiji haka kuma yana iya kasancewa }ar}ashin inuwar mulki guda na siyasa don tafiyar da gwamnatin.

**3.8 Muhimmacin Siyasa da Tasirinsa ga Bahaushe.**

Ha}i}a Bahaushe ko al'ummar Hausawa mutane ne masu ma'amalla da sauran jama'a ta kowace fuskar rayuwa don samun ci gaba kuma da maraba da ci gaba idan ya zo cikin su. Ta dalilin haka siyasa tana da muhimmanci ga ci gaban rayuwar al'ummar Hausawa musamma ta fuskar jagoranci da kasuwanci da sauran mu'amalla na rayuwar yau da kullum don ta nan ne yake jawo ra'ayin jama'a a lokacin da ya fara hul]a da su, wannan yana faruwa ne tun kafin shigowar ba}i cikin al'ummar Hausa. Siyasa na da tasiri ga rayuwar Hausawa musamman da juyin zamani ya shiga cikin jama'ar Hausawan sai ya ]auki irin na zamanin ya ha]a da nasa kamar yadda masu Karin Magana ke cewa "zamani riga ce" Don haka siyasar zamani ta }ara wa al'ummar Hausawa wayewa da gogewa ta wajen shugabanci da sauran al'amuran rayuwa.

**3.9 Wasannin da suke {unshe da Siyasa a cikin Wasannin Duniya Budurwar Wawa.**

A wannan fage na siyasa marubuci wasannin da ake gudanar da binciken irin gudummuwarsa wajen bun}asar wasan kwaikwayo ya ba da nasa a fage fa]akar da jama'a musamman talakawa da }ananan 'yan siyasa a kan abin da ke gudana a fagen harkar mulkin siyasa da zaben masu mulkin kamar a wasansa mai suna: 'Mutuwar Zuciya', a fitowa ta biyu kamar haka:

| | |
|---|---|
| ***Shafi'u:*** | ***Gaskiya dai al'amura ne suka cabe na yanayin siyasan nan ne. To mu dai mun saba yadda muke zuwa muna 'yan harkokinmu muna samun na cefane da na kashewa, nan gidan Gwamna a gidan gwamnati wajen 'yan siyasa.*** |
| ***Malam:*** | ***Ei, kwarai-kwarai.*** |
| ***Usman :*** | ***Kafin ayi zabe ba, ka fa]a masa.*** |
| ***Shafi'u :*** | ***To Allah cikin ikonsa*** |
| ***Usman :*** | ***Kafin a yi zabe.*** |
| ***Shafi'u :*** | ***Ai ya san komai.*** |
| ***Usman :*** | ***Duk inda muka tafi, muka sami abin da muke so.*** |
| ***Mallam :*** | ***Na'am!*** |
| ***Usman :*** | ***Mu ciko aljihunmu a wajen 'yan siyasar nan har mu ma mu wadata wasu.*** |
| ***Mallam:*** | ***Wannan gaskiya ne.*** |
| ***Usman :*** | ***To amma tun da aka ce an gama komi na bangaren siyasar. To haka mu ma an gama da mu fa! yanzu haka muke tsaye cik.*** |
| ***Mallam :*** | ***Wato kun gama aiki ke nan. Subahanallah, Allahu akbar.*** |
| ***Usman :*** | ***Yanzu haka muke tsaye cik komi ya tsaya mana.*** |
| ***Shafi'u :*** | ***Kasan wani abun mamaki ne ?*** |
| ***Mallam:*** | ***To amma kuma kuna zuwa gidan Gwamna?*** |
| ***Shafi'u :*** | ***Da ana ganin, ganin Gwamnan shi ne aiki to yanzu sai ka gan shi haka haka nan kuma za ka tashi.*** |
| ***Usman :*** | ***Ba wani bayani?*** |
| ***Shafi'u :*** | ***Sai ka gan shi to amma ba wani abu.*** |

| | |
|---|---|
| ***Mallam :*** | ***Ido da ido?*** |
| ***Shafi'u :*** | ***To abun mamaki. Mu dai mun rasa abin da ya faru. Ko dai wani ne ya shiga gabanmu?*** |
| ***Usman :*** | ***Kuma duka wani wanda ka sani. In dai dan siyasa ne muka ce salamu alaikum zai miko mana hannu har mu samu, amma yanzu sai dai ]aga hannun daga nesa.*** |
| ***Shafi'u :*** | ***E! akwai wani wanda yake neman takara a lokacin sahun gaba yake zama in an zo sallah a masallaci amma yanzu sahun ba yake zama don kar mutane su gan shi ta yanda da an yi sallama daga sallar sai ya saka takalminshi ya yi gaba.*** |
| ***Mallam:*** | ***Allahu Akbar*** |
| ***Usman:*** | ***Ko addu'a ma ba ya tsayawa yi.*** |

A ci gaba da gudummuwarsa na ilmantarwa da fa]akar da jama'a a cikin wasanninsa ya yi hannunka mai sanda ga jama'a na irin halin da 'yan siyasa su ke yi musamman bayan an gama za~e in za~a~~un sun shiga ofishinsu kamar haka:

| | |
|---|---|
| ***Gwamna:*** | ***To ina jinku Dattijo.*** |
| ***M. Bala:*** | ***To abin da ya zo da mu mai girma Gwamna, mun zo ne domin ina son in yi maka tuni ne, don kasan lokacin da ake neman alfarma wajen jama'a lokacin zabe kenan. To ni ne nake wakilcin mutane a wannan shiyyar namu. To ga shi yanzun an gama komai an zauna kuma kasan lokacin da kake neman wannan takara ka yi ma jama'a alkawura cewa za ka yi masu kaza da kaza, to yanzu sun sa ido kuma kasan in wani abu ya taso mu za'a nufa da shi.*** |
| ***Gwamna:*** | ***Yes.*** |
| ***M. Bala:*** | ***To sai aka ga duk alkawuran da aka yi babu wanda aka duba, shi*** |

*yasa mutane suka fara damuwa, nace to in Allah yaso zan zo in same ka in tuna maka, in an yi alkawari to fa kaya ne ko da shekara nawa to alkawarin na nan, wannan ne yasa nace bari in yi maka tuni ka cika ma mutane alkawuran da aka ]auka, dama wannan ne ke tafe dani.*

**Gwamna:** *To Sidi fa?*

**Sidi:** *Ya mai girma Gwamna, to duk tafiyar ]aya ce, domin duk yanayin da ake bi baya ne, domin duk lungu-lungu da aka bi da ni aka bi, dama ai duk fatawar iri ]aya ce zancen alkawuran da aka yi wa mutane.*

**Gwamna:** *To abin da ke tafe da ku ke nan? To abin da nake so ku gane shi ne: ku]in da ake samu a wancan lokaci babu a wannan siyasar na biyu, sannan abin da aka samu a da babu shi a yanzu, kuma ni na shiga siyasa ne wato abin da ake cema "tun ran gini tun ran zane" amma ni ba na so, domin sai ka yi karya a siyasa.*

**M. Bala:** *Lallai kuwa, kwarai da gaske.*

**Gwamna:** *Dole sai ka yi alkawarin da ba za ka iya cikawa ba, don na tabbata wasu alkawuran da na yi ba zan iya cikawa ba domin in ba ka yi karya ba, ba ka yi alkawarin da ba za ka iya cikawa ba, wasu burikanka ba za su cika ba.*

**Sidi :** *Mutane ba zasu saurare ka ba, ba za ka samu kuri'un jama'a ba.*

**M. Bala:** *To amma Yallabai, wannan ai kun ]aure kanku ne, ya kamata ku dunga cewa in Allah ya yarda, ka*

| | |
|---|---|
| | *ga in bai yiwu ba da ma sun san cewa ka ce in Allah ya yarda.* |
| *Gwamna:* | *A'a da ma ni na kan ce da izinin Allah a zuciyata, in na yi-na yi sai in ce da izinin Allah.* |
| *M. Bala:* | *To shike nan Yallabai.* |
| *Gwamna:* | *To yanzu dai sai a yi hakuri lokacin da Allah yasa ku]i suka zo za mu duba mu ga muhimman abubuwan da ya kamata, a je dai a }ara hakuri don Allah.* |
| *M. Bala:* | *Sai kuma Magana ta biyu Yallabai.* |
| *Gwamna:* | *Ei, ina jinka.* |
| *M. Bala:* | *Koda yake na ji bayaninka yanzu, amma abin da aka saba yi to ni dai na ji shiru kwana biyu.* |
| *Gwamna:* | *Ai ka ji Dattijo, shi ne abin da na yi maka bayani, abin da ke akwai da yanzu babu su, babu kudi.* |
| *M. Bala:* | *Ai mu muna ganin an yi shigan farko da na biyu ba'a bukatan na uku shi ya sa ba a waiwaye mu ba.* |
| *Gwamna:* | *A a, zargin da kuke ke nan?* |
| *Sidi:* | *Allah ya sani haka muke zargi, don mutane suna cewa da kana da sauran bukatan da ka waiwaye su.* |
| *M.Bala:* | *Suna ganin shi ya sa aka rike* |
| *hannu* | |
| *Gwamna :* | *A'a, wallahi ba haka ba ne, abin da ake samu da, yanzu ba shi kada ku yi wannan zargi.* |
| *M. Bala :* | *Amma duk da haka ya kamata abin da aka saba yi mana a yi mana.* |
| *Sidi :* | *Kwarai sai an daure.* |
| *Gwamna :* | *P.A !* |
| *P.A :* | *Na'am !* |
| *Gwamna :* | *Don Allah ka kira mana PAMSEC.* |
| *P.A:* | *To Yallabai, (Tafiya)* |
| *P.A:* | *(ya dawo)Yallabai ga yi nan.* |
| *PAMSEC:* | *Ranka ya da]e gani.* |

*Gwamna:* *Don Allah akwai ku]i wurinka?*
*PAMSEC:* *Ei, akwai.*
*Gwamna:* *To ka ba Dattijo Naira Dubu Hamsin*
*PAMSEC:* *Mallam Balarabe?*
*Gwamna:* *Ey, ka ba Baba Sidi Naira Dubu Talatin*
*PAMSEC:* *To Yallabai.*
*Sidi da M. Bala: To Yallabai mun gode, Yallabai mun barka lafiya.*

Sai kuma a fitowa ta biyar cikin wasan nan ma an yi nuni da irin halin 'yan siyasa na bin wa]anda aka zaba ofishinsu kamar haka:

*Usman:* *Abin da ya kawo mu shi ne so mu ke mu ga His Excellency.*
*Moda:* *To ai ba ka sani ba, saboda sabon da na yi da S.S, da Police da Security na gidan nan da na tunkaro sai a ba ni wuri.*
*Mal. Isah:* *Sai a bu]a ma motarka, ba a tare ta ba.*
*Moda:* *Ai na riga na zama ]an gida.*
*Mal. Jibo:* *To don Allah muna so mu ga mai girma Excellency.*
*Moda:* *To don Allah ku ]an yi hakuri ku jira ni.*
*Haladu:* *Ku bari ya je ya isar da sa}on kun zo.*
*Shafi'u:* *A'a da ma ai mu muna jira ne.*
*Mal. Isah :* *Kai yi sauri ka je ka dawo.*
*Usman :* *Amma mun da]e ba mu sadu ba fa (ya tafiya)*
*Moda :* *Ranka ya da]e ka wuni lafiya?*
*PAMSEC :* *A'a Moda! Moda!!*
*Moda:* *Ranka ya da]e ko Excellency yana ciki?*
*PAMSEC:* *Ey, yana ciki.*
*Moda:* *To don Allah ina son ganinsa ne.*
*P.A:* *A a, ka shiga mana.*
*Moda:* *To madalla, (Tafiya)*

***Moda:*** ***(gyaran murya), Allah ya taimake ka!***

***Gwamna:*** ***Na'am Moda.***

***Moda:*** ***Allah ya }ara maka sutura, Allah ya }ara maka Imani.***

***Gwamna:*** ***Amin! don nabiyyirrahmati.***

***Moda:*** ***Ranka ya da]e ai ba}i ne suka zo ganinka shi ne na ce to bari na yi masu iso, wasu wa]anda aka yi harkokin siyasa da su ne, suka zo, to shi ne na ce su tsaya in sanar da kai cewar su na son ganinka su yi gaisuwa.***

***Gwamna:*** ***To sai ka zama zaginsu.***

***Moda:*** ***To ranka ya da]e duk ba}on da ya zo wurinka gidannan in ban masu iso to mene amfanin zamana a gidannan? Ai ba shi da amfani ke nan.***

***Gwamna:*** ***Wai Moda kai wai me ya sa ina ganin kamar kana da hankali, amma baka dashi?***

***Moda:*** ***Ya aka yi ranka ya da]e.***

***Gwamna:*** ***Kullum ba ka da burin zucci, kullum kana nan kana takama da ni, kullum kuna nan gidan in ba}i sun zo 'yallabai, ranka ya da]e, Allah ya taimakeka, 'Yallabai ya sanyi! 'Yallabai ya zafi? Da sun zo. Yallabai a sauka lafiay har gindan moto. Shin wai baka tunanin wata rana Moda? Shin in ba ni gidan nan ya za ka yi?***

***Moda:*** ***Ranka ya da]e wannan ai daban ne.***

***Gwamna:*** ***In gari yawaye ka je ka samar ma kanka abin da za ka yi ka ci da kanka ko kana nan gindana, to yau in aka ce ba wannan gidan ya za ka yi?***

***Moda:*** ***Wannan fa daban, amma ranka yada]e tun da kana nan wallahi ba zan iya barinka ba, ai ba na iya rabuwa da kai wallahi, indai kana gidannan kana gwamna.***

***Gwamna:*** ***To, in ba niba ne Gwamna fa?***

***Moda:*** ***To, sai in nemi wani hanyar daban.***

***Gwamna:*** ***Yau idan aka ce Allah ya ]auki ran Gwamna Iro, za ka bi shi ne?***

***Moda:*** ***A'a sai mu yi maka addu'ar halin da ka yi nagari ya bi ka ya raka ka gidanka.***

***Gwamna:*** ***Moda don Allah a rage mutuwar zuciya.***

***Moda:*** ***To ranka ya da]e ya za mu yi?***

***Gwamna:*** ***Ka rika tsayawa kana nema, amma ina amfanin kullum ka rin}a tsayawa nan, ni aikin da nake yi kuna hana ni, kullum kuna wannan wurin ga wannan ya zagi wancan ya zo, alkawuran da na yi wa jama'a ba ku bari ni na ida masu ba, kun hana ni inyi aiki, shin zan ji da ku ne ko ko da aikin da aka rantsar dani akai?***

***Moda:*** ***Ey! To, za kai aiki Yallabai amma jama'a kake ma aikin kuma jama'a suka zabe ka.***

***Gwamna:*** ***Je ka ce su shigo.***

***Moda:*** ***To, yallabai.***

***Gwamna:*** ***A'a mutane ku hana ni in yi aiki kullum wa]annan su zo wancan gruf su zo wancan gruf su zo.***

***Mal. Jibo:*** ***Your Excellency ranka ya da]e barka da aiki***

***Gwamna:*** ***Mal. Jibo barka da zuwa, Shafi'u barka da zuwa.***

***Shafi'u:*** ***Ey ranka ya da]e ya aiki ya gwagwarmayar siyasa?***

***Gwamna:*** ***Alhamdu Lillahi.***

| | |
|---|---|
| ***Shafi'u:*** | ***Kai amma ranka ya da]e na da]e ban zo nan ofis ]in nan ba, mun kai wata shida ba mu yi ido biyu da kai ba sai dai in ganka a moto ka wuce.*** |
| ***Gwamna:*** | ***Tun lokacin da ku ka zo murna ke nan?*** |
| ***Shafi'u:*** | ***Kwarai da gaske.*** |
| ***Mal. Jibo:*** | ***Kasan gwagwarmaya da mu ka yi na siyasa.*** |
| ***Shafi'u:*** | ***Ai wannan ba a tunawa, shi ya sani ya san komai game da yanayin siyasar da ake ciki da jama'a a yazun, kar ma ka yi wahalar ba shi labari.*** |
| ***Usman:*** | ***Lokacin wani mara kunyan yaro ya kai man sara na kwanta sannan na samu na sace akwatin }uri'an zaben da aka yi.*** |
| ***Shafi'u:*** | ***Kasan kuwa har lahira yai niyyar kai ka.*** |
| ***Usman:*** | ***Da shike dai da rabon shan ruwa!*** |
| ***Mal. Jibo:*** | ***Da mu ma ko lokacin bukatarmu ka sami wannan kujera kuma Allah ya yi ka zama Gwamna.*** |
| ***Gwamna:*** | ***Allah sarki.*** |

Bayan wa]annan sun fita sai {ungiyar mata 'Yan Siyasa su kuma suka zo su ma ga abin da ya gudana a fitowa ta shida.

| | |
|---|---|
| ***Gwamna:*** | ***A'a mutane kun hana ni aiki.*** |
| ***P.A:*** | ***Your Execellency, wasu mata ke jiranka.*** |
| ***Gwamna:*** | ***Kai billahillazi da Gwamnan kasuwa na tsaya kowa ya fito ya gan ni a fili gani nan da ya fi.*** |
| ***P.A:*** | ***To ya za ka yi tun da Allah ya ba ka mukami, ha}uri za ka yi*** |
| ***Gwamna:*** | ***Kullum so suke Hypertension ya kama ni? Sun hana ni yin ma mutane aikinsu, sai wannan group su zo wancan su zo? Na gaya maka wallahi idan da akwai gwamnar*** |

***kasuwa to da shi na nema, kowane ]an iska yazo ya ganni kuru-kuru. Su wane ne kuma?***

***P.A:*** ***Wasu mata ne.***

***Gwamna:*** ***Ce masu su shigo.***

***P.A:*** ***To ku shigo.***

***Mata:*** ***Salamu Alaikum, Salamu Alaikum…***

***Gwamna:*** ***Shugaba?***

***Shugaba:*** ***Allah ya ja zamaninka ya biya bukata.***

***Gwamna:*** ***Amin, yauwa sannunku, lafiya lau, aiki da godiya, na gode***

***Mata:*** ***Allah ya taimake ka***

***Gwamna:*** ***Shugaba ai kun yi yawa, da kun koma kun na]o guda daya (you are too many)***

***Shugaba:*** ***Ai ba komai maganar ba mai tsawo ba ce.***

***Gwamna:*** ***To mene ne?***

***Shugaba:*** ***Gaisuwa ce dai da rokon iri ranka ya da]e.***

***Gwamna:*** ***Ai ka ji, kash!***

***Shugaba:*** ***Yallabai ya za a yi?***

***Salamatu:*** ***Wato yanzu ne muka yi yawa ko? Amma ai lokacin zabe ba mu yi yawa ba.***

***Shugaba:*** ***Bai kamata ki fa]a mai haka ba, ai shi ba yaro ba ne ya san komai.***

***Gwamna:*** ***Ai yanzu gwamnati nake ma aiki, nan ofishin Gwamna ne. Kai mene ne dai ko ko dai...***

***Shugaba:*** ***Mun zo gaisheka muna gaisheka da aikin da kake mana.***

Yana ]aya daga cikin gudummuwarsa ta wajen fa]akar da jama,a idan sun shiga cikin wata matsala ga hanyar da za su fita a sauwa}e kamar yanda ya yi hannunka mai sanda ga irin wa]annan shuwagabannin a cikin wasan nasa mai suna Mutuwar Zuciya a fitowa ta bakwai kamar haka:

***Gwamna:*** *Kiranka na yi ka ba ni shawara an zabe ni in yi wa mutane aiki amma mutane sun hana ni yin aiki, kullum group su zo wancan ma su zo su fita, kuma ba da wani tunani sai dai personal matter nasu ba wai kan aikin da ya shafi mutane ba, to gaskiya abin ya yi mani yawa shi ne na kira ka a matsayinka na tsohon ma'aikaci ka ba ni shawara.*

***PAMSEC:*** *To an bar shiri tun rani.*

***Gwamna:*** *Assha! Assha!!*

***PAMSEC:*** *An bar shiri tun rani, wato, tun lokacin da ake kanfen wanda suke binka su ne wanda suka zama uwa da uba a wurinka domin su za su kawo maka kujera, da suka kawota sai ka ga bai kamata ka barsu ba, kowane yana ta}ama shi ya fasa akwati ko shi ya sace akwati ko a gidan shi ne aka shirya yanda za a yi, ko ni ne na ta da fa]a a wurin don kada a yi zabe sai dare ya yi.*

***Gwamna:*** *Kwarai duk su Mallam Jibo haka suke fa]i, to yanzu ya za a yi a rabu da su?*

***Mal. Shehu:*** *Ai zai yi wuya, ni fa ma'aikacin gwamnati ne ba ]an siyasa ba ne.*

***Gwamna:*** *Ai duk ina da labari, kwarai har da wannan mahaukacin Moda.*

***PAMSEC:*** *To ai da gaskiyanshi, shi da ake wani yaro yaso ya sare kanshi ta kan ya hana a fasa akwati.*

***Gwamna:*** *To ai mu ne na gaban Gwamna! Ko kara muka gilma mashi ba zai tsallaka ba, haba! Haba! Ai abin ya yi yawa.*

***PAMSEC:*** *To ai kai ka sake 'Yallabai.*

***Gwamna:*** ***To yanzu ina mafita, ya za mu yi mu tsai da wannan abu?***

***PAMSEC:*** ***To na farko dai a sa lokacin ganinka daga lokaci kaza zuwa lokaci kaza, kuma a wannan lokacin babu wani aiki da za ka yi in sun kai dubu minti ]ai-]ai, iyakaci ke nan kuma amsarka ey ko a'a, zan maka ko ba zan maka ba, sai kuma wa]anda kuka taso tare ko wa]anda suka ranta maka ku]i kayi kamfen. To wa]annan ko tataunawa za ku yi sai ku yi, amma ba…***

***Gwamna:*** ***To ni zan sa a buga a manna a baki }ofa.***

***PAMSEC:*** ***Amma ranka ya da]e ka yi hakuri kar ka ce na zake, gaskiya in ba haka aka yi ba ba zai yi wu ba.***

***Gwamna:*** ***In maida ganina kawai ranar Juma'a daga safe zuwa lokacin masallaci***

***PAMSEC:*** ***In kuma ka sa haka kar ka canza, sai kuma in an yi ba}i daga wani wuri daban ba 'yan siyasa ba.***

***Gwamna:*** ***Sai in manyan baki ne, sai in karbe su in ba haka ba kuwa sai juma'a, juma'a.***

***PAMSEC:*** ***Da masu zuwa maka firar banza da wofi, da masu firar babu gaira babu sabab.***

***Gwamna:*** ***Zauna gari banza zaka ce.***

***PAMSEC:*** ***A'a zauna gidan gwamna banza dai, in ba su ka dakatar ba, ba za ka huta ba, amma ka yi hakuri fa!***

***Gwamna:*** ***A'a, ai haka za a yi, zan sa masu gadi su sare mani mangwaronrin gidan nan***

| | |
|---|---|
| ***PAMSEC:*** | ***To ai ita suke sha kafin ka fito ka sallame su, da safe ai ita suke sha muna ganinsu ta taga*** |
| ***Gwamna:*** | ***Mangwaron da safe? Subhanalillahi! To Allah wadan mutuwar zuciya*** |
| ***PAMSEC:*** | ***In rana ta yi kuma su sha inuwa.*** |
| ***Gwamna:*** | ***To na gode in Allah ya so haka za mu yi, zan yi proper arrangement, in Allah ya so haka zan yi, in manyan ba}i sun zo ga yanda zan yi, zan gyara wannan na gode fa.*** |
| ***PAMSEC:*** | ***To ranka ya da]e, in dai ba haka ka yi ba ba za ka samu nasara ba har abada. Ko za ka sake shiga wani zaben ne nan gaba, to in ka gyara gaba ai sai baya ta syi kyau.*** |

**3.10 Kammalawa**

Wannan babi yana }unshe ne da zantukar wasannin da aka gudanar da bincike a kan su a inda aka za}ulo zantukan da suka shafi fagen Ilimi da Addini da Siyasa aka yi }o}arin masu sharhi daidai gwargwado don ganin ya taimaka a fagen ci gaban wasan kwaikwayo don gano irin gudummuwar da marubucin ya ba da ta wa]annan fuskoki don fa]akar da masu sha'awar wasanninsa. Sannan kuma babin na }unshe da ma'anar kowane fanni da muhimmancisa ga Bahaushe daga irin gudummuwar da masana suka ba da.

**BABI NA HU[U:**

# GUDUMMUWARSA TA FANNIN AL'ADA DA TATTALIN ARZI{I DA ZAMANTAKEWA.

## 4.0 Gabatarwa

A Babin da ya gabata an dubi irin gudummuwar da marubucin ya ba da ta fuskar Ilimi da Addini da Siyasa a cikin wasannin da aka zaba aka yi nazarinsu. A wannan babin za a fito da irin gudummuwar da ya ba da a cikin wasannin da aka nazarta ta fuskar Al'ada da Tattalin arzi}i da Zamantakewa a inda za a le}a a ga irin gudummuwar da ya ba da wajen bu}asa wasan Kwaikwayo. Haka kuma a wannan babin ne za a yi nazari a kan ire-iren jigogin da marubucin wasan ya yi amfani da su wajen isarda sa}onsa ga masu sauraron wasanninsa da kuma yanda yake sanyawa wasanninsa suna daga cikin jigon wasanninsa, haka kuma za a dubi irin yanayin gudummuwarsa a kowa ne wasan da aka yi nazarinsa a wannan binciken. To amma da farko dai bari a ]auki ma'anar al'ada mu gani.

## 4.1 Ma'anar Al'ada.

Akwai ma'anoni da dama da masana suka ba al'ada cikinsu akwai littafin {amusun Hausa na Jami'ar Bayero Kano(2006:9) ya yi bayyanin ma'anar al'ada har kashi hu]u kamar haka: (i) hanyar rayuwar al,umma (ii) jinin haila (iii) wani irin hali daban na mutum (iv) magani ko tsafi.
Shi kuma (M.S.Ibrahim 1982:13) ya ba da nasa ma'anar al'ada da cewa:

(i) Al'ada tana nufin haila watau irin jinin nan da mata suke yi wata-wata
(ii) Tana kuma nufin bin wata hanya don yin maganin gargajiya misalin yin karatu, ko tofi ko turare ko zubar da jni da sauransu.
(iii) Sa'an nan tana nufin abubuwan da mutum ya saba yi a cikin rayuwarsa ta duniya. Ta kuma shafi yanayin rayuwar al'umma da harkokin da suke yi don zaman duniya.

A tasa ma'nar A.M.Bunza, (2006:xxxii) Al'ada tana nufin dukkanin rayuwar ]an Adam tun daga haihuwarsa har ya zuwa kabarinsa. A ko'ina mutum ya samu kansa duk wata ]abi'a da ya tashi da ita tun farkon rayuwa ya tashi da ita tun farkon rayuwa ya tarar a wurin da ya rayu ko yake rayuwa ita ce al'adarsa da da za a yi masa hukunci a kai.

## 4.2 Muhimmacin Al'ada da Tasirinta ga Bahaushe.

Masana da dama sun ba da gudummuwarsu cikinsu akwai Adamu,M.T, (1997:16), ya ce: "Hausawa mutane ne masu tsananin ri}on al'adansu na gargajiya, musamman wajen tufafi, da abinci da al'amuran da suka shafi aure ko haihuwa ko mutuwa da sha'anin mu'amala tsakanin dangi da abokai da shugabanni, da kuma sana'a ko kasuwanci ko neman ilimi da sauransu".

Ya }ara da cewa Adamu,M.T, (1997:16), "Yawancin Hausawa Musulmai ne, saboda haka mafi yawan al,adunsu da suka shafi aure da haihuwa da mutuwa duk sun dogara ne da yanda addini ya nuna. Sai ]an abin da ba a rasa ban a daga al'adun gargajiya, musamman a wajen Maguzanwa. Haka wajen mu'amala da iyaye ko dangi ko abokai ko shugabanni ko ma}wabta ko wanin wa]annan' yawanci na musulunci ne. Haka kuma sana'a da kasuwanci da neman ilimi duk a jikin Musulunci suka rataya."

Dangane da irin wa]annan gudummuwar da da masana suka ba da ne game da al'adar Hausawa zamu iya cewa su al'umar Hasawa mutane ne masu wayewa da sanin yakamata tu kafin zuwan Turawa cikinsu to amma ko bayan zuwan su har yanzu suna ]aya daga cikin al'ummomin da ba su bar al'adarsu ta gargajiya ba sun ]auki wani sai dai tasirin zamananci da ya shiga cikin al'adun a sanadiyyar sauyin zamani kamar yanda masu karin Magana ke cewa: "kayan aro abin banza ne in mai abin ya karbi abinsa, sai ka koma naka" ko "kayan aro ba ya rufe katare".

**4.3 Wasannin da Suke {unshe da Al'ada a cikin Wasannin Duniya Budurwar Wawa.**

A Al'adar Hausawa musamman wajen neman Aure suna ba da muhimmanci ga sani asalin danginsu kuma har ma in ba a san iNda mai neman aure ya fito ba ko ta fito ba ko ma zuri'arsu yana da wuya auren ya yuwu don haka a wasan 'Kowa ya bar gida… a fitowa ta ]aya" an yi nuna muhimmanci asali. A lokacin da A'isha ke neman sanin inda asalin gari da Iyayensu saka fito suka zo nan gari Kaduna cikin birnin da aka haife su amma su ba su san asalin }auyensu ba, kamar haka:

| | |
|---|---|
| ***A'isha:*** | ***To amma bayani shi ne, ni ina son in san asalin zuri'anmu a yi auren a can to a tafi can tushen maganin a je a yi a wurin ma'ana a tafi can inda iyayen namu suka fito a je a gabansu, mu san inda suke su san mu ma kuma muna nan shi ne bayani.*** |
| ***A'isha:*** | ***A a ka ga Shafi'u tsaya ka bi ni a hankali ba wai wani Maganan*** |

***abin da za'a kasa yi ba ne a nan ni dai bayanina shi ne ka bi ni mu tafi mu nemo ainihin inda mahaifana suke Shi ne bayani, don duk abin da za a yi in dai maganar aure ne to can fa za a yi shi.***

***Malam Jibo:*** ***Sai ta san asalinmu, shin iyayenmu daga wani }auye suke, ba ta son a yi komai a bariki.***

A fitowa ta shida ya nuna al'adar wasu Hausawa wa]anda suka fito daga karkara suka shigo birane don ci-rani suka yi arzi}i kuma, su manta da asalinsu su kuma }i bayyanawa yaransu asalinsu wanda shi ne yake ]aya daga cikin sa}on da wasan 'Kowa ya bar gida…'

***Dattijo:*** ***Amma kai duk inda kuka je kai Allah shi yi muku albarka kai da ku yarda ku ri}a ~oye sunan nan muna da wani al'ada namu mara kyau, inda muka je sai mu yi shekaru, mu yi haife-haife mu yi arzi}i mu}i fa]in garinmu***

***Malam Jibo:*** ***To halim Kanawa ke nan?***

***Dattijo:*** ***Kuma mun bar garin nan ba mun yi laifi ne ba balle a ce kar mu dawo da baya.***

A wasan 'Mutum sai Allah," a fitowa ta uku, akwai al'adar da aka nuna ta Hausawa wajen godiya wanda ta zama jiki kamar haka:

***Kawu:*** ***Alhamdulillahi! Na gode, madallah.***

**4.4 Ma'anar Tattalin Arzi}i.**

Daga cikin littafi {amusun Hausa na Jami'ar Bayero Kano(2006:432) na nufin: Tanadi ko kula ko ajiye wani abu don yin amfani da shi nan gaba.

**4.5 Muhimmacin Tattalin Arzi}i da Tasirinsa ga Bahaushe.**

Bahaushe bai yarda da zaman banza ba a rayuwarsa da dukkanin mu'amalarsa don haka ya kan yi Karin Magana da cewa "Ba maraya sai rago". Kuma mafi yawancin hanyar da Hausawa kan bi wajen neman tattalin arzi}insu ya dogara ne da irin albarkar da Allah ya yi wa }asar Hausa mafi yawancin Hausawa manoma ne sai kuma kasuwanci kamar yanda Adamu,M.T, (1997:14), ya yi bayani inda yake cewa "Noman da Hausawa ke yi ya }unshi na ci da kuma na sayarwa. Haka kuma bishiyoyin da ke

}asar Hausa babu mara amfani akwai na ci kamar tsamiya, kanya, kurna, ]orawa, ka]anya, aduwa tsada, faru da sauransu. Bayan ci ma ana amfani, da itacen wajen sassa}e-sassa}en kayan amfani, kamar }otoci, akushi, }oshiya, kujera, turmi da tabarya da sauransu, sannan ga magunguna. A wani fannin kuma, Allah ya yi wa}asar Hausa albarkar dabbabi da tsuntsaye, na gida da na dawa sannan kuma ga baramu wato ma'adanai, kuma tun daga Azurfa da Tagulla da Tama da ba}in {arfe, har zuwa kan Kwalli da Darma da Kanwa da Gishiri da jar {asa da farar {asa da jan gargari da bakuwa da koya ga duwatsu iri-iri da marmara da sauransu."

Idan aka dubi irin wannan gudummuwar game da Tattalin arzi}i da irin albarkar }asar Hausa yasa su alummar Hausawa ba su yarda da zaman banza ba su kan ce "Sana'a sa'a rashin sana'a sata". Don haka yasa suke da sana'o'i daban-daban kuma Allah ya hore masu hikima da basira wajen sarrafa albarkatun }asar da ke kewaye da su na cikin }ar}ashin }asa da na sararin doron }asar kai har ma na cikin kogunar da ke yankin }asar Hausa, har ma suna fita zuwa fatauci da ci-rani a ma}wabtasu don tattali arzi}i da tsumi da tanadi kamar yanda masu karin magana ke cewa "ba maraya sai rago."

**4.6 Wasannin da Suke {unshe da Tattali Arzi}i a cikin Wasan Duniya Budurwar Wawa.**

Masu Karin magana ka ce 'Ku]i masu gidan rana" Rayuwa bata inganta sai da ku" haka a cikin wasan 'Kowa ya bar gida… a fitowa ta ]aya" an nuna tasirinsu ta wajen neman asalin zuri'ar su A'isha a lokacin da maganar aurenta ya taso a inda take cewa:

***A'isha:*** ***To ni yanzu na san abin da yake dubawa, yana duba maganar ku]i ne, ban ce ne ni ban ce ina son sisi nashi be.***

***A'isha:*** ***Ni zan ]auki nauyin tafiyarmu da dawowarmu da duk abin da za a kashe ni na ]auki nauyi.***

***Iroro:*** ***A'isha ta ]ebo aiki subuhanalillahi kai ni da ina jinka maganar ku]i na?***

A cikin fitowa ta biyu ta wajen mu'amallar kasuwanci tsakanin Iroro da Nda akwai alkawari biyan bashi na ku]i wanda a lokaci an zo ma da Iroro wata maganar amma hankalisa na wajen ku]insa misali:

***Iroro:*** ***Amman ya muka yi da kai da, cewa ka yi yau zaka kawo mini ku]in nan.***

***Nda:*** ***To naje na nema ban samu ba, wa Nda na ke son in je wurinshi da naje sai na samu kukan da ya ke mini yafi nawa saba da haka nake son ka taimaka mini kwanannan insha Allahu idan na samu zan kawo maka.***

***Iroro:*** ***A'isha ta ]ebo aiki subuhanalillahi kai ni da ina jinka maganar ku]i na?***

***Nda:*** ***Me na gaya maka Alhaji Wallahi yanzu bani da ku]i bani da ma hanyar da zan samo wa]annan ku]in yanzu.***

A fitowa ta hu]u akwai harkar kasuwanci na sayar da goro wanda aka san Hausawa na zuwa cin kasuwa don sayarwa kamar haka:

***Malam Shehu:*** ***{warya nawa ka }irga a goron nan?***

***Yusha'u:*** ***{warya takwas ne na }irga a ciki.***

***Malam Shehu:*** ***To a ]aure na fasa, ba za a siyar da shi ba a wannan kasuwar.***

***Yusha'u:*** ***To yanzu kaka wannan goron da ka ce a bai wa wancan mutumin ga shi nan har yanzu bai zo ya ]auka ba.***

***Malam Shehu:*** ***Gara in ]auko lebura inda zan sa }afa in daki mutum ku]ina su yi aiki.***

***Malam Shehu:*** ***Ba makwabta ba duk garin a ji ni, haka nake kuma Allah ya yi mini arziki.***

***Adodo:*** ***Kaka wannan jaka hamsin ]in bari in in ajiye ta a gida.***

A wasansa mai suna 'Mutum sai Allah" an yi nuni da yanda neman ku]i ko bashi a wajen mutanen da kuke zaune a waje ]aya ko kuma gari ]aya ko 'yan'uwa ko ma kuna da zumunci, a fitowa ta hu]u kama haka:

***Hajiya:*** ***Sai ka zaga gida goma baka samu }wandala ba!***

***Hajiya:*** *Rashin ku]i ai ba abin da ba zai faru ba sai dai in ka kai zuciyarka nesa*

A fitowa ta biyar ya yi nuni da jin da]in kyautar ku]i in aka yi wa wani

***Baba Dattijo:*** *Kwanaki dai ]an ku]in nan da ka taimaka min na ji da]i*

A wasansa mai suna Mutuwar zuciya a fitowa ta hu]u an nuna yanda 'yan-siyasa suke bin ofisoshin zababbun suna neman ku]i.

***PAMSEC:*** *Mallam Balarabe ga Naira Dubu Hamsin ya ce a baka sai tukuici. Sidi ga Naira Dubu Talatin ya ce a baka sai tukuici. Ka san yaba kyauta tukuici.*

***M. Bala:*** *To ai ni ban gane ba don na riga na yi godiya*

***PAMSEC:*** *A a wancan shi ka yi wa godiya amma wannan ni za ka ba wa nawa tukuicin.*

***M. Bala:*** *Au to! Daga bangarena ga Naira Dubu Biyar.*

***Sidi:*** *To ni kuma ga Naira Dubu Biyu.*

***PAMSEC:*** *To na gode Allah ya saka da alheri, Allah ya saka da alheri, to shi ke nan.*

***Sidi:*** *Muna godiya (Tafiya).*

***M. Bala:*** *Kai ba ka fahimci abinda suke ciki bane domin su ma'aikatan nan albashinsu ba ya isansu don na fahimci kana son wani bayani shi ne na ce bari in maka. Shi ma'aikaci ba wani abu yake samu fiye da kai, don albashinsu ba ya isansu, ana cire masu harajin ku]in gida, ku]in ruwa da sauransu. Daga }arshe sai kaga ba su da wani abin da ya kamata, to irin wannan 'yan buge-bugen da bin na gaba shi ne za su samu su ]an warke.*

***Sidi:*** *Yauwa, haka ne? Allah sarki.*

| | |
|---|---|
| ***M. Bala:*** | ***Ai ka ga ya nuna irin bukatarsa a kai, wannan shi ne abin da ke jawo haka don haka suke fama da shi, ka gani.*** |
| ***Sidi:*** | ***Allahu Akbar, Allah ya }ara wadata mu amin.*** |
| ***M. Bala:*** | ***Amin ! Amin !!*** |

**4.7 Ma'anar Zamantakewa.**

An ba da gudummuwa da dama don bayyana ma'anar zamantakewa misali, a cikin littafin {amusun Hausa na Jami'ar Bayero Kano, (2006:489) nuni da; Zamantakayya zaman tare wanda kan jawo sha}uwa da juna.

A nasa bayanin ma'nar zamantakewa M.S. Ibrahim (1982:117), Ita ce hanyar rayuwa manufa a nan shi ne 'Tun kafin zuwan addini musulunci Bahaushe yana da hanyarsa ta rayuwa wadda ya gada tun Iyaye da Kakanninsa ta sa'anin aure haihuwa mutuwa da ciniki abinci sutura tarbiya da wajen zama'.

**4.8 Muhimmacin Zamantakewa da Tasirinsa ga Bahaushe.**

Hausawa na ba zamantakewa muhimmanci a rayuwarsu ta yau da kullum har su kan ce "zo mu zauna zo mu saba wannan hali ne na zaman tare" kuma su kan danganta ta da zumunci da cewa 'zumunta a }afa take'. Don haka tasirin zamantakewa a tsakanin al'ummar Hausawa da]a]]i]en al'amari ne domin tun kafin zuwan ba}insu suke da ita kamar yanda (M.S.Ibraahim 1982:117) ya yi bayani "A lokacin da musulunci ya zo sai ya kawo sauyi dangane da rayuwar Bahaushe. A wani wurin ya bar ta kamar da, a wani wurin kuma ya gyara ta ko ya sauya ta baki ]aya. Misali dangane da zaman tare ko lokacin da Bahaushe yake maguzancinsa yana yin biyayya ga iyayensa yana taimakonsu. Haka kuma yana zumunci da 'yan uwansa sukan ha]a kai su yi noma tare, sukan kuma taimaki juna idan akwai bukatar, kamar buki ko suna. Sukan yi, kuma }o}arin rama wa ]an uwansu idan wani ya zalunce shi da sauran irin su.

Halayyar zamantakewa da zumunci na Hausawa sunada dama don }arfafa zamantare da juna don masu iya Magana kan ce: "zo mu zauna zo mu saba" haka kuma "zumunci a }afa ta ke" don haka bahaushe bai wasa da abokin zamansa wato bai son abin da zai bata masa rai.

**4.9 Wasannin da Suke {Unshe da Al'amuran Zamantakewa a cikin Wasan Duniya Budurwar Wawa**

A wasansa na Duniya Budurwar Wawa mai suna 'Kowa ya bar gida…" An fara da yin nuni ne da yanda samarin da 'yan matan zamani ke

tafiyar da zamantakewarsu musamman ‘yan boko kamar haka: A fitowa ta ]aya

***Shafi’u:*** ***Wato Yaya abin da ya sa ka ga na ]an nuna damuwata, ita wannan baiwar Allah. Allah ya sa ni ina matsanancin son ta, kuma tun ma ba ta kammala karatunta ba, na digiri.***

***Shafi’u:*** ***To amman tana kawo wa]ansu cikas, wanda na rasa inda ta dosa da wa]annan cikashin na lokacin auren nan namu.***

***Shafi’u:*** ***Abin kuwa yana damu na matu}a, ba don komai ba saboda in za a yi abin nan ya dace a yi shi a kan lokaci, ba wai a yi ta ja in ja ba ko kuma ana ta kai kawo ba a yi gaba a yi baya ba, to shi ya sanya na ce ni zan zo, a kira ta ga ta ga ka, mu tsaida wannan magana shin wane lokaci ya dace mu ba yara ba ne daga ni har ita ba yara ba ne.***

***Shafi’u:*** ***Duk da cewa ba mu yi aure da wuri ba dai amma ai ba zamu ]auki kanmu a matsayin yara }anana ba.***

***Shafi’u:*** ***To wannan shi ya sanya na ce bari in zo in sake yi ma magana a kira ta mu daddale tunda ba wani abin jin kunya cikin wannan magana, don haka kira ta gani ga ta ga ka.***

Wa]annan zantukan da ‘yan wasan suka yi irin hali ne na zamantakewa tsakanin saurayi da buduwa masoya junansu da zamantakewar aure. Sai kuma a fitowa ta bakwai marubucin ya yi nuni da a rin}a bayyana wa yara asalinsu.

***Baba:*** ***Ya kamata yara su sani, ko baka da rai sun san inda ‘yan uwan babansu suke asalinsu ba zai zamar musu abin damuwa ba, su can sun gane ai ‘yan uwan***

***babanmu asalinsu 'yan gari kaza ne.***

***Baba:** **Kai amma yaran nan sun kyauta mini ba ka]an ba, ai duk wanda ya bar gida dole gida ya bar shi, kuma ya kamata mutane su dinga lissafi yanda kullun Allah shike da kayansa, Allah ya sa mu cika da imani, Allah kuma ya sa mu gama lafiya.***

A wasansa mai suna "Mutum sai Allah" an yi nuni da muhimmancin aikin zumunci a fitowa ta ]aya kama haka:

***Hajiya:** **To saboda haka nake so don Allah don Annabi kawu a taimaka mashi na san kai ma duk da yake ko ina ana cin arzikin juna ne, to kai mai jama'a ne kuma na san insha Allah wannan abu ba zai gagare ka ba.***

A fitowa ta biyu an nuna muhimmancin zaman tare a wasan

***Malam Balarabe: Eh don Allah ka ji mutumin nan bawan Allah nan tun muna 'yan }anana muke tare da shi wai zai zo waje na ne, ba zai zo kai tsaye ba wai sai ya yi mini waya tukuna***

A wasan 'Mutum sai Allah" a fitowa ta uku an nuna muhimmanci sanayya da zumunta ta abokantaka jawabin ya bayyana mana irin }imar da aboki ke da shi a wajen abokinsa kamar haka:

***Malam Balarabe:Haba Alhaji Shehu, wannan abu mai sau}i insha Allahu.***

A wannan wasan a cikin fitowa ta shida an nuna irin yanayin da ]an adam kan nuna idan wani abun farin ciki ko ba}in ciki ya same shi ya kan nemi da ya bayyana wa wa]anda suke tare domin su taya shi murna ko ba}in ciki misali kamar haka:

***Iroro:An ba ni na ga wasu allawus-allawus duk ana ba ni da ma. Malam Jibo duk mutumin da ka ga Allah ya ]ora wa talauci kar kai mai dariya, kar ko kai mai sharri,***

***arziki na Allah ne ba uban wani ke ba da shi ba irin yadda ka ke zuwa fuw ka wuce ni da mota Alhaji na ji labarin har cewa ka ken a tabu to Allah ya warkar da ni, yanzu da ka ke gani na nan kana cewa Iro ya tabu, to ban tabu ba.***

Sannan a fitowa ta shida ne cikin bacin rai ya }ara da cewa:

***Iroro:** **Wai dai in gaya maka dai na tabbata kana daga cikin masu surutu cikin garin nan. Ai Alhaji Iro ya haukace, ba shi wannan kwalbati ba shi wannan gindan itace, to ga shi nan Allah ya ba ni, yanzu aiki ya samu.***

Sai ya mayar masa da amsa cikin lallashi domin ya nuna masa muhimmancin zamansu tare da aminci don kar su yi tashin hankali.

***Malam Jibo:** **A'a to meye na tashin hankali Alhaji Ibrahim? Ai ni amininka ne.***

***Malam Jibo:** **Ni ba mai ba}in ciki ba ne.***

***Malam Jibo:** **Murna ne a gare ni yau in ji an ce ka zama wani abu.***

Akwai hikimar da maigida kan bi wajen sanar da uwargida sa}o na yanayi halin zaman tare musamman a kan maganar kishiya kamar yadda aka nuna a cikin wannan wasan a fitowa ta takwas kamar haka:

***Iroro:** **To na ga dai bai kamata in zalunce ki ba, ko kuma in munafince ki ba ya kamata dai ko mi ne ne dai in ri}a fitowa ina gaya miki.***

***Hajiya:** **Dakata, yauwa don Allah ka yi mini magana ]aya kawkkwara yadda zan fahimta, ba na son wannan kewaye-kewayen kamar Banufe.***

***Iroro:** **Ba kya son randa-bawul.***

***Hajiya:** **A'a ba na son kewano.***

***Iroro:** **To abin da za a yi.***

***Hajiya:** **Kana ta kewayewa kana }arawa.***

*Iroro: Eh maganar aure ne wanda za a ]aura jibi kada a yi abin nan ki ce ba ki sani ba ki zo ki ce na ci amanarki.*

*Hajiya: Allah sarki.*

*Iroro: Shi ya sa na ce gara in zo in shaida miki ki sani eh, jibi ne ]aura auren.*

*Iroro: Shike nan maganar dama eh shike nan da ma wallahi tuntuni ina so in gaya miki ina jin nauyi.*

*Hajiya: Na me? Allah ya kawo lokaci.*

*Iroro: Eh }warai da gaske aure ibada ne na ce.*

A fitowa ta sha]aya an nuna yanda ake zamantakewa tsakanin mata a cikin gida da miji musamman zamantakewar kishiyoyi misali:

*A'isha: Maigidana na kaina (dariya)*

*Iroro: Lafiya dai ko?*

*A'isha: Eh! Lafiya lau.*

*Iroro: To.*

*A'isha: Amma dai gaskiya ina da Magana.*

*Iroro: To! To!! Ta mece ce?*

*A'isha: To ka ga dai Salamatu yaya ta ce a cikin gidan nan.*

*Iroro: Eh!*

*A'isha: To ni sai inganta tana salla-laf-salla-laf a cikin gidan nan ba irin kuzarin nan uhm!*

*A'isha: Sai kace ruwan kudidifi, ba harka ba komai ita dai dankama sunan wani gari, bini-bini tana dan}ame a ]aka.*

*Iroro: Eh!*

*A'isha: Ba za ta fito ba balle mu yi hira, ni ke nan ni ka]ai a tsakar gida, yanzu da ka zo ba ga shi ba.*

*Iroro: Eh! }warai fa.*

*A'isha: Ina ta walkami ina oyoyo maigida yanzu ba kiji da]i ba?*

*Iroro: Wallahi gaskiyarki, ni ma abin nan ya fara isata, gaskiyarki fa*

*A'isha: Ni gaskiya ba na jin da]i, so nike idan ka shigo yadda nake ta tarenka da murna to sai*

***ta je ta ]an kame a cikin ]aki abin duk ya ]aure mini kai.***

***Iroro:To na yarda da maganarki bar ni da ita.***

***A'isha:To shike nan.***

A nan ne aka nuna maganar da aka zuga amaryasa da ta yi masa ya yarda da maganar kuma har ya ]auki mataki a kai kamar haka:

***Hajiya: (salati) Sannu da zuwa.***

***Iroro:Ke don Allah ki ri}a amsa mini magana kin ji ko?***

***Hajiya: Ah-ah-ah!***

***Iroro:Ya ina zama da mace kamar ina zama da tunkiya, wallahi ba ni son mace ba kazar-kazar, wallahi sai in shigo gida bacin rai, can waje a ~ata mini rai sannan gida a ~ata mini rai, mata ba za tai kazar-kazar sannu da zuwa sannu da zuwa ka dawo lafiya ana fara a ka dawo lafiya, kamar ina aure da tunkiya, to ni fa bana son irin wannan, wallahi ki canza, idan ba za ki canza ba ni sai in canza miki wallahi kina amfanin irin wannan, in zauna da mutum kamar alade dim kullum ]aki kullum kina cikin ]aki ko irin fitowa ki sha iskar nan ma ba kya yi.***

***Hajiya: Ka gama?***

***Iroro:To ni fa ba zan yarda da irin wannan ba ki ri}a kazar-kazar don Allah***

***Hajiya: Yi ha}uri.***

***Iroro:Yanzu da na auro wannan yarinyar har na fara jin da]i wallahi***

***Hajiya: Allah sarki.***

***Iroro:Da na dawo sannu da zuwa sannu da zuwa- sannu da zuwa.***

***Hajiya: Yi ha}uri.***

***Iroro:To ki canza in ba za ki canza ba ni sai in canza miki ba na son sakarci.***

***Hajiya: Ka gama dai ko?***

***Iroro:Na gaya miki.***

***Hajiya: Ka gama?***

***Iroro:In shiru-shiru nake son in auro 'yar kurma mana, an ta~a yi mini tayin 'yar kurma na ce ba na so, ba na son irin wannan don Allah.***

A fitowa ta sha uku marubucin ya nuna muhimmancin matsayin Iyaye ta fuskar zamantakewar aure idan rashin fahimta ta shigo a tsakanin miji da matarsa idan suna zaune a wuri ]aya don gudun aikata kuskure misali:

***Hajiya: To madalla, na zo cikin sauri ne.***

***Safiya: To lafiya dai ko?***

***Hajiya: Wani abu ne yake damuna, na ga ba zan nufi gidan Iyaye na ba dole ne in zo wurinku saboda yanzu duk abin da na yi za a ce saboda an yi mini kishiya ne.***

***Safiya: Haka yake***

***Hajiya: Abin da ya faru ina zaune na idar da sallah ina unn…***

***Zuwaira: Karatu?***

***Hajiya: Sai na ]an kishingi]a haka in ]an huta sai ya shigo mini da sababi, wai ni ba na kazar-kazar ni mene ne –mene ne, idan ban canza halaye na ba da dai sauransu, wai shi zai canza mini kazar-kazar, to shi ne na ce bari in zo in gaya maku.***

Sai kuma a fitowa ta sha hu]u inda marubucin ya ci gaba da nuna matsayin iyayen ta fuskar zamantakewa.

***Hajiya: Ka saman mishi aikin nan da ku]in alawus ]in nan nashi ya yi mini kishiya kafin ma a ce an yi bikin sannan ya gaya mini, na ce mishi Allah ya sanya alheri, ban ce mishi komai ba, na }yale shi, kuma ina hidimomina yarinyar nan ta zo ba wani abu tsakani na da ita ni ban nuna mata ba ita ma ba ta nuna mini ba, muna zaune lafiya, shi ne kawai yau ya zo yana yi mini masifa kazar-kazar.***

***Kawu: To dakata, ina zuwa (salati) Adodo?***

***Kawu:Ka ba ni kunya, ka kuma ba ni haushi, ban tsammani za ka yi haka ba, wato an ba ka aiki an ba ka rance ka gyara gida za ka watsa gida, ba a hana ka yin aure ba, amma ka san abin da ka ke yi.***

A fitowa ta sha biyar ya nuna abin da maigida ya kamata da ya yi idan an samu rashin fahimta a gidansa misali:

***Iroro:Salamatu don Allah don Annabi ki yi mana aikin gafara, abin da ya sa kika ga na yi auren nan da ma ina da niyya, kin san yanzu mutuwa gudu take, nan da nan sai ki ji an ce ba wannan ba wannan.***

***Hajiya:Dama kai ne in gida ya lalace kai ne in gida ya gyaru kai ne.***

A cikin wasansa mai suna; "Rayuwa," ya yi fa]akarwa a fitawa ta biyu dangane da halin zamantakewar aure kamar yanda addini ya shar]anta kamar haka:

***Hajiya: Wato duk abin da ya ha]aka da iyalinka bai kamata kace idan tai maka wasa yanzun nan za ka saketa ba, saki wani babban abu ne ga Ubangiji Subhanahu wata'ala saboda haka duk abin da zaka yi tsakanin ka da iyalinka kada ka yarda wani ya ji bare har ya je yana }araswa. Ni ban ji da]in irin wannan kalamai da kake yi ba, idan ranka ya bata, domin ni ya kamata in zo in gaya maku gaskiya ko kai ko ita duk ]aya ne a wurina, tun da Allah ya sa ka auri wannan yarinya, to kuma ni da mahaifinka ko mahaifiyarka duk ]aya ne nake gani, abin da na ga ka yi wanda yake ba dai-dai ba, ina da 'yancin in yi maka fa]a tsakanina da Allah. In ka ji ya yi maka kyau in ba ka ji ba shi ke nan.***

***Alhaji Ibrahim:*** ***Na ji Hajiya.***

***Hajiya:Ni abin da ya kawo ni ke nan, saboda iyayenmu malamai ne, suna magana a kan saki, mutane da yawa suna ta lalata aurensu game da ainihin maganar saki, saboda haka motsi ka]an sai ka ji an ce yanzu za ki kwashe kayanki ki bar gidannan, yanzu zan sake ki. To ka tuna fa kai namiji ne mijin mata hu]u kuma komin yawan da muka yi a duniya ba za mu rasa masu auren mu ba, saboda haka, ni abin da zan gaya maka ke nan, ka kiyaye don Allah.***

***Alhaji Ibrahim:*** ***To shi ke nan Hajiya, na gode Hajiya.***

Hausawa kan ce "zo mu zauna zo mu saba" haka yake ta wajen zamantakewa a kan samu sabani ko da tsakanin harshe da ha}ori haka kuma a kan samu sha}uwa ga irin abin da ma aurata suke ba wa junansu shawara idan an samu rashin fahimtar da har iyaye suka shiga tsakani a wannan wasan mai suna Rayuwa. A cikin fitowa ta biyu:

***A'isha: To ni dai ina baka shawara, in nai maka laifi in za kai min fa]a ka ri}a kwantar da muryarka.***

***Alhaji Ibrahim:*** ***Ke ni fa ban son sakarci idan mun yi abunnan a dinga barinshi nan.***

***A'isha: In kana fa]a ka rin}a rage murya, ta yadda babu wanda zai san halin da ake ciki.***

Sai kuma a fitowa ta biyar inda ake bai wa mata shawara a kan ri}on gida

***Hauwa: Gaskiya yaya ya zo ya taimaka mana a wannan halin da muke ciki. Wai shin ke a matsayinkin na matarshi wai shin kina fa]a mai gaskiya kuwa? Don in gida ya gyaru mace ce, in kuma ya baci ma ita ce. Don inkin ha]a kanmu da shi sai muji da]i.***

A yanayin zamantakewar al'ummar Hausawa akwai shugabanci don haka idan wani abu ya faru cikin al'ummar a kan je don neman shawara kamar yanda aka nuna a fitowa ta shida wasan a "Rayuwa."

***Alhaji Shehu:*** ***Wato abin da Shafi'u ya yi min ba zan manta ba har abada a nan gidan duniyar, ya wula}antani ya wula}anta ni irin maganganun da ya fa]a wa yarona ma, da ya zo kasa fa]a min ya yi.***

***Mai Unguwa:*** ***Wato saboda abin yana da nauyi ba zai iya fa]a wa mahaifinsa ba.***

***Alhaji Shehu:*** ***Sai har yana cewa da ni "wa]anda na ba arzi}i suna nan wai har yana kiran Iron, ai su ka taimakawa, ban da shi ma ka taimaka wa dubbai me ya sa ba za ka je wurinsu ba." sai na kwantar da murya na ce ka yi wa Allah ka taimaka don na ji an ce kana taimakawa, sai ya taso min da fa]a. "ba zan yi ba, ba zan yi ba". Sai na ba shi ha}uri, hakan na taso ba nauyi.***

***Mai Unguwa:*** ***To ai ba ka ji ba kana dai jin yin fa]a ne kawai, don kuwa ya fa]a maka gaskiya ne. don kuwa ba shi daga cikin wa]anda ka taimakawa.***

***Mai Unguwa:*** ***(ya ci gaba da tambayar Alhaji Shehu) wato yan zun ko ha]uwa ba kwa yi da shi ke nan? Don na ji kana tambayar wai ina za ka gan shi?***

***Alhaji Shehu:*** ***Ni abin da yake bani mamaki da mutanen Arewa ]an'uwa yana da arzi}i, amma 'yan uwanshi sai ka ga wani sakar zana yakeyi, wani Allah-Allah yake yi kaka ta yi ya tafi kalar gya]a, wani ruwa yake ]ebowa ya saida don ya samu abin da zai ci. Amma na nesa sai ka ji***

*an zo ta hanyarka yin godiya saboda wane ya yi min abu kaza.*

*Mai Unguwa: Wannan al'ada ce ta mutanen Arewa, wanda ya zama dole mu ajiye ta gefe guda, mu so namu. Tun da yanzu idan 'yan uwanshi masu arzi}i suka zo aka ce musu wannan ]an uwanshi ne, zai ji da]i?*

*Mai Unguwa: Mutane ya kamata su san abin da suke yi, da ha}}in ma}wabta, da ha}}in 'yan uwa ba a yi wasa da shi saboda gaba.*

*Mai Unguwa: To! yau kai Ibrahim wannan wane ne?*

*Alhaji Ibrahim: Alhaji Shehu ne.*

*Mai Unguwa: Yaushe rabonka da ganinshi?*

*Alhaji Ibrahim: Ey tun kwanaki da ya yi mura, mun ha]u da shi a bakin kasuwa mun gaisa.*

*Mai Unguwa: Wato ba ma gidan ka je ba ke nan? Ina so in nuna maka cewar Alhaji Shehu lokacin da yake cikin ganiyar arzi}insa, yana da dukiya sosai kuma ni nasan ya taimaka wa mutane. Kuma kai da kanka ka zo nan kana so in ha]a ka da Alhaji Shehu don ya taimaka maka ya saka ka ta hanyar da yake ]auko kaya. Amma ka ga halin da Alhaji Shehu yake ciki kuma ko gida ka ce baka zuwa sai dai ku ha]u a hanya. Kai sai ma an ce maka ka je ka gaida shi, ko kuma ka yi masa wani abin alheri?*

*Alhaji Ibrahim: Wato, wallahi Baba bani da lokaci ne.*

*Mai Unguwa: Har kai yanzu wani mai ku]i ne nan ina su Dan Karuna? Kuma komai ku]inka yau, kai ina Sayyadina Abubakar ne? wanda yake shi taimakon jama'a kawai yake yi.*

*Alhaji Shehu: Randa ya gan ni a kasuwa, ina cinikin buhun dawa ina ce zai biya min, amma sai cewa ya yi shi ke nan ni na tafi. Ban ma }ara sani abin da ya ce ba sai ya yi gaba, nima ko da na ji an ce an sallama maka sai nai gaba saboda ba ku]in biya.*

*Mai Unguwa: Ba wai ya zo ya kawo }ara ba ne, a a abin da ya kamata a ce mutum ya yi ne aka fa]a maka. Amma abin da nake so ka yi yanzu ka ro}e shi gafara.*

*Alhaji Ibrahim: Alhaji Shehu ka yi ha}uri, don Allah ka ya fe mani, kuma zan zo gida duk abin da ya kamata in yi zan yi kuma basussuka da duk ake bin ka zan zo duk in bibbiyasu. kuma ni na san abin da zan yi.*

*Mai Unguwa: Kuma ban ji da]i ba }anwarka ta zo jiya take gaya min irin abin da ka yi mata ka ce wai karta sake zuwa gidanka.*

*Alhaji Ibrahim: Ta zo Baba wancan satin na ]auki ku]i har Naira ]ari (#100) na ba ta.*

*Mai Unguwa: A yanda kake kai mai arzi}in nan mene ne naira ]ari. Idan ba ka taimaki 'yan uwanka ba, to su wa za ka taimaka?*

*Alhaji Shehu: To ko za a taimake ni ya fara ba ni a nan kada ya fita daga nan ya mance da ni.*

*Mai Unguwa:Ai zai baka tun da ya ce zai baka.*

*Alhaji Shehu: To shi ke nan.*

A fitowa ta bakwai cikin wannan wasan halin al'adar zamantakewa tsakanin ma aurata kan kawo zargi a 'yan'uwa kamar yadda aka nuna ya kamata abin da iyaye da surukai su ri}a yi idan sun samu labarin abin da ke tafiya a gidajen 'ya'yansu kamar haka:

*Alhaji Ibrahim: Hajiya sannu da zuwa.*

*Hajiya: Yauwa, a gurguje nike abin da ya kawo ni shi ne, idan za ka kyautata wa 'yan'uwanka ka kyautata musu tsakaninka da su karka goga wa yarinyar nan ba}in jini ka san dangin miji yadda suke kuwa? Kullu yaumun za su ce ita*

*matar nan ita ta hana ka. Kana so ka rin}a jawo mata ba}in jini bakin gwargwadon abin da Allah ya hore maka ka dinga taimaka musu don Allah. Ni dama abin da ya kawo ni ke nan.*

*Alhaji Ibrahim: To Hajiya na gode, kuma in sha Allahu zan gyara Hajiya ki gai da gida.*

*A'isha: To Alhaji ka dai ji abin da ta ce.*

*Alhaji Ibrahim: Ey na ji don Allah a yafe ni, Baba ma ya kira ni duk maganar da yake fa]a min ke nan. Ni wani lokaci sai in dinga tunanin in ku]in nan suka }are yaya zan yi, ina zan samo wasu? Ni kinji abin da yake hanani sakin ku]i kenan.*

*A'isha: To ai in ma ka ba su Allah zai fi bu]a maka (Allah na gode maka, yanzu ya gane. Masu hali irin nashi, Allah ya sa su gane su ma su daina.)*

A fitowa ta biyu a wasansa mai suna "Jahilci Ciwo," an yi nuni da irin tarbiyar da Hausawa kan yi wa yaransu musamman ta fuskacin addin da sauran al'amurar rayuwa ta yau da kullum ga inda uba ke wa ]ansa fa]a a cikin wasan domin ya gyara yanayin zamantakewar rayuwarsa na duniya.

*Baba: Ni wannan yaron kullum idan na tashi fita sallar asuba na bu]e }ofar gida na kan tashe shi }arfe biyar domin ya yi sallah amma ba zai tashi ba sai }arfe goma na safe yake tashi to wai mene ne dalilin da ya sa yake haka ne?*

*Baba Sarki: Ga kuwa kiran sallah an yi.*

*Baba: Ina yi maka wannan abu tun muna da rai, idan ban yi maka wannan abin ba mai za ka ce tsakanin ka da Allah.*

*Adamu: Baba wallahi ban dawowa da wuri ne*

*Baba Sarki: Kai Adamu ka tuna kana bauta wa Allah mu tsakanin mu da ku tarbiya da ilimi mun ba ku ilimi da tarbiya ku yi aiki da shi idan ku ka }i za mu sa muku ido a kan abin da ku ke yi tun muna da rai.*

***Adamu:*** ***Wallahi ban dawowa da wuri ne idan na yi hira da daddare na dawo na kwanta sai na ji na makara.***

***Baba:*** ***Duk wani yaron arzi}i daga sallar magariba zuwa sallar isha har zuwa }arfe goma sai mutum ya dawo gida.***

***Adamu: Baba in sha Allahu na daina ba zan }ara ba***

***Baba: Idan ma ba ka bari ba ni na san abinda zan yi***

***Adamu:*** ***Na gode Baba.***

***Baba Sarki:*** ***Kar ka bi yaudaran samari fa, akula fa.***

A fitowa ta hu]u a cikin wannan wasan an nuna muhimmancin gudanar da bincike idan ana da tunanin wani abu na faruwa atsakanin zamantakewar aure kamar haka:

***Ibrahim:*** ***Ya tsakanin zamanka da kai da matarka?***

***Usman:*** ***Babu…Ba komai muna zaune lafiya sumul.***

***Ibrahim:*** ***Ba ka sake ta ba?***

***Usman:*** ***Maganan saki bai taso ba, wani irin saki?***

***Ibrahim:*** ***Usman ka saki matarka saki uku, amma kuma har yanzu kana tare da ita, kuna zama zaman zina, kuma an ce wa]annan yara biyu na 'yan shekarun nan, }anana }ananan nan bayan saki uku ne aka haifisu.***

A wasansa mai suna Mutuwar Zuciya" a fitowa na farko an fara ne da hannunka mai sanda ga irin halayya da tunanin da matan 'yan siyasa ke yi a dukk lokacin da mazajesu suka tafi waje shuwagabannin da aka zaba a kan mulki kamar haka:

***A'isha:*** ***Ni ni wallahi na gaji, kullum za ka gidan Gwamna kuma kullum haka kake zuwa zikau haka kuma kake dawowa zikau.***

***Shafi'u:*** ***To mene ne na tashin hankali? Ke ba ki tsayawa.***

***A'isha:*** ***Haka masu zuwa ganin Gwamnan suke dawowa gida?***

***Shafi'u:*** ***To da in da nake zuwa da ya wuce nan wurin ne eye?***

| | |
|---|---|
| ***A'isha:*** | ***To ni banga zahiri ba!*** |
| ***Shafi'u:*** | ***Banga… ban gane abin da kike nufi ba!*** |
| ***A'isha:*** | ***Au ba ka gane ba?*** |
| ***Shafi'u :*** | ***Ey…*** |
| ***A'isha:*** | ***To za ka gane ba na ce da kai ne daga yanzu duk lokacin da ka je gidan Gwamna ka dawo da leda da nauyi ba maganar ke nan.*** |
| ***Shafi'u :*** | ***To nauyin da da nake ba ki kina nufin daga ina nake samo su ba daga gidan Gwamna ba. Ni fa ba ni son tashin hankali ey…He ban son irin abubuwan da ki ke mani ba na so, na gaya maki ey hey. Idan ina harkana ba na so mutum ya sa man ido. Yanzu inda kuma nike neman ku]in nan ban son mutum na sa min ido abubuwan da nakeyi.*** |
| ***A'isha:*** | ***To shi kenan na daina sa ma ido na shirya sai mu tafi tare.*** |
| ***Shafi'u:*** | ***Ina?*** |
| ***A'isha :*** | ***Na ce tare za mu tafi*** |
| ***Shafi'u:*** | ***Ai ba mahaukaci ba ne ni, kin taba ganin an ]auki mace an je wurin Gwamna da ita?*** |
| ***A'isha:*** | ***Na ce tare za mu tafi da kai.*** |
| ***Shafi'u :*** | ***Na ce ina za mu da ke ?*** |
| ***A'isha :*** | ***Gidan Gwamna in gani idan Gwamna yana ba ka in gani idan ma baya ba ka ma in gani, idan kuma kaucewa kake yi kana wani wuri da shi to ka ga duk zargin da na ke maka ya kauce. Ko ba haka ba?*** |
| ***Shafi'u :*** | ***Au Abin ya zama 'yar }ure ne, rainin har ya kai nan ? To wallahi karya ki ke yi.*** |
| ***A'isha :*** | ***To }afarka }afata.*** |

| | |
|---|---|
| ***Shafi'u :*** | ***A'a haba A'isha, yanzu saboda Allah meye naki na haka?*** |
| ***A'isha:*** | ***(Dariya) yauwa-yauwa. Ai wallahi kai mai gidan wani lokaci idan ba na ]an bu]e wuta ba, ba ma daidaitawa.*** |
| ***Shafi'u :*** | ***Amma kuma kar ki zarce, ba a zarcewa ki kwantar da hankalinki, can muke ta abubuwanmu, ko ba gaskiya ba, kuma ai al'amarinku na mata ku dai ku zauna a gida ku yi ta yi mana addu'a kawai in za mu fita sai ku ce Allah ya ba da sa'a. Ey, kar ki damu, maganan da na fa]a ita ce. Yauwa!*** |
| ***A'isha:*** | ***Yau cefane na mai lafiya za ka kawo mun.*** |
| ***Shafi'u :*** | ***E, in Allah ya yarda.*** |
| ***A'isha:*** | ***To a dawo lafiya.*** |

### 4.2.0 Ma'anar Jigo

Don ganin irin gudummuwar da masana suka ba da wajen bayyana ma'anar jigo. Kamar yadda masana adabin Hausa suka yi bayani ma'anar jigo. A cikinsu akwai 'Yar aduwa (2007:43), ya ce "jigo kalma ce da masana adabin Hausa suke yin amfani da ita da nufin "Ma}asudi" ko Manufa" ko kuma "Sa}o" da mai rubutu ke baiyana wa jama'a. Duk wani abin aka rubuta da yashafi rayuwar ]an Adam tilas ne ya kasance yana da wata manufa, Saba da kaza, wasan kwaikwayo, kowane iri ne akan shirya gudanar da shi ga jama'a da wata manufa.

A nan dai na ]an lelle}a cikin wasan kwaikwayo na Hausa sai na fahimci cewa gundarin jigogin wasannin kwaikwayon Hausa guda biyu ne rak, su ne:

- fa]akarwa
- Ilmantarwa

Sauran jigogin wasan kwaikwayo kuwa duk }anana ne da suke }ar}ashin wa]annan biyun, kamar su jigon soyayya dagarga]i da nasiha duk suna }ar}ashin fa]akarwa ne." 'Yar aduwa (2007:43), ya ci gaba da bayaninsa a kan jigon wasannin kwaikwayon Hausa kamar haka; "idan muka tsaya tsaf muka dubi wasannin kwaikwayon Hausa,sai mug a cewa ana shirya su ne don jawo hankalin jama'a ga wasu abubuwan rayuwa da suka da]e da sani, sai dai suka shagala, suka shantake, tare da gafala ga aikata su,ko kuma suke yi masu ri}on sakainar-kashi, a kan haka ne ake shirya wasan kwaikwayo don a yi masu nuni a kuma tunatar da su a kan wannan sakaci dasuke yi don su dawo su rungumi abinsu; wannan shi ne nufi da ***fa]akarwa****"*.

Dangane da wannan ne binciken an ]auki wasu daga cikin wasannisa a yi bayanin jigonsu, don gano irin jigon da marubucin wasan ya yi amfani da shi wajen shirya wasansa, da ya rubuta aka gabatar wa jama'a masu sauraron wasannin kwaikwayon Hausa musamman na Rediyo Tarayya Kaduna.

Don ganin yadda masana adabin wasan kwaikwayon suka ce, irin su; 'Yar aduwa (2007:42), ya ce,"Tsari a wasan kwaikwayon Hausa yana da muhimmanci matu}ar gaske, wasan kwaikwayo ya sami tsari na musamman dangane da 'yan wasa da kayan wasa da muhallin wasa (wato dandamali). A tattare da tsarin rubutaccen wasan kwaikwayo, babu labari ko mai ba da labari, sai da tankiya da hira da kuma yin nuni tare da jagora."

Bari mu dubi ire-iren jigogin da ya yi amfani da su a cikin wasanninsa da ya rubuta kuma ya yi jagoranci aka gabatar wa jama'a a kafafen gidan Rediyon Tarayya na Kaduna.

**4.2.1 Jigon "Kowa ya bar Gida…"A Wasan Duniya Budurwar Wawa.**

Ha}i}a kamar yadda sunan wasan ya nuna haka ne! kuma an gina jigon wasan ne a kan fa]akarwa, musamman ga mutanen karkara masu yawan ci-rani zuwa birane, in sun samu Arzi}i sai su manta da asalinsu kuma in sun samu zuru'a ba sa nuna masu ainihin asalinsu da }auyen da suka fito, wato ainihin karkaransu, wasan na nuni ne ga irin mutanen da sukan bar al'adinsu, su manta da }auyensu na asali, su bar zumunci da ala}a da ke tsakaninsu da 'yan uwansu, wannan wasa yana yi hannunka mai sanda ga duk wadda yake neman aure, da su binciki asalin junansu kafin a kai ga ]aurin auren.

A cikin shirin wannan wasan an yi }o}arin yin nuni da yadda mahaifan Malam Jibo da Iroro suka bar garinsu na asali suka fito daga }auyensu suka je wani garin Kaduna, suka zauna har aka haife su da }anninsu maza da mata kuma iyayensu ba su nuna masu }auyyensu ba su kuma ba wadda ya san ainihin }auyen da mahaifansu suka fito ba, har sai da maganar auren }anwarsu A'isha, ya taso. Ita kuma ta dage da cewa sai an je ainihin }auyen da iyayensu suka fito suka zo nan sannan za'a ]aura mata auren, ta kuma sha alwashin sai an gano ainihin asalinsu. Wannan shi ne, ya zaburar da sauran 'yan uwanta su Malam Jibo da Iroro har sai da suka gano asalin }auyen da iyayen da mahaifansu suka fito suka zo nan Kaduna aka haifesu. Bayan sun tambayan abokan hu]]an mahaifinsu, san nan suka fara samun labarin inda ainihin }auyen da iyayensu suka fito suka zo inda suke zaune yanzun, sannan suka je bayan sun sha wuyan neman }auyen, wannan

wasa yana nuna illar sakacin iyaye a kan rashin kulawa da asalinsu. Wato, duk yadda asalinka yake bai kamata ka koma wani gari ka manta da iyayenka da ‘yanuwan ka da dai sauran danginka kuma ka yanke zumunci da su sannan ka }i bayyana wa zuri’anka inda ka fito kamar yadda aka nuna a wasan sai da, Malam Jibo da Iroro suka tsananta bincike sannan suka samu nasara gano }auyen da danginsu su ke,  don haka ne Malam bahaushe ya ke cewa cikin Karin Magana “kowa ya bar gida ya barshi”. Tabbas wannan suna da aka sanya wa wannan wasa na “kowa ya bar gida” ya dace da irin sa}on da ake bu}ata ya isar ga mai sauraro kuma ya fa]akar da ilmantarwa da kuma nisha]antarwa.

Wannan abu ne da yake faruwa musamman a cikin al’umma nan namu a wannan lakaci sai ka ga mutum ya bar gidansu saboda wani dalili ko kuma ya tafi ci-rani a wani gari, inda ba a san shi ba, ya zauna har ya samu arziki na dukiya da ‘ya’ya kuma ba zai sanar da yaran nan nasa asalin garinsu ko kuma ya rin}a kai su, su rin}a gaisawa da sauran danginsu ba. Wannan wasan yana nuni ne da irin masu wannan hali, kuma wasan ya yi kira da jawo hankali a kan masu irin wannan hali da su bari. Irin wannan halin don ga irin illar da yin hakan ke jawowa, ko ba komai akwai ciwo da mutuwa. Kamar yadda masu iya magan kan ce “sanin asali shi ya sa kare cin alli.”

**4.2.3 Jigon “Mutum sai Allah”. A Wasan Duniya Budurwar Wawa.**

Wannan wasa an gina jigon sa ne a kan nasiha, ga jama’a masu sauraro da hannunka mai sanda ta hanyar garga]i ga masu zaman banza marasa aikin yi ko wa]anda aka sallamasu a wurin aikinsu, musamman masu yawon maula a wajen jama’a. Haka kuma a wasan akwai fa]akarwa ga

manyanmu masu halin taimaka wa jama'a don su samu wajen aiki, kamar yadda aka shirya a cikin wasan, inda A'isha ta je wajen kawunta  don ya sama wa mai gidanta Ibrahim aiki, sannan kuma wasan ya nuni da shi wadda aka samama aiki, ya kamata ya san yadda zai rike aiki da kyau wato akwai nasihohin da aka yi masa tare da garga]i ta yadda zai kula da aikin duk a cikin wasan, sannan kuma kar ya yi al'mubarzaranci da abin da yake samu na daga albashinsa da sauran alhairi da ke wajen aikin nasa,kuma ya rin}a girmama shugabanninsa, Wasan ya yi nuni da mata ta rin}a yi wa miji biyayya a kowa ne irin hali yake ciki, matu}a bai sa~awa shari'ar Allah ba. Kamar yadda wasan ya nuna A'isha ta je wajen  kawunta don ya sama wa minjinta Iroro aiki, shi kuma bayan ]aukarsa aikin, da ya fara samun albashinsa da bashin da aka bashi don gyaran gida, maimakon ya gyara gidansa sai ya }ara aure, ita kuma A'isha ba ta ~ata ranta ba,sai ta yi masa addu'a kamar yadda wasan yake nusarwa.

Wannan wasa da aka sawa suna "mutum sai Allah" ya ci sunarsa kamar yadda aka bayyana inda, A'isha ta je wajen kawunta don ya samawa mijinta Iroro aiki, kamar yadda yake a wasan; lokacin da kawanta yake ce mata "to wai kina nufin a taimaka mai da ku]i?" Ita kuma ta ce "A a ina! ai ni bana son mu zo yau mu ce a ba mu gobe, mu zo mu ce a ba mu" manufa a nan shi ne, ba wanda zai iya haka sai Allah. Sai kuma inda abokin Iroro yake masa nasiha a kan yadda zai zauna a wurin aikinsa, bayan wannan shi ma Shafi'u yana nuna kwa]ayinsa da in ya je wajen aikin da ya samu, to ya yi mashi hanya da a ]auke shi  a nan ne Iroro ya ce "Mutum sai Allah" wato tun kafin ya zauna a kan kujeran aikinsa an a fara kawo masa wani tunani.

Haka kuma a wasan lokacin da Hauwa ta zo gidan Iroro don  ta ba amaryarsa A'isha muguwar shawara a kan uwargidanta da ta san yadda za ta

yi don Iroro ya kore ta, wannan ya bayyana manufa da jigon wasan ba mai iyawa mutum sai Allah.

### 4.2.4 Jigon “Rayuwa”. A Wasan Duniya Budurwar Wawa.

Sunan wasan ya samu ne daga jigon wasan, domin yadda rayuwa yakan canza wa ]an-Adamu daga wannan matsayi ya zuwa wancan matsayi daga yanayin halin mastayisa na rayuwarsa. Rayuwan kan kai mutum ya zuwa ga wani babban matsayi na wadata ko rashin wadata ko  matsayi na mulki, shin mulkin nan na sarauta ne ko na siyasa ko na wani babban mukami ko wani matsayi da mutum zai kasance ko ya zamantowa mashahuri a fagensa ko ya zamo wani gwani a kan sana’arsa, kuma daga baya Allah ya kar~i wannan matsayi ko mu}ami, ya }as}antar da shi ya komo kamar bai ta~a ri}e wani matsayi ba ko kuma bai ta~a samun irin wannan dukiya da yake da shi ba a  wannan duniyar, wato a yanayin rayuwa da ta canza masa.

Don haka a wannan wasa mai suna rayuwa da gwanin namu ya shirya kuma ya sa ma shi suna “Rayuwa” mun ga yadda rayuwr Alhaji Shehu take da farko shi mai wadata ne wato,mai arzi}i ne  kuma mai taimakon jama’a ne, da arzi}in nasa yana cikin wannan rayuwar ce sai ya samu sauyin rayuwa samun arzi}i ba. To amma daga }arshe da ya samu karayar arziki rayuwar sai ta canza aka rasa mai taimaka masa wajen tafiyar da rayuwarsa, a wasan ne muka ga babban yaronsa da ya kafa a harkar kasuwanci, kuma ya sami arzi}i sai ya ki shi, ya gaje shi kuma yaki taimaka masa har said a jama’ar gari suka kai ga yi masa magana a kan yanda rayuwar sa take a da, da kuma yadda rayyuwar Alh. Shehu take a yanzu na rashin samun abin duniya kamar yadda yake da shi a da. Don haka kar ya manta Alhaji Shehu ne ya kafa shi, a baya har ya zama haka. Ta kar}ashin Alhaji shehu ne Allah ya yi ma Alhaji Ibrahim arzikin da yake da shi a yanzun, haka kuma wannan jigon wasan kaikwayon yana isar da sa}on a kan fa}akarwa ga jama’a a kan duk

irin halin da suka samu kansu ko matsayin da suka kai, kar su guje wa jama'a ko su butulce wa Allah(S.W.T).

### 4.2.5 Jigon "Jahilci Ciwo". A Wasan Duniya Budurwar Wawa.

Sunan wasan ya samo asali ne daga jigon wasan.A nazarin da aka yi na jigon wasan, wato; sa}on da wannan wasa ke ]auke da shi ko manufar mai shirya wannan wasan, ga jama'a ya na ]auke da babban jigo, wanda shi ne amfanin neman ilimi sai kuma }ananan jigogin da ke cikin wasan su ne i. mahimmancin tarbiya ii. Illar jahilci a zamantakewar al'umma.

Ta hanyar da mashiryin shirin wasan ya bayyana manufarsa ga jama'a, a cikin wasan shi ne, ya fa]akar da masu sauraro yanda ya kamata a yi himma da }wazo wajen neman ilimi kafin mutum ya kai ga matsayi magidanci. Don ya san ha}}o}in ubangiji game da zamanatakewarsa da iyalinsa,don gudun aikata kuskure ko sa~awa Allah. Nan ne ya nuna illar jahilci wato ta nusarwa da jama'a, irin yadda Usman ya saki matarsa A'isha har sau uku, amma suna zaune tare, kuma suna haihuwa ba tare da aure ba. Wannan a addinance bai halatta ba. Ba wani abu ya jawo wannan ba sai jahilci.kuma "jahilci ciwo ne".

A nan manufan ko sa}on da ke }unshe a cikin wasan shi ne; yana fa]akar da jama'a a kan neman ilimi, don ganin irin yadda jahilci yake kai ga mutum ga hallaka, kuma wani manufar a wannan wasa shi ne; yana nuna wa iyaye ha}}a}ansu na su ba'ya'yansu ilimi da tarbiya don su bautawa Allah ba da jahillci ba. Haka kuma manufan wasa shi ne; ya sanyawa al'umma masu sauraro da su dage wajen neman ilimi. Don da shi ke kaiga mutum da samun rayuwa mai da]i, don jahilci babban ciwo ne.

Misali daga cikin wasanni na farko inda Salamatu ta nuna wa kakansu damuwarta, a kan abin da ke faruwa tsakanin A'isha da mijinta Usman.

Salamatu: “Ba wani abu bane sai dai tsakanin A’isha da mijinta, domin tuntuni zaman banza suke yi, ya sake ta sau ]aya, ya saketa sau biyu ya saketa sau uku kuma suna tare, kuma a takaice ‘ya’ya yara biyu an haife su bayan an yi sakin”

Wannan ya bayyanar da illar jahilci, ko kuma manufar wasan da aka sama suna sai kuma inda shi Usman yake bayyana hujjarsa lokacin da yake cewa:

Usman: “Wai don kawai in raina ya ~aci sai in ce na saketa kuma in na huce in ce na dawo da ita har sau uku.”

Wannan wasa ya ci sunan da aka ra]a masa na; “Jahilci Ciwo” ne,don sa}on da ke ]auke cikinsa.

**4.2.6 Jigon “Mutuwar Zuciya”. A Wasan Duniya Budurwar Wawa.**

Kamar kowane wasan idan aka yi maganar jigon wasa ana nufin ginshi}in ko }ashin bayan sa}on da wasan kwaikwayon ke ]auke da shi. To a wannan wasan mai suna, “Mutuwar Zuciya” yana ]auke da babban jigo da }anana to amma babban jigon wasan shi ne Siyasa.

Da farkon wasan an yi }o}arin bayyana irin tunanin matan ‘yan siyasa na yanayin zamantakewar mata a cikin gidajensu da gani cewa ko da yaushe in sun je wajen za~a~~un shuwagabannin siyasa, da kuma nuni da tasirin addu’a da yanda ‘yan siyasa suka ]auki malami da matsayinsa. Haka kuma an yi hannunka mai sanda game da illar halayen ma’aikatan gidan gwamnati musamman na ‘yan siyasa. Wasan bai tsaya nan ba an gina jigon a kan shawarwari ga shuwagabannin da aka zaba kan mulki.

### 4.2.7 Kammalawa

A wannan Babin an kalli abubuwa da dama a cikinsa kamar yanda aka yi a babin da ya gabata kamar ma'anar Al'ada da Tattalin arzi}i da na Zamantakewa da ma'anar jigo duk an dubi irin gudummuwar da masana suka ba da sannan kuma aka duba zantukan da aka yi amfani da su waje rubuta wasan ko lokacin da ake aiwatar da kin wasanninsa a gidan rediyon. An gudanar da wannan biciki ne ta hannyar za}ulo su sannan aka yi masu sharhi dai-dai gwargwudo da ya kamata. Duk an yi wa]annan ne da nufin gano irin gudummuwar da marubuci ya ba da wajen buna}asar wasan kwaikwayo.

# BABI NA BIYAR: NA[EWA

## 5.0 Gabatarwa.

A wannan Babin za a yi ta}aitattaccen bayanin abubuwan da ya gudana tun daga farkon wannan aiki har ya kawo matsayin da yake, da irin abubuwan da aka gano tare da irin shawarwarin da suka kamata. Haka kuma a nan ne aka kawo ratayen wasannin kwaikwayon da ya rubuta aka yi nazarinsu a wannan kunda biciken ta fuskar Adabin Hausa. A inda aka ]auki ]aya daga cikin ginshi}an Adabin zamani aka nazarci wasu daga cikin wasannin da (Usman Baba Pategi) Samanja Mazan Fama ya rubuta, don gano irin gudunmuwarsa wajen bun}asar wasan kwaikwayo a gidan rediyo Kaduna. Haka kuma wannan Babi ya }unshi irin abubuwan da suka gudana a cikin kundin a ta}aice da irin abubuwan da aka gano wajen binciken, tare da shawarwarin abubuwan da suka dace don samun ci gaba. Sai daganan aka na]e shimfi]ar da aka yi da farkon gudanar da wannan nazarin kundin binciken. Daga karshen Babin aka kawo Ratayen wasu daga cikin za~a~~un wasannin da aka aiwatar da nazarinsu sai kuma Manazartar da wannan bincike ya dogara da su wajen samun muhimman bayanen da aka samu a cikin kundin.

## 5.1 Abubuwan da suka Gudana a Ta}aice.

Wasan kwaikwayo na ]aya da cikin rassa uku na Adabin zamani, baya ga rubutun zube da rubutacciyar wa}a. Hakika abubuwan da suka gudana a ta}aice a wannan kundin biciken mai taken "Gudunmuwar Samanja Mazan Fama Wajen Bun}asar Wasan Kwaikwayo: Nazari kan Wasu Wasanninsa. Wannan kudin bincike yana ]auke ne da Babi biyar. A Babi na farko yana }unshe da muhimman abubuwa kamar gabatarwa da irin abubuwan da ake

burin nazari a wannan kundin da dalilan gudanar da bicike da Farfajiyar da wannan bincike zai tsaya, hakanan kuma a wannan Babi ne aka yin bayanin Muhimmamcin binciken tare da hasashen binciken da tarihin wasannin kwaikwayao na gidan Rediyon Tarayya na Kaduna da tarihin marubucin wasannin kwaikwayon wato Usman Baba Pategi da aka fi sani da Samanja sai kammalawar wannan Babin na farko. Babi na biyu na wannan bincike nan ne aka yi abin da masu Karin Magana ke fa]i "*Waiwaye adon tafiya*" Wato abin nufi anan shi ne: Nan ne aka yi bayanin irin ayyukan da suka gabaci wannan aikin, musamman ta fuskar Adabi ~angaren wasan kwaikwayo, cikin ayyukan da aka nazarta sun ha]a da masu ala}a ta kusa da ta nesa da wannan kundin biciken. Hakanan kuma nan aka yi bayanin abin da masana suka ce game da Adabin wasan kwaikwayo da muhimmancinsa. Tare da hirar da tattaunawa da Samanja kuma har da da sauraron kaset-kaset na wasu daga cikin wasannin da ya rubuta aka gudanar da nazari don samun ingantattun bayanai tare da nazarin wallafaffun ayyuka da kudayen bincike da mu}alun }arawa juna sani. Babi na uku nan ne aka fito da irin gudummuwar da ya ba da cikin wasannan da aka nazarta ta fuskar Ilimi da Addini da Siyasa a inda aka za}ulo zantuka da suka shafi wannan fagage aka yi masu sharhin da ya kamata bayan an gabatar da wannan ne sai aka tsunduma cikin Babi na hu]u. Da yake ]an juma ne da ]an jummai tsakanin Babi na uku da Babi na hu]u sai aka nazarci irin gudummuwarsa ta fuskar Al'ada da Tattalin arzi}i da zamantakewa duk a cikin wasannin da aka zaba don binciken a ciki ne aka fito da dukkannin abin daya shafi wa]annan al'amurar rayuwar a wasan aka yi masu sharhi kamar yanda aka gudanar a Babi na uku tare da nazarin jigon wasannin da aka aiwatar da binciken. Daga nan sai Babi na biyar wanda yake ]auke da Na]ewar Tabarmar wannan kundin binciken da sakamakon binciken da jadawalin wasu wasannin da ya

rubuta da shawarwari da Manazarta tare da Ratayen kaset-kaset da aka saurara suka taimaka wajen cimma nasara da kuma Wasannin Kwaikwayon da aka aywatar da nazari a kan su.

## 5.2 Sakamakon Bincike:

Akwai gudummuwa da dama da marubucin wasannin ya ba da ta wajen bun}asa wasan kwaikwayo ta fuskoki da dama cikinsu akwai ta fuskar Ilimi da Addini da Siyasa da Al'ada da Zamantakewa tare da Tattalin azi}i kuma duka wa]annan suna nusartarwa ne zuwa ga tarbiyarwa a inda ya gina jigon wasu wasanninsa a kan tarbiya da fa]akarwa ha]e da nisha]antarwa a inda babbarsu shi ne ilmantarwa kamar yanda muka gani cikin nazarin wasanninsa da aka gudanar da binciken.

Haka kuma wannan bincike ya gano abubuwa kamar haka, da farko dai binciken ya gano cewa (Samanja Mazan Fama) fitaccen ]an wasa ne wanda a sanadiyar kasancewarsa fitaccen ne ya samu wannan suna da ya fi fice da shi SAMANJA. Baya ga haka kuma sai ya kasance marubucin wasan kwaikwayo ne da ake gabatarwa a kafafen ya]a labarai, musamman gidan Rediyon Tarayyar Najeriya na Kaduna da Talabijin wato N.T.A. Misalin wassanin da ya rubuta akwai na Samanja Mazan Fama da shirin Duniya Budurwar Wawa wanda ake gabatarwa a kowa ne mako sau biyu a gidan rediyon.

Haka kuma a sakamakon binciken ne aka gano cewa rubutun wasanninsa suna dacewa da yanayin zamani da ake ciki ko yanayi lokacin da ake gabatar da wasan. Sannan binciken ya gano ba ya rasa wasannin biyu da zai rubuta kafin makon ya zo. Haka kuma binciken ya gano jama'a da dama musamman masu sha'awar wasannin kwaikwayonsa suna samun ilmantawa da fa]akarwa da nisha]antarwa daga wasanninsa. Ta fuskoki da dama kamar

Tarbiyar Addini da Zamantakewa da Tattalin arzi}in }asa da Siyasa da Al'adun gargajiar Bahaushe kai har ma da sauyin Siyasar zamani dukan wa]annan daga cikin wasanninsa.

Sai dai kuma kash! duk da yake ana da fitaccen ]an wasa, kuma marubucin wasannin kwaikwayo da ake samun irin wa]annan al'amuran ci gaban rayuwar al'umma a gidan Rediyo Tarayya na Kaduna sai ya kasance ayyukansa ba a ]aukarsu da muhimmanci ba an bar su ne a wula}ance domin ba a adana su balle na baya su zo su gada. Wannan ya kasance ne a dalilin yanda hukuma ta yi wa ayyukan nasa ri}on sakainar kashi duk da irin wannan gudunmuwar da yake bayarwa ga ci gaban adabin wasan kwaikwayo ga al'umma. A hiranmu da mai gabatar da shirin wasannin da ya rubuta aka gabatar a gidan rediyon Malam Musa Ibrahim ya yi bayani cewa ba a taskance wa]annan wasannin ko a adana sabo da gaba wani lokacin ma su 'yan wasan ne suke sayen kaset ]in da za a ]auki wasansu kuma in ba su samu wani sabon kaset ba sai su goge na baya su ]auki wani sabon shirin wannan yana ]aya daga cikin abin da yake damunsu da ~angaren hukumomin da abin ya shafa, duk da ganin yanda Allah ya wadata }asarmu da makartantu da Jami'o'in da ake nazarin Harshen Hausa har ma da }asashen }etare wanda ya kamata a rin}a nazarin irin wa]annan wasannin.

## 5.3 Shawarwari

Dangane da irin sakamakon da binciken ya gano, shawara a nan da farko dai ya kamata a rin}a karfafawa masu bincike da su ri}a zakulo irin ayyukan masu muhimmanci wanda zai taimaka wa al'umma wajen ci gaba ta fuskar ilimi a rin}a adana su don ]alibai kuma ayyukan irin wa]annan a rin}a taskance su ana adana su saboda sauyin zamani don kar su bace a nan gaba musamman wa]anda ake gabatarwa a kafafen ya]a labarai don ko

yanzun da ake gudanar da wannan bincken sai  da aka yi da gaske sannan aka samu nasaran amma ba yanda rai ya so ba. Wasu wansannin da aka gabatar sun ~ace wannan ta fuskar hukumomin da abin ya shafa ke nan da masu sha'awar wasannin kwaikwayo ke nan.

Sai ta fuskar makarantu da jami'o'inmu masu nazarin Harshen Hausa ganin yanda aka sha wahala wajen nasaran wannan bincike da kuma samun irin wa]annan yana da wuya kamata ya yi a ri}a tura 'yan makaranta suna nazarin irin ayyukan irin wa]annan fitattun 'yan wasa da marubuta wasanni kwaikwayo kamar irin su Umaru Danjuma (Kasagi na Halima) da Haruna Danjuma (Mutuwa Dole) da Muhammadu (Idon Mujiya) da Ibrahim Abubakar Faskari (Iroro).

Ta ~angaren hukuma kuma sai ta taimaka masu da kayan aikin da zai sauwa}awa masu aikin da ]alibai wajen nazari da bincike musamman na'urorin zamani da zai taimaka waje tacewa da adana wa tare da }arfafa masu }warin gwuiwa da tallafawa wannan ~angare na adabin Wasan Kwaikwayon Hausa.

**5.4 Kammalawa**

A nan ne aka na]e tabarmar da aka shimfi]a tun farkon gudanar da wannan bincike na wannan kundin, sai dai ga abin da ya gudana a cikin kundin a takaice.

Wannan kundin an tsara shi ne a bisa Babi biyar. A Babi na farko, nan ne aka gabatar da shimfi]a tabarnar gudanar da wannan bincike tare da dalilan gudanar da shi da manufrar binciken tare da farfajiyar binciken da muhimmancin bincike da hasashen bincike da tarihin wasan kwaikwayon rediyo da ta}aitccen tarihin Alhaji Usman Baba Pategi (Samanja Mazan Fama) da Hanyoyin gudanar da binciken sannan da kamalawar abin da aka tattara a Babin.

Babi na biyu kuma yana tattare da ayyukan da suka gabata ne, wa]anda suka danganci adabin wasannin kwaikwayo da wanda suke da ala}a na kusa da na nesa da wannan aikin, da kuma wallafaffun litattafai, tare da kundaye da mu}alun }arawa juna sani, wa]anda suka danganci wannan bincike.

A Babi na uku nan ne aka nazarci gudummuwarsa da suka shafi rayuwar jama'a kamar Ilimi da Addini da Siyasa daga wasanninsa da aka za~o don gudanar da binciken. Sai a Babi na hu]u inda aka ci gaba daga abin da aka fara a Babi na uku inda aka dubi fuskoki da suka shafi Al'ada da Tattalin arzi}i da Zamantakewa a cikin wasannin da ake gudanar da binciken.

A Babi na biyar kuma a nan akn tattara abubuwan da suka gudana a ta}aice da irin abubuwan da aka gano wajen gudanar da binciken tare da shawarwari da suka kamata. A }arshen Babin kuma an kawo manazartar da ratayen kaset-kaset da aka saurara suka taimaka wajen gudanar da binciken da ratayen wasannin da aka nazarta tare da suka taimaka wajen samo ingantattun bayanai da ke cikin kundin.

## 5.5 Manazarta


Abbas, U.A (1994) Nason Adabin Baka cikin rubutaccen wasan kwaikwayo Kundin Digiri na Biyu, Sashen Harsunan Nigeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Abdu, S. (1985) Adabi Madubin Al'umma: Nazarin Halaiyen Hausawa ta fuskar Salihi na cikin Littafin Nagari na Kowa Kundin Digiri na Biyu, Sashen Harsunan Nigeriya, Jami'ar Bayero Kano.

Abdullahi, B.H.(2002) Gudmmuwar Gidan Radiyo da Talabijin na Jihar Kano (S.T.V.67) Wajen Ha~aka Wasan Kwaikwayon Hausa. Kundin Digiri na [aya, Sashen Harsunan Nigeriya, Jami'ar Bayaro Kano.

Abdullahi, I. (2001) Gudummuwar Wasan Kwaikwayon Hausa Wajen wayar da kan Al'umma. Kudin Digirin farko, Sashen Harsunan Nigeriya, Jami'ar bayaro Kano.

Abdullahi, M.S. (2002) Bambance-Bambancen da ke tsa kanin Wasan kwaikwayo na Hausa da Gargajiya da Fina-finan Zamani Nazari a kan Jigo Kundin Digirin farko, Sashen Harsunan Nigeriya, Jami'ar Bayero Kano.

Abdul}adir, H.M.(1998) "Rayuwa Malam Ibrahim Mandawari ta Fuskar Wasan Kwaikwayo da Yun}urin Samar da Finafi Hausa" Kudin Digiri na Farko, Sashen Harsunan Nigeriya, Jami'ar Bayaro, Kano.

Adamu,A.U. (2003), The Hausa Home Video: Media Parenting and Changing Popular Culture in Northern Nigeria (in press).

Adamu, M.T.(1997), *Asalin Hausawa da Harshensu*. [an Sarkin Kura Publishers L.T.D. Kano.

Ahmed, U.B. (1985), "Nau'o'in Wasan Kwaikwayon Hausa" Cibiyar Nazarin Al'adun Nigeriya, Jami'ar Ahmadu Bello Zariya.awa.

Ahmed, U. B. (1985), “Nau’o’in Wasan Kwaikwayon Hausa” Cibiyar Nazarin Al’adun Najeriya Ahmadu Bello, Zariya.

Ahamed, U. B (1983) *“A Taxonomy of Hausa Drama”.*

Aminu, H. (1991), Enlighment and Prapaganda as in *Wasan marafa*. Post Graduate Seminar, Departiment of Nigerian and African Laguage A.B.U. Zaria.

Bargery, G.P. (1934), Hausa *English Dictionary* And *English-Hausa Vocabulary* London Oxford University Press.

Bello A. (2008), Nazarin Salon Sarrafa Harshe a Wa}o}in Littafin Dausayin Soyayya. Kundin Digiri na Farko, Sashen Harsunan Nigeriya, Jami’ar Ahmadu Bello Zariya.

Buhari, M.(1988), “ Nazarin Jigon Wasu Littattafan {agaggun Labarai na Hausa”. Kundin Digiri na Biyu, Sashen Harsunan Nigeriya, Jami’ar Bayero, Kano.

Bunza, A.M.(2006), *Gadon Fe]e Al’ada* Tiwal Nigerial LTD.

Chamo, I.Y.(2002), “Tasirin Al’adun Turawa a cikin Fina-finan Hausa”. Kundin Digirin na [aya, Sashen Harsunan Nigeriya, Jami’ar Bayero, Kano.

[angambo, H.A. (2002), “Salon Sarrafa Jigo a Adabin Baka na Hausa: Nazari kan Jigo Fa]akarwa”, Kundin Digiri na [aya, Sashen Harsunan Nigeriya, Jami’ar Bayero, Kano.

[angambo A.(1984), *Rabe-raben Adabin Hausa da Mahimmancinsa ga Rayuwar Hausawa,* Triumph Publishing Company Kano.

[ankiri, U.R. (1982), Nazarin Wasan Kwaikwayo a Hausance Kundin Digiri na [aya, Sashen Harsunan Nigeriya, Jami’ar Bayaro Kano.

[anjuma, U.H.(1998), Salo da Sarrafa Harshe a Wasan Samanja, Kundin Digiri na [aya, Sashen Harsunan Nigeriya da Afirika, Jami'ar Ahmadu Bello Zariya.

Ewu, R.J. (1999), "The Politics of Television Drama in Nigeria, a case study of N.T.A Kaduna". Unpublished M.A. Thesis Department of English A.B.U Zaria.

Furniss, G. (1996), *Portry Pross and Pupolar culture in Hausa* University Press Plc. Ibadan, Nigeria.

Gusau,S.M. (2003), *Jagoran Nazarin Wa}ar baka*. Benchmark Publishes Limited, Kano

Gwar,E.Y. (1993), "Television Drama: Advertisement and Propaganda tendencies a case study of Samanja. Kundin Digiri na farko, Sashen Harsunan Nigeriya da Afirika, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya.

Hun}uyi, D.K.(1992), "Rayuwa daAyyukan Alhaji Usman Baba Fategi (Samanja mazan fama)" Kundin Digiri na [aya, Sashen Harsunan Nigeriya da Afirika, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya.

Ibrahim,M.S. (1982), Dangantakar Al'ada da Addini Tasirin Musumci kan rayuwar Hausawa ta Gargajiya, Kundin Digiri na Biyu, Sashen Harsunan Nigeriya da Afirika, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya.

Inuwa, U.A (2000), Tarbiya cikin Fina-finan Wasan Kwaikwayo na Hausa Kundin Digiri na Biyu, Sashen Harsunan Nigeriya, Jami'ar Bayero Kano.

Isa, S.A. (2007), Raha a wasannin {asimu Yero, Tarken wasannin Karambana kudin Digiri na Biyu, Sashen Harsunan Nigeriya da Afirika, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya.

Joe A.Y. (1984), “Hausa folk thatre and occupational groups” same examples in Zaria Kaduna State”, an Unpublished M.A Thesis English Department A.B.U Zaria.

Jummai, E.R.(1986), M.A.Theses “The Polities of Television Dramma in Nigeria a case study of N.T.A. Kaduna A.B.U. Zaria.

Kofoworola, E.O. (1978), “A Comparative Analysis of the Development of drama in Kaduna state and in Medieval and Ealy Renaissance Europe” An Unpublished M.A Thesis, English Department, A.B.U Zaria.

Kofoworola, Z.O. (1987), *Hausa Performing Arts and music*, Gaskiya Corporation Limited, Zaria.

Magaji, U. (1987) Tasirin Turanci a Rubutattun Wasannin Kwaikwayo Kundin Digiri na Farko, Sashen Harsunan Nigeriya da Afirika, Jami’ar Ahmadu Bello Zariya.

Malumfashi, A.I (1984), “The Development of Written Hausa Drama: Islam and Ajami as Factors”. A post graduate seminar, Department of Nigerian and African Languages A.B.U Zaria.

Malumfashi, I.(1990), “Madubi [aya Fuska Biyu, Nazarin da sharhi kan Rubutattun Wasannin Kwaikwayon Hausa” Takardar da aka gabatar a sashen Nazarin Harsunar Nijeriya, Jmi’ar Usman Dan Fodiyo Sakkwato.

Mansur, L. (1985), Dangantakar Suna da Hali a cikin Rubutaattun Wasannin Kwaikwayo, Kundin Digirin Farko, Sashen Harsunan Nigeriya da Afirika, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya.

Musa, H. (2004), “Yusuf Ladan da Gudummuwarsa ga Wasan Kwaikwayon Hausa”. Kundin Digiri na Farko, Sashen Harsunan Nigeriya da Afirika, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya.

Panda, I.A (1993), Mahimmancin Wasan kwaikwayo dangane da Ilimantarwa ga Al'ummar Hausawa Kundin Digiri na [aya, Sashen Harsunan Nigeriya, Jami'ar Bayero Kano.

Sa'idu,A.S. (1998) "Garga]i a Wasan Samanja" Kundin Digiri na [aya, Sashen Harsunan Nigeriya da Afrika, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya.

Saminu A. (1982), Hausa a Gidajen Rediyo da Talabijin a Nijeriya Kaduna. Kundin Digirin Farko, Sashen Harsunan Nigeriya, Jami'ar Ahmadu Bello Zariya.

Shehu, S. (2009), Hausa Popular Culture and Polical Discouse in Nigeia: Some insights into Samanja Drama on Radio Kaduna. A.B.U Zaria.

Sulaiman, A.I. (1992), Wasan Tausayi, Kundin Digiri na [aya, Sashen Harsunan Nigeriya da Afirika, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya.

Umar, M. B. (1982), Bori A Mastsayin Wasan Kwaikwayon Hausa na Gargajiya, Sashen Harsunan Nigeriya da Afirika, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya.

Umar, R.T. (2001), Tasirin Ba}in Al'adu cikin Wasannin Kwaikwayon Hausa a Zariya. Kudin Digirin farko, Sashen Harsunan Nigeriya da Afirika, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya.

Yahaya, I.Y da [angamboA. (1986), *Jagoran Nazarin Hausa* N.N.P.C Zariya.

Yahaya, M.W. (1985) Wasan Kwaikwayo a Gidan Rediyo na Kaduna. Kundin Digirin Farko, Sashen Harsunan Nigeriya da Afirika, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya.

'Yar'aduwa, T.M. (2001), Wasan Kwaikwayo: Sigoginsa da Jigoginsa" Algaita Journal of Current Research in Hausa Studies Vol.1, No.1 2002 Department of Negerian Laguages, Bayero University, Kano.

Wushishi, A.J. (1995), Adabi Hoton Rayuwar Al'umma Tsokaci a kan Nau'o'in Adabin Hausa Kundin Digiri na [aya, Sashen Harsunan Nigeriya, Jami'ar Bayero Kano.

## RATAYE NA [AYA

**Jerin Kaset da aka Saurara**

Sauraron Kaset, na Wasan Kwaikwayon "[a'a" a Wasan Samanja mazan fama da aka gabatar a gidan Rediyon tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, na Wasan Kwaikwayon "Daga }in gaskiya…" a Wasan Samanja Mazan Fama da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan "Jahilci ciwo" na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan "Kowa ya Bar Gida…" na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan Kwaikwayon "Kura da shan Bugu Gardi da amshe ku]i" a Wasan Samanja Mazan Fama da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N.).

Sauraron Kaset, Wasan "Mutum sai Allah" na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan "Mutum ba kyau" na Duniya Budurwar Wawa, aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna.

Sauraron Kaset, Wasan "Rayuwa" na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan "Sar}a}iya" na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan "Wayon Rashin Wayo" na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan "Garin neman }iba…" na Wasan Samanja Mazan Fama, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan "Bulalan Duniya" na Wasan Samanja Mazan Fama, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan "Zato Zunubi" na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan "Ai Don Kiya" (I don't care) na Wasan Samanja Mazan Fama, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan "Mutuwar Zuciya" na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan "Mu koma ga Allah" na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan “Amfanin Hankali” na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan “Rainin Hankali” na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan “Aji Tsoron Allah” na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan “Komai ya yi Zafi Maganinsa Allah” na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan “Allah gatan Kowa” na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya, Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan “An Fake da Guzuma…” na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya, Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan “Maganin Sharri…” na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan “Hakkin Allah” na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan “Kai dai ga Mutum” na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan “Allah ya Shirya” na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan “{adangaren Bakin Tulu” na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan “Mutuwa Tonon Asiri” na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya, Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan “Gani ga Wane…” na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan "Wula}anci" na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan "In Kura na Maganin Zawo" na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya, Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan "Mutuwar Zuci" na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya, Kaduna (F.R.C.N).

Sauraron Kaset, Wasan "Mu koma ga Allah" na Duniya Budurwar Wawa, da aka gabatar a gidan Rediyon Tarayya, Kaduna (F.R.C.N).

## RATAYE NA BIYU

**Wasannin da aka Gudanar da Bincike**

**(I) Wasan "Kowa ya bar Gida…"A Wasan Duniya Budurwar Wawa**

**Mutanen da ke Cikin Wasan sune:**

1. Alhaji Shehu - Shehu Namadina Paki
2. 'Yan Labai - Balarabe Ciroma.
3. Baba Sidi - Sarki Aliyu Dini
4. Yusha'u - Yusha'u Sulaiman

| | | | |
|---|---|---|---|
| 5. | Malam Jibo | - | Jibrin Yahaya Nasarawan danmahawa |
| 6. | Shafi'u | - | Shafi'u Magaji Usman |
| 7. | Isa | - | Isa Garba Jeman |
| 8. | Adodo | - | Adamu [anjuma Kinafa |
| 9. | Iroro | - | Ibrahim Abubakar Faskari |
| 10. | Baba mai tabarau | - | Usman Baba Fategi |
| 11. | Hauwa | - | Hauwa Abubakar Gamawa |
| 12. | A'isha | - | A'isha Usman |
| 13. | Salamatu | - | Salamatu Sulaiman |
| 14. | Zuwaira | - | Zuwaira [alhatu |
| 15. | Nda | - | |

**Fitowa ta [aya**

(A gidan malama jibo)

Shafi'u: Wato Yaya abin da yasa kaga na ]an nuna damuwata, ita wannan baiwar Allah. Allah ya sani ina matsanancin son ta, kuma tun ma ba ta kammala karatunta ba, na digiri.

Malam Jibo: Haka ne.

Shafi'u: Allah Ubangiji ya ha]a mu.

Malam Jibo: Haka ne.

Shafi'u: To amman tana kawo wa]ansu cikas, wanda na rasa inda ta dosa da wa]annan cikashin na lokacin auren nan namu.

Malam Jibo: Haka ne.

Shafi'u: Abin kuwa yana damu na matu}a, ba don komai ba saboda in za a yi abin nan ya dace a yi shi a kan lokaci, ba wai a yi ta ja in ja ba ko kuma ana ta kai kawo ba a yi

gaba a yi baya ba, to shi ya sanya na ce ni zan zo, akira ta ga ta ga ka, mu tsaida wannan magana shin wane lokaci ya dace mu ba yara ba ne daga ni har ita ba yara ba ne.

Malam Jibo: Haka ne

Shafi'u: Duk da cewa ba mu yi aure da wuri ba dai amma ai ba zamu ]auki kanmu a matsayin yara }anana ba.

Malam Jibo: Haka ne.

Shafi'u: To wannan shi ya sanya na.ce bari in.zo in sake yi ma magana a kira ta mu yi daddale tunda ba wani abin jin kunya cikin wannan magana, don haka kira ta gani ga ta ga ka.

Malam Jibo: Eh, kasan Ilimi in ka yi shi, ka yi aiki da shi ma wani abu ne.

Shafi'u: Eh.

Malam Jibo: Tana da nata hanzarin.

Shafi'u: To amma ai…

Malam Jibo: A'isha.

A'isha: Na'am.

Malam Jibo: Ah! Mallam Shafi'u ya zo.

A'sha: Too.

Malam Jibo: A kan maganarku.

A'isha: Eh.

Malam Jibo: Ko ba gaskiya ba.

A'isha: Haka ne.

Malam Jibo: To ban son in ji wani dogon surutu, ya mene ne bayani, ke dai ba yarinya ba ce, kin yi karatu, kwanan nan kika

gama karatun lauya ]in ki, ko ba gaskiya ba, to mene ne bayani yanzu don ba na son…

Shafi'u: Batun lokacin ne fa, ai duk wani matsala bai wuce lokacin auren mu ba

Malam Jibo: To lokacin ai mu ba za mu ]auke ta mu cusa ta gidan miji ba?

Shafi'u: Eh.

Malam Jibo: Tunda ta yi karatu, ta san abin da take yi ita ma ya kamata ta za~i lokacin da take so, ko kuma ya take so ayi abubuwan don mu ji daga bakinta.

Shafi'u: Eh.

A'isha: To yaya ni ba wai batun aure ne yanzu a gabana ba, ba kuma wai don bana son auren ba ne.

Malam Jibo: Uhum.

A'isha: To amma bayani shi ne, ni ina son in san asalin zuri'anmu a yi auren a can to a tafi can tushen maganin a je a yi a wurin ma'ana a tafi can inda iyayen namu suka fito a je a gabansu, musan inda suke su san mu ma kuma muna nan shi ne bayani.

Shafi'u: Yaya Jibrin, yanzu ke A'isha wa]annan ba yayyin ki ba ne, me ye ba za su iya ba a nan ai wannan sabon aiki ne?

A'isha: A'a kaga Shafi'u tsaya ka bini a hankali ba wai wani Maganan abin da za a kasa yi ba ne a nan ni dai bayanina Shi ne ka bini mu tafi mu nemo ainihin inda mahaifana suke Shi ne bayani, don duk abinda za'ayi indai maganar aure ne to can fa za a yi shi.

| | |
|---|---|
| Shafi'u: | Kai kin ]ebo aiki gaskiya, wannan aiki kuma waya san lokacin da za'a gama wannan binciken? |
| Malam Jibo: | To ita rayuwa ai sai a hankali malam Shafi'u. |
| A'isha: | To tunda kace na ]ebo aiki idan ba zamu je mu nemosu ba, maganar aure a barshi, sanda Allah ya kawo wanda zamu je mu nemo ainihin iyayen mu shikenan sai a yi da shi falillahil hamdu. |
| Shafi'u: | A'a ba za a bar shi ba a je a bincika. |
| A'isha: | To ni yanzu nasan abinda yake dubawa, yana duba maganar ku]i ne, ban ce ne ni ban ce ina son sisi na shi ba. |
| Malam Jibo: | Haka ne. |
| A'isha: | Ni zan ]auki nauyin tafiyarmu da dawowarmu da duk abin da za a kashe ni na ]auki nauyi. |
| Malam Jibo: | Eh haka ne, haka ne, to shi ke nan A'isha ah ki saurare mu, ki saurare ni eh. |
| A'isha: | Amma maganar tafiya ai ba fashi. |
| Malam Jibo: | Kana ji abin da nake so in fa]a maka to ka ga sha'anin ilimi kenan. |
| Shafi'u: | Eh! |
| Malam Jibo: | Shi yasa ka ji na ce bari in bita a hankali, ka ga maganar nan da yarinyar nan ta yi ni na ji kunya, da girmana da komaina na kasa wannan tunanin ka ga ta yi! |
| Shafi'u: | To yayan ku fa]a wa,babban yayanku. |
| Malam Jibo: | Yanzun zan ]auke ka ne mu je wajen shi ai ko kuma ni zan tafi wurinshi don in shaida masa. |
| Shafi'u: | Ai ni ba sai na je ba. |

Malam Jibo: In ina kan hanya ne inda yarinyar ta tsaya ne kuma na ji kunya a gabanka da ta da]a wanan maganar ta gaskiya.

Shafi'u: Maganar da ya kamata ku yi ta yi.

Malam Jibo: Ta yi shi to Al'amarin ilimi kenan.

Shafi'u: Don Allah a sanar da ni ko ta hanyar waya ne.

Malam Jibo: To bari in je in same shi.

## Fitowa ta Biyu

A gidan Iroro

Malam Jibo: Salamu alaikum.

Iroro: Wa'alai kumussalam, Malam jibo.

Malam Jibo: Yaya!

Iroro: Barka dai (gaisuwa)

Malam Jibo: Yauwa, wata magana ce take tafe da ni.

Iroro: To!

Malam Jibo: A gurguje.

Iroro: To!

Malam Jibo: Shafi'u kai

Iroro: Oho! Shafi'u

Malam Jibo: Shi ne ya zo a kan maganar A'isha ya zo tuni sai A'isha ta fan]are, ta ce ita ba za ta yarda ai wannan abu ba ka fahimce ni.

Iroro: Eh.

Malam Jibo: Sai ta san asalinmu, shin iyayen mu daga wani }auye suke, ba ta son a yi komai a bariki.

Iroro: Baka gaya mata daga bisa hadari aka jefomu ba! ai sai ka gaya mata daga sama muke, in har sai ta san asalinmu za

| | |
|---|---|
| | ta tsaya ta yi mana wannan dogon binciken, ko daga daji muka fito? |
| Malam Jibo: | To amma yaya in ka duba, yarinyar nan fa ta yi magana na ilimi, ta ce ita wannan }auyen, tana so tasan ainihin }auyenmu, idan aka nemo }auyen, anan za a yi biki, anan za a yi komai ala bashi duk inda za a zauna a je a zauna, Shi ne nace to ai ni ma ina da wa bari in zo in sameka! |
| Iroro: | A'isha ta ]ebo aiki subuhanalillahi kai ni da ina jinka maganar ku]i na? |
| Nda: | Me na gaya maka Alhaji Wallahi yanzu ba ni da ku]i ba ni da ma hanyar da zan samo wa]annan ku]in yanzu. |
| Iroro: | Amman ya muka yi da kai da, cewa ka yi yau za ka kawo mini ku]in nan. |
| Nda: | To na je na nema ban samu ba, wanda na ke son in je wurinshi da naje sai na samu kukan da ya ke mini yafi nawa saba da haka nake son ka taimaka mini kwanan nan insha Allahu idan na samu zan kawo maka. |
| Iroro: | To wai yaushe zaka kawo mini ku]i na? |
| Nda: | To yanzu dai ba ni da abin da zan ]auka in siyar balle in ce ga randa zan kawo maka. |
| Iroro: | Amma kana da }arfin da zaka iya zama gidan yari a kan wannan ku]i ko ba gaskiya ba, shi tasa duk wata hur]a ba na son in yi ta da Banife! |
| Nda: | Haka ne. |
| Iroro: | Wallahi duk hul]a ban a so in yi ta da Banufe. |

| | |
|---|---|
| Nda: | Haka ne! ai Banufe zai gaya maka gaskiya ba zai maka dungu ba, amma abin da nake so yanzu ka ba ni kamar wata uku insha Allahu idan na samo zan kawo maka shi. |
| Iroro: | Ni gaskiya ba zan baka wata uku ba Nda zan dai iya baka sati uku ka kawo mini ku]ina, idan baka kawo mini ku]ina ba ni kuma za ka ganni gidanka da 'yan sanda na dai gaya maka gaskiya! |
| Nda: | To Allah ya taimakemu, Allah ya kaimu lokacin. |
| Iroro: | Amin don nabiyyu rahamati. |
| Malam Jibo: | Allah ya baka yadda za ka yi! |
| Nda: | To sai anjima. |
| Malam Jibo: | To ka ji bayani dai? |
| Iroro: | Tabas! |
| Malam Jibo: | Ni ma sai na ji kunya a gaban Shafi'u ]in tun da ina babba yarinya ta yi wannan tunanin. |
| Iroro: | (kira) Isa |
| Isa: | Na'am! |
| Iroro: | Don Allah zo, don Allah akwai wani dattijo anan garin baba sidi kana da labarinsa. |
| Isa: | Eh baba Sidi yana nan. |
| Iroro: | Yana da rai? |
| Isa: | Yana da rai. |
| Iroro: | Shin ina yake da zama ne baba Sidin. |
| Isa: | Ai yanzu baba Sidi ya daina zirga-zirga duk inda ka sani yana zuwa yanzu ya daina. |
| Iroro: | Allahu akbar. |

| | |
|---|---|
| Isa: | Yanzu sai dai a share }ofar gida a fito da kujera ta, ta gwado ya zauna a }ofar gida yana shan iska sannan jikan yana yi masa tausar matsa. |
| Iroro: | Allah sarki. |
| Malam Jibo: | Allahu akbar. |
| Isa: | Kuma aminin Isa ]an Fulani ne. |
| Iroro: | Mu je don Allah ka kai mu wurin shi. |
| Isa: | To mu je. |
| Iroro: | Domin wannan yarinyar ce A'isha ta jawo mana fitina, aurenta ya tashi ta ce ita ba za ta yarda ta yi auren nan ba, sai an je asalin tushenmu nan za a yi auren. |
| Isa: | To ba aminin mahaifinta ba ne. |
| Iroro: | To Shi ne na ce ai mu je. |
| Isa: | Mu je. |

**Fitowa ta Uku**

| | |
|---|---|
| Usman: | Kaka-kaka! |
| Baba Sidi: | Malam Shehu. |
| Usman: | Ni fa matse-matsen ya fara isata. |
| Baba Sidi: | Yanzu kaga tun lokacin Ubanka yana da rai wajen shekarar shi casa'in kulum shi yana tare da ni amma yanzu gaka jika, kana kwashe daula kullum kana samun tarihi da labari kana mammatsa mini }afa kullum na fito shan iska, shi yasa kake }aru wa da labarin duniya! |
| Usman: | To aini wannan matse-matsen wai yanzu wannan fata da ta yi tauri yanzu aka sa reza aka yanka jini zai fito kuwa? |
| Baba Sidi: | Kai ko ka fara kenan, ta]i da jika sai ka ce almara! |

| | |
|---|---|
| Usman: | Kaka ka da]e gaskiya. |
| Baba Sidi: | To ai kaga sauran jikoki sukan matso nan na kanga wani lokaci kai ne kafi dama-dama da ni. |
| Usman: | To ni ai labari nake so inji tarihi, an ce, :Kunne ya girmi kaka. |
| Baba Sidi: | Kana ko samu insha Allahu. |
| Isa: | Salamu alaikum. |
| Usman: | Wa'alaukumussalam. |
| Isa: | Jika jika. |
| Usman: | Na'am ina tare da kakan nawa ai ni da na dawo aiki ina nan. |
| Isa: | Baba Sidi. |
| Baba Sidi: | Na'am mane ne? Malam Shehu mene ne? |
| Isa: | Ba}i ne ka yi ga su nan ga wannan ga wannan ba}i ne tafe da su Isa. |
| Baba Sidi: | To daga ina ne haka? |
| Isa: | Wato su dai suna so su san inda babban aminin nan naka yake wanda kuke safara da shi tare. |
| Baba Sidi: | Wanda muke zuwa gwanja da muna harkan goro? |
| Isa: | Yauwa-yauwa to sun zo su ji cikakken bayani inda yake a wurinka. |
| Baba Sidi: | To wane a cikin su ne? |
| Iroro: | Mallam mai Sammatsi. |
| Baba Sidi: | Ok mallam mai Sammatsi? |
| Malam Jibo: | Eh. |
| Baba Sidi: | Wane ne ]anshi a cikinku? |
| Malam Jibo: | Ga mu nan. |

Baba Sidi: Dukkan ku 'ya'yan shi ne masu neman albarka? To shi wannan malam.

Isa: Da Jibo da Iroro.

Baba Sidi: Da Jibo da Iroro, shi ko na san yana wani tsohon gari ne, can wani gari wai shi dajin bauta!

Isa: Ni fa na barku lafiya fa!

M.Jibo: To madallah.

Baba Sidi: Shi wannan dajin bauta da Allah ya yi mishi arzi}i sai ya koma can yake zauna yana safara can ya yi gida ya yi komai abin da na sani kenan.

Iroro: Dajin bauta?

Baba Sidi: Dajin bauta, yana can nesa wurin yana da nisa in an fara tafiya daga nan yana da nisa!

Iroro: To yanzu Baba Sidi ina ne za mu je mu }ara samun cikakken bayani.

Baba Sidi: To!

Usman: Ku bi shi a hankali wannan fa Dattijon ba ya mantuwa.

Baba Sidi: Yanzu wannan gari in kuka je ku yi tambaya akwai wani tsaran cikinmu da shi ma shi ma goron yake tafiya yake sayarwa a gwanja ]in nan ana ce da shi Sarkin goro sunan shi.

Iroro: Sarkin goro ko?

Baba Sidi: Mun riga mun saba muna jigila shi ma ya koma yana cin kasuwar shi.

Iroro: Shi Sarkin goron yana nan da rai?

Baba Sidi: Da jikokin a gabanshi da 'ya'ya, yana da rai Insha Allahu.

| | |
|---|---|
| Iroro: | To mun gode Baba. |
| Baba Sidi: | To madallah shikenan Allah ya baku sa a. |
| Malam Jibo: | Don Allah jika ga ]an wani abu dai a sai mai goro. |
| Usman: | Wannan sun ba ni sun ce a sai maka goro |
| Baba Sidi: | To ba laifi kai wa]annan ba}i Allah ya ba mu lafiya. |
| Usman: | Baba. |
| Baba Sidi: | Na'am! |
| Usman: | Kaga jiya na sai maka kwai ka ce yana ]aci. |
| Baba Sidi: | Yana ]aci. |
| Usman: | To saboda Allah kaka ka zauna daga fura sai goroshi kenan abincinka? |
| Baba Sidi: | Ai furan nan da in ba tsami asa tsamiya ta yi tsamin nan ina jin da]inta. |
| Usman: | To shikenan ni ina ganin na yi maka, wai ka ]an ji da]i ne. |
| Baba Sidi: | A'a ai tsami-tsamin nan shi yake sawa nake jin da]i. |
| Usman: | To shikenan za a kawo furar za a kawo. |

**Fitowa ta Hu]u**

| | |
|---|---|
| Malam Shehu: | Yusha'u! |
| Yusha'u: | Na'am kaka! |
| Malam Shehu: | {warya nawa ka }irga a goron nan. |
| Yusha'u: | {warya takwas ne na }irga a ciki. |
| Malam Shehu: | Ina tsintar. |
| Yusha'u: | Ga ta can gefe. |
| Malam Shehu: | Ina kuma hannun ruwar. |
| Yusha'u: | Duk suna na gefe guda. |

Malam Shehu: Ina kasa hannun ruwa.

Yusha'u: Hannun ruwar ne, Adamu ya ]auke.

Malam Shehu: Bana son sakarci irin wannan, zan maka duka, koda bana iya tashi zan sa }afa in make ka.

Yusha'u: To kai Kaka mai yasa kake haka?

Malam Shehu: (kira) Adodo, ina Adodo?

Adodo: Yusha'u don Allah bashi ya je a kwance ba, kaka kai kace a kwance ba?.

Malam Shehu: To a ]aure na fasa, ba za a siyar da shi ba a wannan kasuwar.

Yusha'u: To yanzu kaka wannan goron da kace a baiwa wancan mutumin gashi nan har yanzu bai zo ya ]auka ba.

Malam Shehu: Kar ya zo ya ]auka, goron wane ne lokacin da nake zuwa gwanja, na je gwanja na sayo, na je Agege da }afa nake tafiya kun san lokacin dana wahala na samu arzi}ina da kaina?

Adodo: Yanzu in koma in ci gaba da buhun a sama ko?

Yusha'u: Amma wallahi Kaka tsufanka da masifa ne!

Adodo: Wallahi kuwa, Allah wallahi ni irin wannan tsufa naka.

Malam Shehu: To ai naga za ku fini masifar an saku abu kun kasa.

Adodo: To ka ce mu yi wannan muna yin wannan kuma ka ce wannan so kake mu raba kan mu goma?

Yusha'u: Ji mana Adodo, yanzu wannan da ba don imani ba, ba sai mu tafi mu }yale maka kayan ka ba, muga wanda zai yi maka.

Malam Shehu: Gara in ]auko lebira inda zan sa }afa in daki mutum ku]ina suyi aiki.

| | |
|---|---|
| Yusha'u: | Kai da baka iya tashi Ado, ka ji fa mutumin da baya iya tashi shi ne wai yake irin wannan maganar. |
| Malam Shehu: | Na yi wa yaro baki ko, in na yi wa yaro baki kuma fa? |
| Yusha'u: | To yanzu me ka ke so a yi? |
| Iroro: | Salamu Alaikum. |
| Yusha'u: | Wa'alaikumunsalam. |
| Iroro: | (Gaisuwa) |
| Malam Shehu: | Za ku ba su goron nawa ne, za ku ba su goron nawa ne? |
| Yusha'u: | Tsaya mana Kaka. |
| Iroro: | Muna tambayar sarkin goro ne. |
| Yusha'u: | Ai Kakan mune ga shi nan. |
| Adodo: | Wannan tsohon ba. |
| Yusha'u: | Kaka ka yi ba}i ne. |
| Malam Shehu: | Na'am. |
| Yusha'u: | Ka yi ba}i ne. |
| Malam Shehu: | Bana siyar wa ba ne goron. |
| Adodo: | A'a ba goro suka zo siya ba Kaka. |
| Malam Shehu: | Me suka zo yi? |
| Adodo: | Ba}i ne sun zo wajen ka ne daga wani gari. |
| Yusha'u: | Ku yi ha}uri shi haka yake ku yi ha}uri don Allah. |
| Malam Shehu: | Me ya kawo ku? |
| Iroro: | Wato mu ]iya ne na Malam mai Sammatsi. |
| Malam Shehu: | To! To! To! Allah Sarki. |
| Iroro: | To muna tambaya ainihin inda yake a kai mana kwatance da wani dattijo Baba Sidi can cikin gari. |
| Malam Shehu: | To to duk tare muka taso da su. |

Iroro: Muka je wurin Baba Sidi shi ne ya ce mana lallai idan mun zo nan kasuwa mu tambayi Sarkin goro.

Malam Shehu: Eh gani.

Iroro: Me yuwa kai zaka san asalin tushe mu?

Malam Shehu: Ah! Ah! Ha! na sani, Allah sarki shi gidan kuke nema?

Iroro: Eh.

Malam Jibo: Mu ‘ya’yansa ne.

Malam Shehu: To ai sun koma Kirgi, yanzun nan za a tarar da shi a Kirgi!

Iroro: An shiga uku.

Malam Shehu: Kirgi sunan garin kenan!

Iroro: Mun shigo Kirgi kam.

Malam Shehu: Da sunan garin Dajin Bauta, gwamnati tasa katafila aka kwashe garin ta yi madatsar ruwa, dab da }ofar gida shi kuwa nanaka shuka darbejiya duk gurin darbejiya ne.

Malam Jibo: Yanzu sai mun je Kirgi kenan?

Iroro: To in mun je Kirgi wa za mu tambaya?

Malam Shehu: Kafin kuje ma sai an goya ku a gungura, keke ba zai je can ba, ko jaki to sai ku tambayi ina Malam Balarabe.

Iroro: Malam Balarabe.

Malam Shehu: To sai ku sadu da shi amma ya tsufa.

Iroro: Shi Mallam Balaraben?

Malam Shehu: Eh.

Malam Jibo: To Alhamdulillahi.

Iroro: Ya dangantakar ku take a wurin Babanmu.

Malam Shehu: Ni {aninshi ne kamar mu yi bu]e a wurin sansa.

Iroro: Mun gode! Mun gode!! (Suka yi Sallama).

Yusha'u: Wannan, wannan tsohon kayi musu bayanin abin dake akwai.

Malam Shehu: Waye zai sayi goro.

Yusha'u: Kaka, Kaka don Allah ka ri}a magana ta fahimta ga mutane me yasa kake haka nan ne?

Malam Shehu: Ba makwabta ba duk garin a jini, haka nake kuma Allah ya yi mini arzi}i.

Adodo: Kaka wannan jaka hamsin ]in bari in in ajiye ta a gida.

Yusha'u: Eh ka ajiye ta a gida.

Malam Shehu: Ajiye mini ita a gaba na in ganta.

Yusha'u: Ba tana hannun sa ba?

Malam Shehu: Duk kuna yi mini sata.

Yusha'u: Mu zamu je mu ci gaba da aiki

Malam Shehu: To ku koma ku ci gaba da aiki.

## Fitowa ta Biyar

(A garin Kirgi)

Safiya: (Tari) Yaya

Iroro: Sannunku dai

Zuwaira: Marabanku (gaisuwa)

Iroro: Don Allah nan ne Kirgi

Zuwaira: Eh, ba ku iso garin ba mu zamu je ]iban ruwa ne amma ba ku shigo garin ba.

Iroro: Nan ne ko Allah sarki.

Zuwaira: Amman Kirgin kenan?

Iroro: Don Allah muna tambayar wani Dattijo ne Mallam Balarabe.

| | |
|---|---|
| Safiya: | Eh na san shi. |
| Malam Jibo: | Kin san shi ko? |
| Safiya: | Eh Balarabe Allah gatan bawa ko, eh na san shi na san shi sosai! |
| Iroro: | Allah Sarki. |
| Safiya: | Shi ne shi ne dai... |
| Zuwaira: | Daga ina kuke? |
| Iroro: | Daga nesa muke, mu ba}i ne. |
| Zuwaira: | Ku yi mini bayani mana |
| Iroro: | Bayani shi muke son gani |
| Safiya: | Sun ce gidan shi zasu ko ke ki wuce ]ebo ruwan ni in je in kai su. |
| Zuwaira: | Ke dai wannan bokitin yafi }arfina ki bani inje in kaisu. |
| Safiya: | To inda mun tafi taren ke dai ki tafi ni inje in kaisu. |
| Zuwaira: | To ba ke zaki ]ora ni ba? |
| Safiya: | To ai zan dawo, in na raka su sai in dawo ko? Kai ku taho inje in kaiku kun ji. |

**Fitowa ta Shida**

| | |
|---|---|
| Safiya: | Ke ke yarinya ke Salamatu. |
| Salamatu: | Na'am! |
| Safiya: | Zo. |
| Salamatu: | To, sannunku. |
| Malam Jibo: | Yauwa. |
| Safiya: | Don Allah wa]annan baki zasu gidan ku ne. |
| Salamatu: | To, sannun ku da zuwa. |

| | |
|---|---|
| Safiya: | Ba}in Balarabe ne, kunga ga jikarshi nan. |
| Safiya: | Ni zan koma saboda kuna jin yaya tana mitar ]auko ruwa. Ki kaisu wurin Balarabe. |
| Salamatu: | Sai anjima. |
| Iroro: | To mun gode. |
| Safiya: | To ai kun zo gida. |
| Salamatu: | Salamu alaikum. |
| Dattijo: | Wa alaikumssalam. |
| Salamatu: | Maigidan ga ba}i ka yi. |
| Dattijo: | To daga ina? |
| Salamatu: | Nima ban sani ba. |
| Dattijo: | Sannun ku da zuwa, sannun ku yara. |
| Malam Jibo: | Yauwa. |
| Dattijo: | Marabanku, kun zo lafiya (gaisuwa). |
| Iroro: | Wato daga nesa muke Baba. |
| Dattijo | To. |
| Iroro: | Ainihin mu ]iyan marigayi Malam mai Sammatsi ne. |
| Dattijo: | Allahu akbar. |
| Iroro: | Yarinya }anwarmu ta tashi za ta yi Aure ta ce ita Allanbaran ba za a yi auren nan ba sai ta san asalin ainihin inda muka fito aka yi mana kwatanci da wani bawan Allah Baba Sidi muka je wajen Baba Sidi muka yi masa bayani, ya ce eh gaskiya sai dai mun je wajen kasuwa mu tambayi Sarikin goro. |
| Dattijo: | Eh haka. |
| Iroro: | Muka je kasuwa muka tambayi Sarkin goro Shi ne yayi mana cikakken bayani, ya ce da ainihin can dajin bauta |

aka ce babanmu daga dajin bauta ya fito, aka ce yanzu dajin bautar an tashi shi ne ya ce lallai idan mun zo nan mu tambayi Baba Balarabe kana nan da ranka zamu samu cikakken bayani eh.

Dattijo: To Alhamdulillahi to kanga.

Iroro: Eh.

Dattijo: Kun zo gida, nan da kuke gani nan ne gidan ku.

Malam Jibo: Nan.

Dattijo: Nan ne zuri'ar ku kuka tashi, kun sani mu a duniyar nan mu masu yawo ne ba garin da ba mu a duniyar nan.

Malam Jibo: Ku su wane ne?

Dattijo: Mu kanawa.

Dattijo: Na sha gaya mishi inda suka tafi su ce mu mutanen wuri kaza ne kaga yanzu ba don yarinyar nan tayi }o}ari ba da an wahala ai nan ne tushen ku.

Malam Jibo: Ko!

Dattijo: Inda duk ba Kano muka je na kan ce ku fa]i ku ga wurin ku, ga kaza sannan kuma kuji wani abin mamaki a }asar Kano nine Sarkin wannan garin ga bayan gida nan shi ne ainihin gidan mahaifinmu kenan, shi yayi sarautar da bashi ne na hau amma nan ne gidanku ku kanku 'ya'yan sarauta ne.

Malam Jibo: Yanzu Baba kai }anin shi ne uwa ]aya uba ]aya.

Dattijo: Uwa ]aya uba ]aya muke da shi.

Malam Jibo: To Alhamdulillahi.

Dattijo: Amma kai duk inda kuka je kai Allah shi yi muku albarka kai da ku yarda ku ri}a ~oye sunan nan muna da

wani al'ada namu mara kyau, inda muka je sai mu yi shekaru, mu yi haife-haife mu yi arzi}i mu }i fa]in garinmu

Malam Jibo: To halim Kanawa ke nan?

Dattijo: Kuma mun bar garin nan ba mun yi laifi ne ba balle ace kar mu dawo da baya.

Iroro: Za mu je mu shiryo sai mu dawo

Dattijo: Mu asalin mu Kanawa ne.

Iroro: Allah sarki.

Malam Jibo: Kuma yarinya zamu zo maganar ]aurin auren ta!

Dattijo: To a zo a ]aura aure a nan.

Salamatu: Ikon Allah Kaka ashe 'yan uwan mu ne wa]annan kamar turawa Allah sarki!

Dattijo: Kuna da 'yan-uwa can amma sun}i fa]in sunansu sai da wata zata yi aure, ita ba za ta yarda a ]aura aurenta ba sai an gane asalinsu!

Salamatu: Allah Sarki! oh Allah Sarki!!

Dattijo: Dama un mutum shi kenan ba mai sanin asalinku.

Salamatu: Yanzu da ana samun irin wa]annan yaran ai da ka sani

Dattijo: Wallahi Alhamdulillahi! Da kowa ya san zuri'arsu.

Salamatu: To wallahi gaskiya ya kamata mutane su yi hattara.

Dattijo: {warai.

Salamatu: Duk inda kaje wallahi komai nisa ka fa]i inda kake, kuma ka nuna ma zuri'arka gida saboda mutuwa, mutuwa na nan ciwo na nan.

Dattijo: To yau ko da kufai ne gidan nan nasu yarinyar nan ni ta ci mini goro ta ce a zo don a ga kufan ]in nan aga gidansu

to kaga zuri'arsu daga nan har shekara ]ari zasu gane gidansu.

Salamatu: {warai da gaske.

Dattijo: To mu Kanawa ne su san da wannan.

Salamatu: To madallah.

**Fitowa Ta Bakwai**

Iroro: Na manta ban je wajen Baba mai tabarau ba kuma ina zuwa kullum in ]an samu ilimi, bari in zaga wurin shi tukun.

Iroro: (Sallama a gidan Baba mai tabarau) Salamu alaikum.

Baba: Amin wa'alaikumussalam.

Iroro: Baba!

Baba: Ibrahim!

Iroro: Barka dai!

Baba: Ai na aika nace in kana da lagwanin fitila nawa ya fa]a aka ce wai kaje bautan daji bautan daji.

Iroro: Dajin bauta.

Baba: Dajin bauta me ya kaika dajin bauta?

Iroro: Wato ainihin ita }annuwarmu ita ce ta tashi ta ce ba za ta yarda a yi auren nan ba sai mun je an san asalin garinmu, kaji dalili ke nan.

Baba: To! Yarinya tayi hankali.

Iroro: Shi ne muka yi ta bincike muka yi ta bincike ma kuma tayi ilimi 'yar makaranta ce eh.

Baba: Kun gano garin?

Iroro: Eh mun gano.

Baba: Ai mutum in dai kana da rai.

Iroro: Eh.

Baba: Abin da Allah ya baka ka Haifa a duniyar nan ta Allah.

Iroro: Allah Sarki.

Baba: Kabar ]iyan ]iyanka su san daga ina babansu ya fito wane ‘yan uwan baban naku.

Iroro: {warai da gaske.

Baba: Ya kamata yara su sani, ko baka da rai sun san inda ‘yan uwan babansu suke asalinsu ba zai zamar musu abin damuwa ba, su can sun gane ai ‘yan uwan babanmu asalinsu ‘yan gari kaza ne

Iroro: {warai da gaske!

Baba: Ah’ah Ibrahim ai kun yi }o}ari.

Iroro: Mun yi }o}ari?

Baba: Allah shi yi muku albarka.

Iroro: Wallahi aka ce dajin bauta daga bauta muka je Kirgi yawo fa mukai tayi fa.

Baba: Har girki.

Iroro: Kanin babanmu shi ke sarautar garin.

Baba: Allah sarki! Allah ya taya shi ri}o.

Iroro: Amin don nabiyyirrahamati.

Baba: To dai yau dai Ibrahim abin da tabarauna ya hango yau.

Iroro: Eh.

Baba: Duk mutumin da ka sani.

Iroro: Na’am.

Baba: Ko mai ku]i ne, ko mai mu}ami ne ko mai wani dai mai ]aukaka.

Iroro: Eh.

Baba: In kaga yana gudun mutum ba mai gaskiya ba ne.

Iroro: Ah! Ah!

Baba: Baka gane Hausan ba ne?

Iroro: Ni ban gane Hausan ba

Baba: Duk mai gudun mutane ba mai gaskiya ba ne.

Iroro: Wato duk mai gudun mutane ba mai gaskiya ba ne.

Baba: Ba mai gaskiya ba ne wallahi ba mai gaskiya ba ne, kana da gaskiya ba za ka guji mutane ba.

Iroro: Su zo.

Baba: Su zo.

Iroro: Eh ko a'a ne.

Baba: In dai kaji mutum yana gudu to ba mai gaskiya ba ne, ba shi da gaskiya.

Iroro: Ba mai gaskiya ba ne kenan.

Baba: Amma in kana da gaskiya ba ka gudun mutane.

Iroro: Allah Sarki.

Baba: In ku]i gareka, mene ne na gudu, ko ka bayar *yes*, ko ka bayar *No* ko eh ko a'a in wani Magana ne na ]aukaka shikenan eh a'a.

Iroro: {warai ya isa.

Baba: Amma duk mutumin da ka samu a duniyar nan yana gudun mutane to ba shi da gaskiya, Allah ba mai gaskiya ba ne.

Iroro: Allahu akbar.

Baba: Na ba ka wannan la}anin.

Iroro: Lallai ni yau na yarda da wannan la}anin.

Baba: Saboda kar ka yi mamaki idan a cikin lisafin marasa gaskiya, duk mai gaskiya wallahi baya gudun mutane son su yake yi.

Iroro: Wato in dai kana da gaskiya.

Baba: Wallahi ba za ka guji jama'a ba.

Iroro: Wato ba za ka guji jama'a ba, eh }warai ko a a.

Baba: Shikenan.

Iroro: *Yes* ko *No.*

Baba: Eh, amma da zarar ka guji mutane an kauce hanya to kada Allah yasa mu guji mutane.

Iroro: Amin don nabiyirrahamati.

Baba: Kada Allah yasa mu guji jama'a.

Iroro: Allah ya kawo mana su.

Baba: Ai baka sani ba Ibrahim.

Iroro: Eh.

Baba: Allah ya ce "Aljama'atu rahamati."

Iroro: Allahu akbar.

Baba: Jama'a su ne rahama.

Iroro: Su ne rahama.

Baba: Me zai sa ka guji mutane?

Iroro: Lallai fa sai in ba gaskiya.

Baba: Mutane fa ba gudun su ake ba neman su ake.

Iroro: To amman yanzu gudunsu ake.

Baba: Ah to, ba marasa gaskiya ba, in dai baka da gaskiya dole ka guji mutane, amman in kana da gaskiya dole ka nemi mutane.

Iroro: Dole ka nemi mutane.

Baba: {warai da gaske, ba za ka gujesu ba.

Iroro: Uhm, wato sai ka je nan a ce wane bayanan ka je nan a ce bayanan ashe kai ka }ara mini ilimi, in dai mutum na da gaskiya wallahi ba zai guji mutane ba ka zo kawai eh ko a a.

Baba: Wallahi.

Iroro: To na gode Baba na gode }warai.

Baba: Kai amma yaran nan sun kyauta mini ba ka]an ba, ai duk wanda ya bar gida dole gida ya barshi, kuma ya kamata mutane su dinga lissafi yanda kullun Allah shike da kayansa, Allah yasa mu cika da imani, Allah kuma yasa mu gama lafiya.

To jama'a a nan kuma muka kawo muku }arshen wannan wasa da muka sawa suna "**KOWA YA BAR GIDA…**" a cikin shirinmu na Duniyabudurwar Wawa

**(ii) Wasan "Mutum sai Allah". A Wasan Duniya Budurwar Wawa**

**Mutanen da ke cikin Wasan**

| | | | |
|---|---|---|---|
| 1. | Alhaji Shehu: | - | Shehu Namadina Paki. |
| 2. | 'Yan Labai: | - | Balarabe Ciroma. |
| 3. | Baba Sidi: | - | Sarki Aliyu Dini. |
| 4. | Yusha'u: | - | Yusha'u Sulaiman. |
| 5. | Malam Jibo: | - | Jibrin Yahaya Nasarawan danmahawa. |
| 6. | Shafi'u: | - | Shafi'u Magaji Usman. |
| 7. | Isa: | - | Isa Garba Jeman. |
| 8. | Adodo: | - | Adamu [anjuma Kinafa. |
| 9. | Iroro: | - | Ibrahim Abubakar Faskari. |
| 10. | Baba mai tabarau: | - | Usman Baba Fategi. |
| 11. | Hauwa: | - | Hauwa Abubakar Gamawa. |
| 12. | A'isha: | - | A'isha Usman. |
| 13. | Hajiya: | - | Salamatu Sulaiman. |
| 14. | Zuwaira: | - | Zuwaira [alhatu. |

**Fitowa ta Farko**

(A gidan kawu Shehu Namadina)

Hajiya Salamatu: Salamu alaikum.

Kawu Shehu: Wa'alaimussalam.

Hajiya: Kawu kana kusa.

Kawu: Ina kusa yanzu nake shirin ma zan fita.

Hajiya: Allah Sarki sannu.

Kawu: Sannu!

Hajiya: Ya hidimomi ya iyali?

Kawu: Alhamdulillahi, mun gode Allah.

Hajiya: To madallah, to kawu na zo wurin ka ne.

Kawu: To.

Hajiya: Kasan maigidana ba ya aiki, ba shi da aiki yanzu.

Kawu: Aha na sani.

Hajiya: Ya kuma ]an kwana biyu da rashin aikin nan.

Kawu: Allah sarki!

Hajiya: Wata rana ma haka ko ku]i makaranta da abin da zamu ba. yara ma yana son ya rika mana wuya.

Kawu: Ehm-Ehm!

Hajiya: Ga hidindamun makaranta kuma…?

Kawu: Gaskiya?

Hajiya Salamatu: Ta kan naira talatin sai a koro maka yaro a hana shi ya tsaya ya yi jarabawa.

Kawu Shehu: Haka fa.

Hajiya: To saboda haka nake so don Allah don Annabi Kawu a taimaka mashi na san kai ma duk da yake ko ina ana cin arzi}in juna ne, to kai mai jama'a ne kuma nasan insha Allah wannan abu ba zai gagare ka ba.

Kawu: To wai kina nufin a taimaka mai da ku]i ne?

Hajiya: A a.

Kawu: Maimakon ke ki ri}a kashe naki.

Hajiya: Ina! Ai ni ba na son mu zo yau mu ce a ba mu gobe mu zo mu ce a ba mu.

Kawu: Me kike bu}ata?

Hajiya: Aiki nake so a sama mishi.

Kawu: Kai! Kai!! Kai!!! Kai kin ]auko aiki.

Hajiya: To kawu ya za a yi?

Kawu: Kina neman aiki kin ]auko aiki.

Hajiya: To kawu ya za ayi?

Kawu: Da zamanin da ne.

Hajiya: Eh!

Kawu: Kama hannunsa zan yi duk ofis ]in da ana shigo wa aba wannan aiki za a ba shi.

Hajiya: Allahu Abkar!

Kawu: To amma yanzu akwai wanda suka fishi karatu.

Hajiya: Uhm.

Kawu: Suna nan ba su sami aiki ba.

Hajiya: Wallahi, haka ne gasu nan!

Kawu: To amma.

Hajiya: Sai dai ana cewa hanya tafi ku]i.

Kawu: Eh, tafin to ina da irin wannan hanyoyin.

Hajiya: To madallah.

Kawu: In Allah ya yarda zan wa mutumina magana.

Hajiya: To.

Kawu: Madallah!

Kawu: Zan je har gurinshi.

Hajiya: To.

Kawu: Bayan na yi mishi waya.

Hajiya: To.

Kawu: Don in sanar da shi ga ni nan zuwa.

Hajiya: Eh garkiya ne.

Kawu: Kin san halinsu gara su san kana zuwa.

Hajiya: Eh haka ne.

Kawu: Kar inje in tarar baya nan.

Hajiya: Allah Sarki!

Kawu: Abin duk da mu kayi za ki ji bayani.

Hajiya: To na gode!

Kawu: In Allah ya yarda.

Hajiya: A gaida su inna.

Kawu: Za su ji! Za su ji!!

Kawu: *(yana waya) Salamu alaikum! Halo Halo!! Aha aha an ce salamu alaikum, ka ce hello na ce ka ce salamu alaikum Shehu Namadina ne don Allah ina son in zo wurinka.*

*ne ina son in ganka aha'aha abin da yasa na yi maka waya don in tabbatar kana nan to shike nan sai na zo.*

**Fitowa ta Biyu**

Baba Sidi: Malam Balarabe wake maka waya haka?

Malam Balarabe: Kaji mutumi na ne Alhaji Shehu.

Baba Sidi: Shehu Namadina paki.

Malam Balarabe: Eh don Allah kaji mutumin nan bawan Allah nan tun muna 'yan }anana muke tare da shi wai zai zo waje na ne, ba zai zo kai tsaye ba wai sai ya yi mini waya tukuna.

Baba Sidi: Ai yana da amfani wai ya bincika }ila kana nan.

Malam Balarabe: To amma dai meye na waya yaushe ya ~ullo koda yaushe ya zo ai zai ganni.

Baba Sidi: Ai kaga in ya zo baka nan ya yi wahala.

Malam Balarabe: Ma yaya tambaya ta ko kana kusa ai ya san tsa kaninmu. bama rabuwa kannan tare da ni.

Baba Sidi: Ai ina ji fa?

Malam Balarabe: Yauwa!

Baba Sidi: On ni na ce insha Allahu ina ji kana ce mishi.

Malam Balarabe: Zan jirashi ya zo eh?

Baba Sidi: Insha Allahu!

**Fitowa ta Uku**

(A Ofishin Malam Balarabe)

Shehu: Salamu alaikum.

Malam Balarabe: Wa'alaikumssalam kaga fakat ]an hala} haba Alhaji Shehu?

Shehu: Abin dake tafe da ni!

Malam Balarabe: Tsakaninmu da kai sai ka yi waya, an gaya maka ka zo kai tsaye mana.

Shehu: Uhm abin da yasa nake yin waya ]innan don in tabbatar da inda kake.

Malam Balarabe: Eh to kuma haka ne!

Kawu: Idan ban yi wayar ba ku]in da zan kasha sai ya ninka na wayar ko na ma ]ari ban kuma same ka ba.

Malam Balarabe: Ya yiwu ka zo bana nan.

Kawu: Abin dake tafe dani wato 'yata yar wana.

Malam Balarabe: To naji.

Kawu: Ka gane ta wacce kuka gaisa, ta ce zata zo wajen kawu ka ce waye kawu ta ce da kai Shehu to ita.

Malam Balarabe: To na gane na gane ta eh.

Kawu: To mijinta a wani lokaci ma ‘ya’yan nata ku]in makaranta ma koro su ake yi daga makaranta a kan naira talatin.

Malam Balarabe: Haka yake!

Kawu: To shi ne nake son don Allah a sama mishi aiki don na san abin da yasa na zo wurinka.

Malam Balarabe: {warai da gaske , ah! }warai da gaske ai na gaya maka mai za ka nema in Allah ya yarda a rasa samu, kai ah! Yusha’u!

Yusha’u: *Yes Sir*, ranka ya da]e *sir!*

Malam Balarabe: Barka, sannu!

Yusha’u: Yauwa sannu, ina gajiya *sir*.

Malam Balarabe: Don Allah je ka ka ]auko mini fayil na ma’akata nan, ka ]auko shi maza da sauri.

Yusha’u: To *Sir*.

Malam Balarabe: Haba Alhaji Shehu, wannan abu mai sau}i insha Allahu.

Kawu: Ai ka san abin ne masu neman aiki Allah ya yi yawa da su ne.

Yusha’u: Gashi ranka ya da]e

Malam Balarabe: Waye sunan yaron?

Kawu: Ibrahim.

Malam Balarabe: Ibrahim ko, ai shi kenan.

Kawu: Amma a kan masa la}ani da Iroro chaba-chaba gara a sa la}ani kar a je a ba wani.

Malam Balarabe: Ka je maza ka cika a zo a abinnan.

Yusha’u: Za a ba shi *Appointment letter* ne ko kuwa?

Malam Balarabe: Eh! A ba shi kai tsaye zai zo da takardunsa gobe da safe za a ba shi insha Allahu.

Kawu: Alhamdulillahi! Na gode madallah.

**Fitowa ta Hu]u**

(A gidan Iroro)

Hajiya: Uhm-Uhm-Uhm, Allah mun gode maka, ina mai gidan, ah-ah-ah na dawo daga gidan kawo ka zaga ne?

Iroro: Kawu Shehu!

Hajiya: Eh!

Iroro: Allah sarki!

Hajiya: Shi na yi ma magana kamar wasa.

Iroro: Eh!

Hajiya: To yanzu, ni abin da nake so da kai.

Iroro: Eh!

Hajiya: Tun da Allah ya kawo wannan abin da nake so da kai.

Iroro: Eh!

Hajiya: Tun da Allah ya kawo wannan abu to ka kula da kyau.

Iroro: Dole!

Hajiya: Na gaba da kai kasan yana gaba da kai.

Iroro: Eh gaskiya ne.

Hajiya: Don Allah, don Annabi ba na son a kawo mishi }ara.

Iroro: Uhm-Uhm!

Hajiya: Game da kai a ce mishi ka yi wani abu, ni abin da nake so ke nan da kai.

Iroro: To babu damuwa Salamatu.

Hajiya: Allah ya yi mana jagora, Allah ya taimakemu.

Iroro: Amin don albarkar Annabi, na gode }warai. Na gode }warai Allah ya bar zamunci.

Hajiya: Amin.

Iroro: Allah ya saka da alheri.

Hajiya: Amin-amin!

Iroro: Eh, Allahu akbar, Allah mai yadda ya so.

Hajiya: Yau za mu kwana muna farin ciki.

Iroro: Wallahi!

Hajiya: Alhamdulillahi!

Iroro: Amman matum ya fita gida yana zallumin dawo wa gida.

Hajiya: Eh.

Iroro: Ai abin ya kai in da ya kai.

Hajiya: To, zamani ne ya canza ko rance ka ke nema.

Iroro: Eh.

Hajiya: Sai ka zaga gida goma baka samu }wandala ba!

Iroro: Baka samu.

Hajiya: Ba shi?

Iroro: Su Malam Jibo saboda sharri cewa suke Iro ya haukace, saboda zama kan kwalbati.

Hajiya: Rashin ku]i ai ba abin da ba zai faru ba sai dai in ka kai zuciyarka nesa.

Iroro: Eh, }warai haka ne.

Hajiya: To Allah ya yi mana taimako.

Iroro: Amin don Nabiyur Rahmati!

Hajiya: Yauwa!

Iroro: Eh na gode.

Hajiya: Bari inje in yi ma yara wanka.

Iroro: Bari inje in samu Baba Dattijo.

Hajiya: To shi ke nan.

**Fitowa ta Biyar**

(A gidan Baba mai tabarau)

Baba Dattijo: (Tari)

Iroro: Salamu Alikum.

Baba Dattijo: Amin wa'alaikummussalam.

Iroro: Aha Baba mai tabarau har yanzu dai muran nan ba ta sake ka ba?

Baba Dattijo: Ai ya sake ni!

Iroro: Ya sake ka ko?

Baba Dattijo: Tare aka yi mu?

Iroro: Allah Sarki.

Baba Dattijo: Kuma zai tafi.

Iroro: Eh, zai tafi haka ne.

Baba Dattijo: Sannu Ibrahim.

Iroro: Yauwa sannu.

Baba Dattijo: Sannu Ibrahim.

Iroro: Eh sannu, Allah sarki.

Baba Dattijo: Ya aka ji da yau?

Iroro: Eh yau ka ganka kana annashuwa, nace to Baba yau lafiya lau?

Baba Dattijo: Wato abin da yasa ka ganni ina farin ciki.

Iroro: Eh.

Baba Dattijo: Abin da manya Arewa ni ke so su yi.

Iroro: To.

| | |
|---|---|
| Baba Dattijo: | Sai yanzu suka ]aga kai suka fara sannin ciwon kansu. |
| Iroro: | Sun falka ke nan? |
| Baba Dattijo: | Suke magana ba tare da jin tsoron kowa ba. |
| Iroro: | Na gode. |
| Baba Dattijo: | Yau in ba tsiya ba Ibrahim. |
| Iroro: | Allah sarki. |
| Baba Dattijo: | Yaushe kare zai iya shiga rigar fatan martaban kura? |
| Iroro: | Eh. |
| Baba Dattijo: | Ya ce zai yayyagashi. |
| Iroro: | Ina ba zai yiwu ba. |
| Baba Dattijo: | Eh. |
| Iroro: | Ya ce zai fito ya ci mutuncin kura. |
| Baba Dattijo: | Ya zauna lafiya. |
| Iroro: | Ya san }arya yake yi. |
| Baba Dattijo: | Arewa ba banza ba ne. |
| Iroro: | Allahu akbar. |
| Baba Dattijo: | Arewa Allah ya yi mana martaba. |
| Iroro: | Allah sarki. |
| Baba Dattijo: | Ya albakace mu. |
| Iroro: | Allah sarki. |
| Baba Dattijo: | Muna da mutuncin mu. |
| Iroro: | Allah sarki Baba. |
| Baba Dattijo: | Amma sai muka zama kurman jamus. |
| Iroro: | Ya kurman jamus yake kuma? |
| Baba Dattijo: | Kurman jamus shi ne, ga shin rana tana dukan shi. |
| Iroro: | Eh. |
| Baba Dattijo: | Idan an yi magana sai ya uhm-uhm. |

| | |
|---|---|
| Iroro: | (dariya) Allahu akbar. |
| Baba Dattijo: | Ya za mu zama kurman jamus? |
| Iroro: | Eh kai |
| Baba Dattijo: | Duk wanda ya ce ma mutumin Arewa kule, don Allah don annabi ka ]aga yatsan ka ka ce masa cas. |
| Iroro: | Na gode. |
| Baba Dattijo: | Ba abin da zai ma. |
| Iroro: | Na gode ranka da]e. |
| Baba Dattijo: | Rashin magana ne shi yasa ake cutarmu. |
| Iroro: | Gaskiya ne ranka ya da]e. |
| Baba Dattijo: | Ni na yarda akwai wasu munafikai cikin mu. |
| Iroro: | Eh. |
| Baba Dattijo: | Amma wallahi tallahi mu muke yar da mutuncin kan mu. |
| Iroro: | Eh gaskiya ne. |
| Baba Dattijo: | To na yi farin ciki. |
| Iroro: | To na gode }warai. |
| Baba Dattijo: | Kai kosai na siya na raba saboda jiya. |
| Iroro: | Eh. |
| Baba Dattijo: | Don Allah ya fadakar da shuwagabannin mu kowa ya tashi mallam. |
| Iroro: | Allah sarki. |
| Baba Dattijo: | Ka fa]i ra'ayin ka. |
| Iroro: | Eh na gode Baba. |
| Baba Dattijo: | Nijeriya ta Allah ce, ba ta uban kowa ba. |
| Iroro: | Eh gaskiya ne. |
| Baba Dattijo: | Allah kuma yana gidan uban kowa. |
| Iroro: | Gaskiya ne Baba. |

Baba Dattijo: Uhm.

Iroro: Na gode Baba.

Baba Dattijo: Ba abin da ya dame mu.

Iroro: Uhm.

Baba Dattijo: Muna nan.

Iroro: Allah sarki.

Baba Dattijo: Ina tare da Allah.

Iroro: Eh }warai da gaske.

Baba Dattijo: Yan arewa wanda dama suke gyangya]i su bu]e idandunansu ras tas ba lokacin barci ba ne yanzu.

Iroro: Ba barci.

Baba Dattijo: Ibrahim ba barci.

Iroro: Allah sarki.

Baba Dattijo: Ba barci.

Iroro: Na gode.

Baba Dattijo: Ba barci.

Iroro: Eh na gode }warai da gaske.

Baba Dattijo: Allah kuma ya taimake su.

Iroro: Amin don nabiyyur rahmati.

Baba Dattijo: Allah kuma ya ba su goyon bayan da ya kamata
Su samu.

Iroro: Amin, kuma Allah ya ha]a kawunansu.

Baba Dattijo: Duk munafikin dake cikinsu ubangiji ya san yadda zai yi maganinsa.

Iroro: Allah ya nuna masu shi.

Baba Dattijo: Ah wannan ba komai.

Iroro: Eh.

Baba Dattijo: Ai mai nema yana tare da Allah.

Iroro: Eh gaskiya ne.

Baba Dattijo: Manjadda.

Iroro: Wajadda, mai nema yana tare da samu.

Baba Dattijo: Ibrahim.

Iroro: Eye.

Baba Dattijo: Na gode.

Iroro: Allah sarki Baba.

Baba Dattijo: Kwanaki dai ]an ku]in nan da ka taimaka min na ji da]i.

Iroro: To ai ka ji ka.

Baba Dattijo: Allah ya rabani da ku]in cizo, wallahi na samu lafiya.

Iroro: To ai kaji ka.

Baba Dattijo: Allah ya rabani da ku]in cizo, wallahi na samu lafiya.

Iroro: Allah sarki.

Baba Dattijo: Na samu lafiya.

Iroro: Eh.

Baba Dattijo: Wallahi tallahi naji da]i kwarai da gaske.

Iroro: Ga hamsin ]in kuma kasan wancan karon hamsin na ba ka.

Baba Dattijo: Ibrahim.

Iroro: Wannan ma karon ga hamsin.

Baba Dattijo: In ya zama na kullum ka zo sai ka yi mini kyauta kuma ai.

Iroro: A'a ya ranka ya da]e ai Hausawa sun ce "ka yara baya sai ka tsinta a gaba".

Baba Dattijo: Wai ka da tabarau ya zo ya na hangen inda ma ba zai iya hanga ba.

Iroro: A a don Allah kada ya wuce ya dai hango bakin mizaninsa. Yauwa tabarau ya dai hango bakin mizanin da zai hango amman kada ya wuce wuri.

Baba Dattijo: To shikenan, Allah ya ba mu sa a na gode Ibrahim.

Iroro: Yauwa.

Baba Dattijo: Allah ya yi maka albarka.

Iroro: Amin don nabiyyun rahmati.

Baba Dattijo: Yauwa.

**Fitowa ta Shida**

(A gidan Malam Jibo)

Iroro: Assalamu alaikum.

Malam Jibo: Wa'alakumussalam, mutumina ai da ji na ce kai ne.

Iroro: Malam Jibo.

Malam Jibo: Na'am.

Iroro: Sannu.

Malam Jibo: Ya gida, ya aiki.

Iroro: Alhamdulillahi, madallah.

Malam Jibo: Yauwa sannu, don Allah ba ka ]inke rigarnan.

Iroro: A'a ga shi ga shi, ya]i maza ka ga sabo an sa me ka gani nan?

Malam Jibo: Ah takardar ]aukar aiki ne.

Iroro: Eh to Alhamdulillahi.

Malam Jibo: Kai ga albashin mai dama.

Iroro: Ga kuma "*loan*" an ba ni dam wallahi!

Malam Jibo: An baka *loan*?

Iroro: An ba ni na ga wasu allawus-allawus duk ana ba ni da ma. Malam Jibo duk mutumin da kaga Allah ya ]orawa talauci kar kai mai dariya, kar ko kai mai sharri, arzi}i na Allah ne ba uban wani ke ba da shi ba irin yadda ka ke zuwa fuw ka wuce ni da mota Alhaji na ji labari har cewa ka ke Allah ya warkar da ni yanzu ka ke garin nan kana cewa Iro ya tabu, to ban tabu ba.

Malam Jibo: To me ya kawo zagi?

Iroro: Wai dai in gaya maka dai na tabbata kana daga cikin masu surutu cikin garin nan. Ai Alhaji Iro ya haukace, ba shi wannan kwalbati ba shi wannan gindan itace, to ga shi nan Allah ya ba ni, yanzu aiki ya samu.

Malam Jibo: Ko ka yi gamo ne?

Iroro: Mahaukaci na buga takarda ne? A'ah mahaukaci na buga takardar aiki ne? Malam Jibo daman na ce yanzu in fara nuna ma tukuna.

Malam Jibo: A'a to meye na tashin hankali Alhaji Ibrahim? Ai ni amininka ne.

Iroro: Wai kasan dai…

Malam Jibo: Ina zuwa.

Iroro: Eh.

Malam Jibo: Ni ba mai ba}in ciki ba ne.

Iroro: E haka ne.

Malam Jibo: Murna ne agare ni yau inji an ce ka zama wani abu.

Iroro: Eh gaskiya ne haka ne.

Malam Jibo: Haka amini yake fa?

Iroro: Eh haka ne.

| | |
|---|---|
| Malam Jibo: | Ka fahimce ni? |
| Iroro: | Amman dai ina son in }ara nuna maka cewa Allah shiya halicci bawansa kuma shi yake azurta bawansa. |
| Malam Jibo: | Haka ne. |
| Iroro: | Ina fatan ka fahimta. |
| Malam Jibo: | Haka ne. |
| Iroro: | Eh, duk abin da ka ga bawa ya samu to daga Ubangiji ne. |
| Malam Jibo: | To nima ina da wata 'yar }aramar nasiha, kasan aikin gwamnati yadda yake Ibrahim. |
| Iroro: | Eh }warai. |
| Malam Jibo: | Wani lokaci ko ka barshi ne ko ya barka kaga na farko. |
| Iroro: | Eh. |
| Malam Jibo: | Kaga in ka je ofis ]innan za ka samu wa]ansu ne a ofis ]innan. |
| Iroro: | Haka ne. |
| Malam Jibo: | Wasu kuma za su same ka. |
| Iroro: | Eh. |
| Malam Jibo: | Manya da }anana, to ka iya takunka. |
| Iroro: | Eh. |
| Malam Jibo: | Abin da ba ruwanka, ba ruwanka. |
| Iroro: | Eh haka ne. |
| Malam Jibo: | Abin da bai shafe ka ba, bai shafe ka ba. |
| Iroro: | Eh. |
| Malam Jibo: | In kuma an baka aikinka ka tsaya ka yi shi. |
| Iroro: | Eh gaskiya ne. |
| Malam Jibo: | Ka kuma tsaya ka koye shi. |

| | |
|---|---|
| Iroro: | Eh haka ne. |
| Malam Jibo: | Ka fahimce ni ladabi da biyayya. |
| Iroro: | Eh. |
| Malam Jibo: | Shi ya kamata ka yi a wannan wurin. |
| Iroro: | Eh gaskiya ne. |
| Malam Jibo: | In kana bu}atar ci gaban ka. |
| Iroro: | Kwarai da gaske. |
| Malam Jibo: | Kuma kar ka yarda a ha]a baki da kai a yi wani dugu-dugu. |
| Iroro: | Eh. |
| Malam Jibo: | Ko a yi wani almundahana, ko a cuci wani. |
| Iroro: | Eh. |
| Malam Jibo: | Ko a musgunawa wani. |
| Iroro: | Eh kwarai. |
| Malam Jibo: | Ka ji shawarata agareka. |
| Iroro: | Na gode }warai da gaske. |
| Malam Jibo: | Allah ya ba da sa a. |
| Iroro: | Amin don nabiyur rahmati. |
| Malam Jibo: | Allah ya ba da sa a. |
| Iroro: | Amin Malam Jibo. |
| Malam Jibo: | Ni ma zan yi sadaka. |
| Iroro: | To!To!! shike nan. |
| Malam Jibo: | Eh na yi murna. |
| Iroro: | To madalla. |
| Malam Jibo: | Allah ya kiyaye. |
| Iroro: | Amin-amin. |
| Malam Jibo: | Allah ya ba da sa a a gaida su Salamatu. |

**Fitowa ta Bakwai**

(A gidansu Ai'sha)

(magana a hankali) Kai! Allah mai iko! Ka dubi Ibrahim da abubuwa sun tsaya mai cak! Amma na ji an ce ya samu aiki har ma ya soma farfa]owa

Iroro: Salamu alaikum, na samu aiki!

Shafi'u: Wa'alaikumussalam.

Iroro: Ina jin ka ka na ta magana kai ka]ai.

Shafi'u: Ni ka]ai nake ta magana yadda kasan wani, na ji an ce abubuwa sun farfa]o.

Iroro: Eh.

Shafi'u: Gashi na ji an ce sai she}i kake, abubuwa sun gyaru.

Iroro: Kawun Salamatu!

Shafi'u: Uwargidan ka?

Iroro: Eh Alhaji Shehu.

Shafi'u: Eh.

Iroro: Shi ta yi wa magana, shi kuma sai ya buga ma Alhaji Balarabe yalla~ai waya.

Shafi'u: Eh.

Iroro: Nan da nan aka ce in je da takardu.

Shafi'u: Kai tsaye.

Iroro: Kai tsaye, aka bani ofis.

Shafi'u: Duk wahalar aikin nan da ake ciki?

Iroro: Aka kawo *loan* aka ba ni, aka kawo wasu alawus aka ba ni.

Shafi'u: Kafin ma ka fara aikin?

Iroro: Haba, Alhamdulillahi yanzu, eh Alhamdulillahi.

Shafi'u: Alhaji Ibrahim!

Iroro: Eh.

Shafi'u: Ni ma ina da wani ]an uwa da yake neman aiki a yanzu, inka samu wata 'yar kafa a wannan wurin na ku.

Iroro: Ah, ah to kuma kaji-kaji sharrin Bahaushe kuma daga samu, ni ban samu abin nan ba kuma ka fara kawo mini kuka.

Shafi'u: Ah, ah nan gaba nake nufi, ba wai yanzu ba.

Iroro: Ni ko zama ban yi ba a kujerar nan kuma wai ka fara kawo mini wai ga wani ]an uwanka. Kai wohoho…

Shafi'u: Ba komai dai.

Iroro: Mutum sai Allah.

Shafi'u: Eh.

Iroro: Shikenan Allah ya rufa asiri.

Shafi'u: Abin da nake so, da ma zan zo in yi maka murna.

Iroro: To na gode }warai.

Shafi'u: Amma tun da ka zo kaga ba sai na sake zuwa ba.

Iroro: Kuma abin da yake tafe dani na biyu.

Shafi'u: To!

Iroro: Ita wannan }anwarka, ka san kwanaki can na nemeta.

Shafi'u: Shekaru dai wake maganar kwanaki.

Iroro: Shi ne nace shekaru waccan da suka wuce.

Shafi'u: Ko ba kana nufin A'isha ba?

Iroro: Ita fa A'isha to na nemeta.

Shafi'u: To, ai kai ka kasa, mun ce ba za mu ba ka ba ne? Ai kai ka kasa.

Iroro: To, na taso yanzu na taso zan yi.

Shafi'u: To, amman ka san ta ta~a yin aure.

Iroro: To!to!!

Shafi'u: To, amma Allah cikin ikonsa.

Iroro: Eh!

Shafi'u: Koda ka kasa ]in nan tai aure ko haihuwa ba ta yi ba sai Ubangiji ya kawo iyakar abin.

Iroro: Eh yanzu sun rabu.

Shafi'u: Don haka yanzu tana nan tana zawarci ne.

Iroro: To rabona ne, ai rabo na ne, kira mini ita, eh.

Shafi'u: A'isha.

A'isha: Na'am!

Shafi'u: Tsohon saurayinki ne.

Iroro: A'isha.

Shafi'u: Ga shi nan.

A'isha: (Dariya) Iroro.

Shafi'u: Bari in barku ku ]an tattauna. In kin gama kya ganni.

A'isha: To, Iroro.

Iroro: Sannu A'isha.

A'isha: A shey! rai kan ga rai?

Iroro: Rai kan ga rai wallahi.

A'isha: Ikon Allah.

Iroro: Eh nayi tafiya ne.

A'isha: Har naji da]in ganinka!

Iroro: Eh sannu (dariya) mun je wani kwas ne shi ne ya kawo da]ewar.

A'isha: Allah sarki.

Iroro: Eh ban samu nayi a wancan lokacin ba dana taso sai aka ce mu je kwas.

A'isha: Allah sarki.

Iroro: To shi ne yanzu na dawo.

A’isha: Kun gama ke nan.

Iroro: Eh mun gama.

A’isha: Ba shakka.

Iroro: Nace bari in zo in ji yaya maganarmu tana nan?

A’isha: (Dariya)

Iroro: (Dariya) in har yanzu kina da bu}ata.

A’isha: {warai kuwa!

Iroro: To!To!!

A’isha: To, ai dama ko can ]in ba wai ni na}i ba.

Iroro: Eh }warai.

A’isha: Halin auren ne ba ka da shi.

Iroro: A a kwas! Kwas!! Kwas!!! Na je.

A’isha: *Oke*! lokacin ne ka tafi ashey!

Iroro: Shi Shafi’u bai fahimta ba. Ni na je kwas ne lokacin da na yi tafiyar.

A’isha: Eh.

Iroro: Eh, Shi ne yanzu na dawo.

A’isha: Kai! a gaskiya kana da rabo.

Iroro: Eh Allah sarki.

A’isha: Shike nan.

Iroro: To, ah an gama, in dai da rabo.

A’isha: To! yaushe ai ni duka-duka watana ]aya, ka san da yake ni ba son sa nake yi ba.

Iroro: Ka san an ce “matar mutum }abarinsa”.

A’isha: Eh haka ne.

Iroro: Koda kin je Allah yasa rabona ne.

A’isha: Haka ne fa!

Iroro: Shi yasa kika dawo, to amshi wannan eh amsa.

A'isha: In kai ma wane?

Iroro: Ah amshi wannan ki sayi kayayyaki tukun eh.

A'isha: Wannan!

Iroro: Eh wannan ga shi.

A'isha: Duka wannan ku]in?

Iroro: Duka ri}e.

A'isha: Duka nawa ne?

Iroro: Duk naki ne.

A'isha: To na gode.

Iroro: To madallah! Eh.

A'isha: Allah ya sanya alheri.

Iroro: Amin! Amin!

A'isha: Allah ya bar mu tare.

Iroro: To madallah.

Shafi'u: To za ka tafi ne ko?

Iroro: Eh mai gida Shafi'u.

Shafi'u: To, shike nan ba damuwa.

Iroro: Eh!

A'isha: Allah Ubangiji ya tabbatar da alheri.

Iroro: Amin don Nabiyyun rahmati, amin don nabiyyun ruhmati.

Shafi'u: In Allah ya yarda za a yi abin nan, daman a gaya maka tun da...

Shafi'u: To ba komai insha Allahu.

Iroro: Ga wannan ka yi abin nan kai ma.

Shafi'u: Ni ma.

Iroro: An!

Shafi'u: An haba, ni ina matsayin…

Iroro: Amshi don Allah, anshi don Allah.

Shafi'u: To ba komai na gode.

Iroro: She ke nan.

Shafi'u: To na gode (sun yi sallama ya fita)

A'isha: Yaya!

Shafi'u: Ke wannan ku]in wa ya baki su?

A'isha: Shi ya bani.

Shafi'u: A kan me? Daga zuwa kawai?

A'isha: To yana }auna ta, nima ina }aunarsa

Shafi'u: To shi dai ina ya san wannan bu]i? ya ]an samu wani aiki kwanan nan ne, na san dai }ila shi ne ya san ya zai abin nan.

A'isha: Eh !too…

Shafi'u: To insha Allah za a yi abin da ya kamata.

A'isha: To shi ke nan, dama abin da zan ce maka ke nan.

Shafi'u: To meye amfanin zaman naki a gida?

A'isha: To shike nan.

Shafi'u: Eh! Ba komai.

A'isha: Ga shi.

Shafi'u: To.

**Fitowa ta Takwas**

(A gidan Iroro)

Iroro: Hajiya.

Hajiya Salamatu: Na'am Alhajin Allah!

Iroro: Kina ciki.

Hajiya: Muna ciki.

Iroro: Sannu.

Hajiya: Yauwa.

Iroro: Yauwa.

Hajiya: Ka dawo ya aiki?

Iroro: Aiki da godiya, to aikin ne ya yi yawa mu shiga nan mu fita nan.

Hajiya: Ai haka ake so.

Iroro: Eh sannu. Yauwa don Allah Hajiya akwai abin da nake so dama in shaida miki.

Hajiya: To!

Iroro: Kin san shi sha'annin rayuwa, akwai ciwo akwai mutuwa?

Hajiya: {warai da gaske.

Iroro: Ko ba gaskiya ba?

Hajiya: Haka ne.

Iroro: To naga dai bai kamata in zalunce ki ba, ko kuma in munafince ki ba ya kamata dai ko mine ne dai in ri}a fitowa ina gaya miki.

Hajiya: Dakata, yauwa don Allah ka yi mini magana ]aya kawkwakwara yadda zan fahimta, ba na son wannan kewaye-kewayen kamar Banufe.

Iroro: Ba kya son randa-bawul.

Hajiya: A a ba na son kewano.

Iroro: To abin da za a yi.

Hajiya: Kana ta kewaye wa kana }arawa.

Iroro: Eh maganar aure ne wanda za a ]aura jibi kada ayi abin nan kice baki sani ba ki zo ki ce na ci amanarki.

Hajiya: Allah sarki.

Iroro: Shi yasa nace gara in zo in shaida miki ki sani eh, jibi ne ]aura auren.

Hajiya: Bazawara ce.

Iroro: To, da kyau, Allah ya sanya alheri.

Hajiya: Amin-amin.

Iroro: Allah ya kai mu lokacin lafiya.

Hajiya: Amin don nabiyyun rahmati.

Iroro: Yauwa!

Hajiya: Amin.

Iroro: Shikenan maganar dama eh shikenan dama wallahi tuntuni ina so in gaya miki ina jin nauyi.

Hajiya: Na me? Allah ya kawo lokaci.

Iroro: Eh }warai da gaske aure ibada ne na ce.

Hajiya: Ko mene ne a rubuce yake

Iroro: Allah sarki fa, ah!

Hajiya: Ba komai.

Iroro: Sannu-sannu.

Hajiya: Yauwa.

Iroro: Sai na dawo.

Hajiya: To sai ka dawo. Allah ya ba da sa a.

## Fitowa ta Tara

Shafi'u: Kai amma al'amura irin wannan to abubuwa ga shi dai yanzu sun yi dai-dai har an ha]a komai insha Allah wannan aure ba zai ba za a fasa ba.

Iroro: Salamu Alaikum.

Shafi'u: Wa'alaikumussalam.

Iroro: Alhaji Shafi'u an gama komai da komai.

Shafi'u: An gama komai.

Iroro: Komai da komai kuma mun tabbatar da sa}o.

Shafi'u: Mun kai sa}o kuma mun tabbatar da sa}o.

Iroro: To!to!! madalla.

Shafi'u: Don Allah kada ku ~ata mana lokaci, mu ba ruwanmu da ~ata lokaci.

Iroro: Eh! Ba wani abu }warai da gaske.

Shafi'u: Ana zuwa ne za'a ]aura aure.

Iroro: Eh a ]aura aure in taho da mata ta.

Shafi'u: Kada ku ~ata lokaci, a gaya wa masu ]aura auren.

Iroro: Eh! Ba wani abu.

Shafi'u: In ma da kai za a zo, ba wani matsala.

Iroro: To shikenan, na gode }warai.

Shafi'u: Na gode.

**Fitowa ta Goma**

(A gidan Amarya tare da {awarta)

A'isha: Kai wannan aure wannan aure, ni yayi mini da]i.

Hauwa: Salamu Alaikum.

A'isha: Wa'alaikumussalamu.

Hauwa: Ah ah! Kwalli (dariya ha]e da shewa) ba don ina mura ba.

A'isha: Eh!

Hauwa: Gudar da zan yi miki wallahi.

A'isha: To ko ni zan yi da kaina (dariya)

Hauwa: Habawa kawalli.

A'isha: Ah-ah yaya dai?

Hauwa: Aure da]i.

A'isha: Ah ke aure wasa ne?

Hauwa: Ga naira.

A'isha: Ke dai bari kawai.

Hauwa: Ina abokiyar zaman naki take?

A'isha: Tana cikin ]aki.

Hauwa: Kullum.

A'isha: Eh!

Hauwa: [aki, ba ko fitowa ku ]an tattauna haka.

A'isha: Kin san ita haka take tana nan yanzu idan kika le}a tana nan tana nafilfilunta, in kin ganta a waje da abin da ya fito da ita, amma in ba haka ba tana ]aki, ba ruwanta,wallahi baiwar Allah.

Hauwa: Ni ah-ah ke da ki zauna da mai shiru-shiru gara me harshe, in me harshe ne kin san kalamin da za ki yi mata ta mayar miki, kin san zaman da zaki yi da ita, amma mai shiru-shiru wallahi ta dafa ki a ruwan sanyi ta cinye ki, in kin yi magana a ce yaushe ta yi magana kin ganta tana salla laf laf ba ruwnata wallahi.

Hauwa: Wa! shi yasa aka sa mata Salamatu ai!

A'ishatu: Eye!

Hauwa: Eh!

A'isha: Ni kuma sai in ganta salaha ce.

Hauwa: Ke kiyayi kan ki.

A'isha: To mene ne bayani?

Hauwa: Bayani?

A'isha: Eh!

Hauwa: Ki gaya wa mijinki, in za a zuba miki wa]ansu irinki to in kuma ba za a zubo ba, wannan ba za ki iya zama da ita ba. Ah! Ina samumu kasau kenan. Kin san akwai wani miciya yana cikin kai ka yi.

A'isha: Eh!

| | |
|---|---|
| Hauwa: | In baki taba shiba ba zai taba ki ba amma kina taba shi daya sare ki sai tafiya, ah ne shiru-shiru! |
| A'isha: | To ka da Allah ya nuna mini wannan lokacin. |
| Hauwa: | Amin summa amin, amin summa amin ki sake bayani. |
| A'isha: | To shikenan Hauwa. |
| Hauwa: | Ki gaya wa mai gidanki. |
| A'isha: | To shikenan na gode. |
| Hauwa: | Kullum tana nafilfili }ila ma ba nafilan take yi ba tana sauraren abin da za ki fa]a. |
| A'isha: | Ko? |
| Hauwa: | Ta nai gaba, ah! Sai an jima kawali. |
| A'isha: | To sai an jima, to wannan. |

**Fitowa ta sha [aya**

(A ]akin amarya)

| | |
|---|---|
| Iroro: | A'isha! |
| A'isha: | Na'am. |
| Iroro: | Sannu. |
| A'isha: | Ka dawo? |
| Iroro: | Wannan }awarki ce? |
| A'isha: | Eh! |
| Iroro: | Allah sarki. |
| A'isha: | Hauwa kenan, ba ka gane ta ba? |
| Iroro: | Eh! Hauwa ce, naga ta yi lullubi ai. |
| A'isha: | Ah sannu da zuwa. |
| Iroro: | Sannu. |
| A'isha: | Wallahi dama ina ta son inga shigowarka. |

Iroro: Ayya! Allah sarki, sannu.

A'isha: Maigidana na kaina (dariya)

Iroro: Lafiya dai ko?

A'isha: Eh! Lafiya lau.

Iroro: To.

A'isha: Amma dai gaskiya ina da Magana.

Iroro: To! To!! Ta mece ce?

A'isha: To kaga dai Salamatu yaya ta ce a cikin gidan nan.

Iroro: Eh!

A'isha: To ni sai inganta tana salla-laf-salla-laf a cikin gidan nan ba irin kuzarin nan uhm!

A'isha: Sai kace ruwan kudididfi, ba harka ba komai ita dai dankama sunan wani gari, bini-bini tana dan}ame a ]aka.

Iroro: Eh!

A'isha: Ba zata fito ba balle mu yi hira, nikenan ni ka]ai a tsakar gida, yanzu da ka zo ba ga shi ba.

Iroro: Eh! }warai fa.

A'isha: Ina ta walkami ina oyoyo maigida yanzu ba kiji da]i ba?

Iroro: Wallahi gaskiyarki, nima abin nan ya fara isata, gaskiyarki fa

A'isha: Ni gaskiya ba na jin da]i, so nike idan ka shigo yadda nake ta tarenka da murna to sai ta je ta ]an kame a cikin ]aki abin duk ya ]aure mini kai.

Iroro: To na yarda da maganarki barni da ita.

A'isha: To shike nan

Iroro: Salamatu!

A'isha: To bari in shigo ciki.

Iroro: Shigowa, Salamatu.

Hajiya: (salati) Sannu da zuwa.

Iroro: Ke don Allah ki ri}a amsa mini magana kin ji ko?

Hajiya: Ah-ah-ah!

Iroro: Ya ina zama da mace kamar ina zama da tunkiya, wallahi bani son mace ba kazar-kazar, wallahi sai in shigo gida bacin rai, can waje a ~ata mini rai sannan gida a ~ata mini rai, mata ba za tai kazar-kazar sannu da zuwa sannu da zuwa ka dawo lafiya ana far'a ka dawo lafiya, kamar ina aure da tunkiya, to ni fa bana son irin wannan, wallahi ki canza, idan ba za ki canza ba ni sai in canza miki wallahi kina amfanin irin wannan, in zauna da mutum kamar alade dim kullum kinma ]aki kullum kina cikin ]aki ko irin fitowa ki sha iskar nan ma ba kya yi.

Hajiya: Ka gama?

Iroro: To nifa ba zan yarda da irin wannan ba ki ri}a kazar-kazar don Allah.

Hajiya: Yi ha}uri.

Iroro: Yanzu dana auro wannan yarinyar har na fara jin da]i wallahi.

Hajiya: Allah sarki.

Iroro: Da na dawo sannu da zuwa sannu da zuwa – sannu da zuwa.

Hajiya: Yi ha}uri.

Iroro: To ki canza in ba za ki canza ba ni sai in canza miki ba na son sakarci.

Hajiya: Ka gama dai ko?

Iroro: Na gaya miki.

Hajiya: Ka gama?

Iroro: In shiru-shiru nake son in auro ‘yar kurma mana, an ta~a yi mini tayin ‘yar kurma nace bana so, bana son irin wannan don Allah.

Hajiya: To bari in yi maka tambaya.

Iroro: To ki canza.

Hajiya: Ah’ah tambaya zan maka, don Allah don Annabi ina son in tambayeka, yaran mu nawa ne?

Iroro: Ke kika sansu.

Hajiya: Au!

Iroro: Shikenan kuma kullum ni ne mai }irga yara kullum ni ne mai }irga yara cikin gida?

Hajiya: To, tsaya, ni iyakar maganata na }ure shi mene ne? Ka gane ko?

Iroro: Eh.

Hajiya: Sabada kaza hajitta ta kenan, kuma Mutum bai isa ya canza min halitta ba.

Iroro: Ba wani halitta, kace kika maida kanki haka.

Hajiya: Ka gane ko? Yanzu dai ka yi ha}uri shikenan.

Iroro: Amma ko kurma ai tana dariya wallahi amma mutum shikenan sai ka ce Saniya.(ya fita cikin fushi).

Hajiya: To a sauka lafiya, ikon Allah, haka ne, ba komai, uhm-uhm, (kira) A’isha.

A’isha: Na’am!

Hajiya: Don Allah ina son zan fita, zan je gidan kaka, amma ban gaya ma maigida ba, kuma bai kamata in fita ba tare da ya sani ba.

A’isha: To.

Hajiya: Amma yanza zan je maza-maza in dawo da sauri kafin ya dawo.

A’isha: To yaya lafiya dai ko?

Hajiya: Lafiya lau ba komai.

A'isha: To shikenan, akwai abin da zan kama miki kafin ki dawo?

Hajiya: A a ba komai ai duk na gama komai.

A'isha: Shi ne ba ki kirani in taya ki ba?

Hajiya: Ah! To don Allah aikin guda nawa yake ai kin sani.

A'isha: To shi ke nan yaya.

Hajiya: Ai idan da akwai abin da ya kamata ki taimaka mini zan yi miki Magana.

A'isha: To, shikenan a dawo lafiya.

Hajiya: To, madallah!

A'isha: Ki gaishe su.

Hajiya: To, sai na dawo.

A'isha: Yauwa.

**Fitowa ta sha Biyu**

Isah: Salamau Alaikum.

Hajiya: Wa'alakumussalam.

Isa: Yaya ina wuni?

Hajiya: Lafiya lau, lafiya.

Isah: Yaya, na zo ne ko da zan samu ]an wani abu ne.

Hajiya: Don Allah ka wuce ka bani wuri babu, wuce nace ka ~ata mini da gani.

Isah: Me ya faru Yaya?

Hajiya: Ina ruwanka da abin da ya faru dani?

Isah: To Allah ya baki ha}uri.

Hajiya: Amin.

Isah: Allah ya baki ha}uri.

Hajiya: Ha}uri kaya ne, ka na]a gammo ka ]auka.

Isah: Allah ya huci zuciyarki.

Hajiya: Wuce ka tafi, ka bani wuni wuri.

Isah: Ah'ah.

**Fitowa ta sha Uku**

(A gidan kaka)

Hajiya: Salamu alaikaum.

Safiya: Wa'alaikumussalamu.

Safiya: Ah'ah iye!

Zuwaira: Uwargida.

Hajiya: Ka gan su dai 'yan tagwaye.

Zuwaira: Kin Fara ba.

Hajiya: 'Yan tagwayen Kaka!

Zuwaira: Uwargida gasa ce dai kina gasa da shi … Ya kamata.

Hajiya: Sannuku-sannunku, ya aiki?

Zuwaira: Yauwa barka dai.

Hajiya: To madalla, na zo cikin sauri ne.

Safiya: To lafiya dai ko?

Hajiya: Wani abu ne yake damuna, naga ba zan nufi gidan Iyaye na ba dole ne in zo wurinku saboda yanzu duk abin da na yi za a ce saboda an yi mini kishiya ne.

Safiya: Haka yake.

Hajiya: Abin da ya faru ina zaune na idar da sallah ina unn…

Zuwaira: Karatu?

Hajiya: Sai na ]an kishingi]a haka in ]an huta sai ya shigo mini da sababi, wai ni ba na kazar-kazar ni mene ne –mene ne, idan ban

canza halaye na ba da dai sauransu, wai shi zai canza mini kazar-kazar, to shi ne na ce bari in zo in gaya maku.

Safiya: Maganar da ya gaya miki kenan?

Hajiya: Eh!

Zuwaira: Duk shekarun nan da kuka yi?

Hajiya: Duk bai sani ba.

Zuwaira: Bai ta~a ganin ba ki kazar-kazar ba, sai yanzu.

Hajiya: Eh!

Safiya: Kai lallai *MUTUM SAI ALLAH!*

Hajiya: Yanzu komai ban iya ba.

Zuwaira: Mutum mai kyau a tafe.

Safiya: To shi baya duba yatsun hannunsa ai inya dubi yatsun hannun sa yasan wani yafi wani, ko ba haka ba? Ya za a yi yanzu a ce ki tashi kina yi mishi ihu kina mishi kyarkyarwa cikin gida?

Hajiya: Eh kuma bakin gwargwado dai zan yi maka sannun da zuwa, ka dawo lafiya lafiya lau tsakanin mata da miji abin da ya kamata ke nan.

Safiya: A kira ki wa?

Zuwaira: Yaya, kin ji maganar nan.

Safiya: *Ah'ah gama, gama mai ajajeren gama mai ]aki gama mai gajeren ]aki.*

Hajiya: To ni ina sauri zan koma.

Safiya: Abin da ya kamata ki yi ki je ki sami kawunmu ki gaya mai

Zuwaira: Ki sami kawunki…

Hajiya: To, shikenan, na gode.

Safiya: Kar ki sake tsawo ya wuce ]aki, ki je ki sami shi Shehu Namadina.

Hajiya: To.

Safiya: Ki gaya mishi kawu kaji-kaji abin da yake gudana.

Hajiya: To, na gode.

Safiya: Allah ya sauwa}e.

Zuwaira: Yaya kin ji ]an Adam ko?

Safiya: Yo dama mana!

Zuwaira: Kin ji mutum, mutum kenan.

Safiya: Mutum kenan, mai kyau a tafe.

Zuwaira: Dama an ce ka shuka ice ka sha inuwa, amma in ka shuka mutum, wallahi in ya tashi sai ka bar wurin.

Safiya: Ah'ah wannan zaune take.

Zuwaira: Bakomai, Allah ya yi maganin abin.

**Fitowa ta sha Hu]u**

(A gidan Kawu Shehu Namadina)

Hajiya: Salamu alaikum.

Kawu: Amin wa'alaikumussalam.

Hajiya: Sannu kawu.

Kawu: Lafiya lau.

Hajiya: Ina gajiya?

Kawu: Lafiya lau, ya na ganki haka?

Hajiya: Eh! To, lafiyar dai da sau}i.

Kawu: Mene ne?

Hajiya: Shi dai wannan waban Allah da ka sama mashi aiki.

Kawu: Naji.

Hajiya: Ka saman mishi aikin nan da ku]in alawus ]in nan nashi ya yi mini kishiya kafin ma a ce an yi bikin sannan ya gaya mini, na

ce mishi Allah ya sanya alheri, ban ce mishi komai ba, na }yale shi, kuma ina hidimomina yarinyar nan ta zo ba wani abu tsakani na da ita ni ban nuna mata ba ita ma ba ta nuna mini ba, muna zaune lafiya, shi ne kawai yau ya zo yana yi mini masifa kazar-kazar

Kawu: To dakata, ina zuwa (salati)Adodo?

Hajiya: Na'am Baba!

Kawu: Adodo-Adodo.

Adodo: Na'am Baba, gani ai ina kusa.

Kawu: Jeka ka kirawo mini Ibrahim.

Adodo: To yanzu ko?

Kawu: Mijin Salamatu.

Hajiya: To ni zan tafi Baba.

Kawu: Jeki-jeki.

Hajiya: To na gode sai anjima.

Adodo: Baba ga shi nan.

Kawu: Ka ba ni kunya,ka kuma ba ni haushi, ban tsammni za ka yi haka ba, wato an baka aiki an ba ka rance ka gyara gida za ka watsa gida, ba a hana ka yin aure ba, amma kasan abinda ka ke yi.

Iroro: To!

Kawu: Ashe haka kake?

Iroro: A yi ha}uri don Allah don Annabi Alhaji, a yi ha}uri, a yi ha}uri.

Kawu: Abin da nake so da kai.

Iroro: To!

Kawu: Abin da nake so da kai...

Iroro: To, shi kenan.

Kawu: Ina ita ba ta yi maka sannu da zuwa, da can ya take maka?

Iroro: Eh! Haka ne.

Kawu: To, bana son irin wannan.

Iroro: To, kuskure ne ya shigo insha Allahu za a gyara.

Kawu: Ka natsu.

Iroro: In Allah ya yarda za a gyara.

Kawu: Allah ya kyauta.

**Fitowa ta sha Biyar**

Hajiya: A'isha?

A'isha: Na'am yaya!

Hajiya: Kina kusa ne?

A'isha: Eh!

Iroro: (Ya shigo ya kirasu) Salamatu.

Hajiya: Na'am!

Iroro: A'isha.

A'isha: Na'am.

Iroro: To abin da nake so.

A'isha: Ka dawo?

Iroro: Don Allah don Annabi a zauna lafiya.

Hajiya: To!

Iroro: Salamatu don Allah don Annabi ki yi mana aikin gafara, abin da yasa kika ga na yi auren nan dama ina da niyya, kin san yanzu mutuwa gudu take, nan da nan sai kiji ance ba wannan ba wannan.

Hajiya: Haka ne.

Iroro: To dama ina da niyyar wannan auren.

Hajiya: To ba komai Allah Ubangiji ya gafarce mu.

Iroro: Don Allah don Annabi ku ha]a, kanku.

Hajiya: Dama kai ne in gida ya lalace kai ne in gida ya gyaru kai ne.

Iroro: Eh! }warai da gaske.

Hajiya: To "Saboda kaza" Allah yayi mana jagora baki ]aya.

Iroro: Amin-amin.

A'isha: Mu dama muna zaune lafiya.

Hajiya: To saboda Allah.

A'isha: Kuma in Allah ya yarda ba wanda zai shiga tsa kaninmu

Hajiya: To Allah yasa.

A'isha: Kuma Allah ya kauda fitina tsakaninmu.

Hajiya: Amin, kuma ya raya mana abinda muka samu da wanda zamu samu nan gaba.

A'isha: To amin.

Hajiya: Yauwa.

To jama'a nan kuma muka kawo maku }arshen wannan wasa namu
Da mu ka san yawa suna "**MUTUM SAI ALLAH**".

**(iii) Wasan Kwaikwayon "Rayuwa". A Wasan Duniya Budurwar Wawa**

**'Yan wasan a yau sune:**

| | | |
|---|---|---|
| ALHAJI SHEHU | - | SHEHU NA MADINA FAKI |
| ALHAJI IBRAHIM | - | IBRAHIM ABUBAKAR FASKARI |
| SHAFI'U | - | SHAFI'U MAGAJI USMAN |
| TIJJANI | - | TIJJANI HALADU |
| ADODO | - | ADAMU [ANJUMA KINAFA |
| USMAN | - | USMAN SHU'AIBU {OFAN KIBO |

| | | |
|---|---|---|
| MALAM JIBO | - | JIBRIN YAHAYA KURIGA |
| DATTIJO | - | BALARABE CIROMA |
| BABAN SIDI | - | SARKI ALIYUDEEN |
| YUSHA'U | - | YUSHA'U SULEIMAN |
| HAUWA | - | HAUWA ABUBAKAR GAMAWA |
| A'ISHA | - | A'ISHATU USMAN |
| HAJIYA | - | SALAMATU SULEIMAN |

WANDA YA RUBUTA: USMAN BABA FATEGI
WANDA YA SHIRYA: MUSA IBRAHIM
WANDA TA HA[A SHIRIN: AHMED ALHASSAN [ANKURMA

**Fitawa ta [aya**

( A Gidan Alhaji Shehu)

(Alhaji shehu mutum ne wanda ya ta~a kasancewa mai arzi}i, kuma mai taimakon jama'a lokacin da yake da arzi}i. To amma daga baya sai ya samu karayar arkrziki. Kuma wa]anda ya taimakawa a baya suka yi arzi}i. Sai suka watsar da shi a yanzu)

Alhaji Shehu: Usman

Usman: Na'am! Baba!

Alhaji Shehu: Ina ka fito ne?

Usman; Na dawo, ba ka aike ni ba?

Alhaji Shehu: To jiya ban yi barci ba.

Usman: Haka ne.

Alhaji Shehu: Kai nake ta tunani a zuciya ta.

Usman: Haka ne.

Alhaji Shehu: Baka da ha}uri! Baka da ha}uri!!

Alhaji Shehu: Duk abin da za ka yi na duniya ka dinga ha}uri.

Usman: Gaskiya ne.

Alhaji Shehu: Muddin ba ka yin ha}uri, ba ka aikata abubuwa tsa kanin ka da Allah, to kai zaka cutu, kai zaka wahala.

Usman: Haka ne: Baba

Alhaji Shehu: Bani son gaggawa cikin al'amarin ka.

Alhaji Shehu: Ina aiken da na yi maka?

Usman: Aiken da ka yi min na dawo, to da na dawo lokacin ka na barci, sai na bari sai ka tashi tukunna.

Alhaji Shehu: To don ina barci baka tashi na.

Usman: Ka yi ha}uri Baba. Don saboda a gaskiya Baba, abin da ka rasa Allah, in ka samu Allah. To amma ni a gaskiya Baba da wani irin hali, wanda yake babu dangana, ya kamata duk abin da keke yi Baba, in ka rasa ka dinga dangana, Allah ne ya baka shi kuma ya hanaka. Irin sakon da ka yi min wurin shi wannan Alhaji Shafi'u, irin maganganun da ya fa]a min ban ji da]insu ba.

Alhaji Shehu: To dakata, wato ni ka ga dai kenan, ni fa]a maka kari}a dangana, ka ri}a yin komai tsa kaninka da Allah. Wato shi ne ni kuma yanzu zaka ce ba ni da dangana, wato ka gane!

Usman: E to, lalle in gadon ne, ni ban gaje ka ba Baba ta ~angaren wannan ne, amma in irin maganar da Shafi'u ya fa]a min a kan wannan sa}o da ka ce inje in kar~o.

Alhaji Shehu: Mai ya gaya maka?

Usman: Ai Baba ba zan iya fa]ar wannan ka ga ni.

Alhaji Shehu: Mai ya gaya maka?

| | |
|---|---|
| Usman: | Ai Baba ba zan iya fa]ar wannan magana ba. |
| Alhaji Shehu: | Shi shafi'un ne? Wata magana ya fa]a da ba za ka iya fa]a min ba? |
| Usman: | I, wai da can! In-in kai a'a! |
| Alhaji Shehu: | To ba komai jeka in ba za ka iya fa]a ba, ni zan ganshi. |
| Usman: | To, shikenan Baba. |
| Alhaji Shehu: | Zanga Shaf'un, ni zai wa wannan mugun aiken, har yarona ya kasa fa]a min abin da aka aiko shi, ni zanga shafi'un. |

**Fitawa ta Biyu**

(A gidan Alhaji Ibrahim)

(Alhaji Ibrahim ya yi sallama ya shigha gidansa)

| | |
|---|---|
| Alhaji Ibrahim: | (ya shigo }was-}was) "am kawo sa}o ]azun ko? |
| A'isha: | E yana nan cikin gida. |
| Alhaji Ibrahim: | To sai a gyara shi. |
| A'isha: | To Alhaji. |
| Hajiya: | (Tai sallama ta shigo cikin gidan) |
| Alhaji Ibrahim: | Hajiya sannu da zuwa. |
| Hajiya: | Kana ciki ne? |
| Alhaji Ibrahim: | Ey Hajiya, ina ciki (ya gaishe ta) |
| A'isha: | Umma sannu da zuwa! |
| Hajiya: | Yauwa A'isha yaya gida? |
| A'isha: | Gida lafiya lau Hajiya. |
| Hajiya: | Dama nayi sa'a ashe kana ciki? |
| Alhaji Ibrahim: | Ey ina ciki Hajiyya, ni ma ban da]e da shigawa ba. |
| Hajiya: | To madalla, a takaice dai na zo wajen ka ne. |

Alhaji Ibrahim: Ai da kin aiko in zo Hajiya, ai ba sai kin zo ba.

Hajiya: Ai na fi son in sameku gaba ]aya. Saboda wa]ansu abubuwa da suke faruwa, wa]anda kuma agaskiya bana jin da]insu, masoyana ba su jin da]insu. Tsakaninka da iyalin ka.

Alhaji Ibrahim: To, assha-assha!

Hajiya: Ka saurare ni da kyau, kaji abin da zan fa]a maka.

Alhaji Ibrahim: Ey ina jinki, ina jinki Hajiya.

Hajiya: Wato duk abin da ya ha]aka da iyalinka bai kamata kace idan tai maka wasa yanzun nan zaka saketa ba, saki wani babban abu ne ga Ubangiji Subhanahu wata'ala saboda haka duk abin da zaka yi tsakanin ka da iyalinka kada ka yarda wani ya ji bare har ya je yana }araswa. Ni banji da]in irin wannan kalamai da kake yi ba, idan ranka ya ba ta, domin ni ya kamata in zo in gaya maku gaskiya ko kai ko ita duk ]aya ne a wurina, tun da Allah yasa ka auri wannan yarinya, to kuma ni da mahaifinka ko mahaifiyarka duk ]aya ne na ke gani, abin da na ga ka yi wanda yake ba dai-dai ba, ina da 'yancin in yi maka fa]a tsa kanina da Allah. In ka ji ya yi maka kyau in ba ka ji ba shikenan.

Alhaji Ibrahim: Na ji Hajiya.

Hajiya: Ni abin da ya kawo ni ke nan, saboda iyayen mu malamai ne, suna magana a kan saki, mutane dayawa suna ta lalata aurensu game da ainihin maganar saki, saboda haka motsi ka]an sai ka ji an ce yanzu za ki kwashe kayanki ki bar gidanan, yanzu zan sake ki. To ka tuna fa kai namiji

ne mijin mata hu]u kuma komin yawan da mu ka yi a duniya ba za mu rasa masu auren mu ba, saboda haka, ni abin da zan gaya maka kenan, ka kiyaye don Allah.

Alhaji Ibrahim: To shikenan Hajiya, na gode Hajiya.

Hajiya: Kuma Rabi ta haihu yau tagwaye, saba da haka za ta je barka.

Alhaji Ibrahim: A'a ta je babu komai, za ta tafi Allah shi raya.

A'isha: Ai mata barka kafin in zo Hajiya.

Hajiya: To za ta ji sai anjimanku.

Alhaji Ibrahim: (Ya fara fa]a) Ke ashe hankali bai isheki ba? A'isha baki da hankali?

A'isha: Da na yi me Alhaji?

Alhaji Ibrahim: Duk fa]an da mu ka yi sai kin je kin fa]awa uwarki, ke baki da tunani?

A'isha: Ai ni bani nake zuwa nake fa]a mata ba.

Alhaji Ibrahim: To yaya akai ta sani, ina da irin wa]annan kalmomin.

A'isha: To ai kaine idan abu ka]an ua ha]a mu sai kai ta ]aga murya duk makwabta sai sunji abin da muke ciki, dole makwabta sai su je su fa]a mata.

Alhaji Ibrahim: A'a ke keke zuwa ki kef a]a mata, yaushe wasu makwabta zau je su fa]a mata, don kawai sun jiyo mu ta Katanga.

A'isha: Ni ya za a yi inje infa]a mata.

Alhaji Ibrahim: To ni dai bana son sakarci irin wannan.

A'isha: To ni dai ina baka shawara, in nai maka laifi in za kai min fa]a ka ri}a kwantar da muryarka.

| | |
|---|---|
| Alhaji Ibrahim: | Ke nifa ban son sakarci idan mun yi abunnan a dinga barinshi nan. |
| A'isha: | In kana da]a ka rin}a rage murya, ta yadda babu wanda zai san halin da ake ciki. |
| Alhaji Ibrahim: | (ya sake taso mata da fa]a) to sai in mai da kaina kurma, don zan yi maki fa]a? |
| A'isha: | A a ka rin}a rage murya, yadda ba wanda zai ji abin da muke ciki. |
| Alhaji Ibrahim: | Ba ni son irin wannan wallahi. Bari in fita na ji ance Tijjani ya zo ya na son ganina. |
| A'isha: | To, adawo lafiya. Idan kana rage murya wa zai dinga sanin abin da muke ciki. |

**Fitowa ta Biyu**

(Tijjani ya zo gidan Alhaji Ibrahim ya sa an yi sallama da shi, ya zo ne kuma don ya shaida masa cewa Alhaji Shehu bai ji da]in ba.)

| | |
|---|---|
| Alhaji Ibrahim: | Tijjani, barka da zuwa |
| Malam Tijjani: | Alhaji Ibrahim barka da gida, an wuni lafiya? |
| Alhaji Ibrahim: | Lafiya lau yaya gidan yaya damuna? |
| Malam Tijjani: | (ya amsa, kuma ya ci gaba da magana) wai shin ka je gidan AlhajiShehu kuwa? |
| Alhaji Ibrahim: | Alhaji Shehu, bai jin da]i ne? |
| Malam Tijjani: | Kai baka san halin da yake ciki ba, na neman taimako? |
| Alhaji Ibrahim: | Me ya dameni da halin da yake ciki, malamTijjani? |
| Malam Tijjani: | Me ya yi ne? A'a! |

Alhaji Ibrahim: Me ya ha]a ni da Alhaji Shehu har da za ka gaya min cewar wai yana cikin wani hali na neman taimako.

Malam Tijjani: Haba-haba, Ibrahim, ai ban yi tsammanin wannan kalmar za ta fito bakinka ba!

Alhaji Ibrahim: (Cikin fa]a) me kake nufi? Me ya dameni, ina ruwana da Alhaji Shehu.

Malam Tijjani: Himm… Haka ne.

Alhaji Ibrahim: Aiko ka aka yi ka gaya min wannan maganar ko kuwa kai kaga dama ka zo ka furta min wannan maganar?

Malam Tijjani: To ai gani nayi, ko da yake na taba jin wata wa}a da Shata yake cewa “asalin sarauta Daura”

Alhaji Ibrahim: Shin Shehu yana sa arzi}i ne?

Malam Tijjani: A’a Allah ke sa arzi}i.

Alhaji Ibrahim: To don me za ka zo ka ce wai na je wajen Alhaji Shehu?

Malam Tijjani: To ai naga mutum kane kuma komai ka zama yau, gobe ba ka isa ka raina Alhaji Shehu ba, saboda nasan ya taimaka maka.

Alhaji Ibrahim: To Tijjani ni ba za ni ba, zuwa wajen Alhaji Shehu ba dole ba ne. Kuma taimaka mashi ba dole ba ne. Kai kanka in ba duniyar nan da ta ha]ani da kai ba ina ruwa na da kai duniya ce fa kawai ta ha]ani da kai. Balle Alhaji Shehu ina ruwa na da kai.

Malam Tijjani: Abin har ya kai ga haka ne?

Alhaji Ibrahim: Me ya kawo ka gidana ka fa]a min wannan Magana? Arzi}i Allah ke yi ko kuwa ku ke raba arzi}in nan ne?

Malam Tijjani: Na sani arzi}i na Allah ne amma ni dai don naga muna tare da kai, da kuma irin taimakon da Alhaji Shehu ya yi maka, shi yasa na zo na fa]a maka.

Alhaji Ibrahim: Alhaji Shehu bai yi mini komai ba. Allah ne ya yi min arzi}i.

Malam Tijjani: Ey na sani.

Alhaji Ibrahim: Saboda haka kar ka zo ka fa]a mini wannan maganar.

Malam Tijjani: To amma ai akwai sila ko?

Alhaji Ibrahim: To kace masa na ce ba ni zuwa. Idan shi ke da arzi}i to ya janye arzi}in, ban zuwa. Idan kuma kai ke da arzi}i to ka je ka yiwa Alhaji Shehu.

Malam Tijjani: A a nima nema nake wajen Allah.

Alhaji Ibrahim: To ka je ka ce mashi ban zuwa.

Malam Tijjani: Allah ya baka ha}uri, maida wu}ar.

Alhaji Ibrahim: To ba ni son irin wannan malam Tijjani.

Malam Tijjani: Wannan Magana ta wuce, yaya ]an abin da za a …

Alhaji Ibrahim: Ai kuma ka bata Magana, wallahi ka bata Magana, ko kwabo baka samu. Ka bata min rai wallahi haka kawai sai ka zo ka ce wai na je… Alhaji Shehu. Ni ke kawo karayar arzi}i, ko ni ke sa a yi arzi}i?

Malam Tijjani: To bari in yi maka ta ku]inka, ka tafi talla ko?

**Fitowa ta Uku**

(Alhaji Shehu da yaronsa Adodo sun zo gidan Alhaji Shafi'u)

Adodo: Baba ga gidan Shafi'un nan.

Alhaji Shehu: Nan ne gidan Shafi'un to yi min sallama da shi.

Adodo: (Ya matsa }ofar gidan ya yi sallama), Assalamu alaikum.

| | |
|---|---|
| Alhaji Shafi'u: | Wa'alaikumussalam. |
| Alhaji Shafi'u: | (Ya fito) kai lafiya yaro? |
| Adodo: | Lafiya lau sai alheri. Baba ne Alhaji Shehu yake son ganinka. |
| Alhaji Shafi'u: | Yana ina? |
| Adodo: | Yana waje. |
| Alhaji Shafi'u: | To mu je. |
| Alhaji Shafi'u: | Assalamu Alaikum. |
| Alhaji Shehu: | Bai amsa sallamar ba, sai ya fara fa]a na zo ne inji irin laifin da na yi maka daka muzantani dana kuma nima ka muzantani. Don aiken da nayi mishi ya kasa fa]a min. sabada haka gani na zo ka fa]a min. |
| Alhaji Shafi'u: | Ai zan fa]a maka tsoronka nake ji? Ka aiko shi in taimaka maka, ni abin daya ]aure min kai shi ne wai duk a garinnan ka rasa wanda zaka aiko ya taimaka maka, wai sai irina, nace to ni ba zan taimaka ma ba, kuma bari in tuna maka in ka manta, ni bani daga cikin wa]anda ka taimakawa su ka yi arzi}i wa]anda ka taimakawa sunanan ka sansu, su Alhaji Ibrahim, kuma ai sun san kana cikin wannan halin. Don me zaka tunkaroni. Don haka ni nasan wa]anda ka taimakawa suka yi arzi}i, yau ka karye su sun yi arzi}i sun wula}antaka, shi yasa nace ya je ya fa]a maka. |
| Alhaji Shehu: | Au wato karyewa na yi? Don na samu rashi, abin da yake hannuna ka }are shi ne na karye. Baka san komai ba na Allah ba ne? |
| Alhaji Shafi'u: | Niko nasan haka. |

| | |
|---|---|
| Alhaji Shafi'u: | Yanzu dai da me ka zo, mai-maita wannan maganar ne ya kawo ka ko-ko me? |
| Alhaji Shehu: | Na zo ne dai don naji ance kana yi, wannan dai shi ne zuwa na farko. Don Allah a taimaka. |
| Alhaji Shafi'u: | Ey to babu halin taimakawa, su Alhaji Iro suna nan a gari. |
| Alhaji Shehu: | Nasan da su ai… |
| Alhaji Shafi'u: | Duk da ha kan dai ba dai yau ba, don Allah ai da wani ]an uzuri a cikin gida, don mun yi da wani zai bugo min waya. sai anjima. |
| Adodo: | Baba abin da za a yi kawai mu koma gida. Ka rungumi }addara, mu ro}a kawai a wajen Ubangiji. |
| Alhaji Shehu: | Allah yasa mu dace. Mu tafi gida Adodo. |
| Adodo: | To Baba, amen. |

**Fitowa ta Hu]u**

(A gidan Malam Jibo, Alhaji Ibrahim ya zo gidan Malam Jibo don ya shaida mishi abin da Tijjani ya yi mishi)

| | |
|---|---|
| Malam Jibo: | Kana ji na? |
| Alhaji ibrahim: | Ey, ina jinka Malam Jibo. |
| Malam Jibo: | Ni na ganka ne kamar a yamutse… |
| Alhaji ibrahim: | Wato ai shi ne nake maka bayani, kawai sai ga Tijjani ya zo gidana. Ashe Tijjani ba shi da kunya, ashe mutumin banza ne? Kawai sai ya zo ya yi min sallama na fito. muka gaisa, kamar maganar arzi}i, na ]auka yadda ya saba zuwa mu gaisa hala ta kawo shi. Kawai daya tashi sai ya ce wai ka ko je wajen Alhaji Shehu. |

| | |
|---|---|
| Malam Jibo: | Oho, Alhaji Shehu? Allah sarki, ina jinka. |
| Alhaji ibrahim: | Nace to Tijjani me kake nufi, wai ai Alhaji Shehu kuma ai ya karye, sai nace to ni na karya Alhaji Shehu? Ko Iro na sa talauci? Ba Allah ke sa arzi}i ba? Allah ya ba Alhaji Shehu arzi}i, Allah ya kawo wa Alhaj Shehu karaya. |
| Malam Jibo: | To kai Alhaji Ibrahim kasan dai kai abokina ne, kuma muna bizines tare da kai. |
| Alhaji ibrahim: | Wannan haka ne. |
| Malam Jibo: | Yanzu saboda Allah ina laifin Tijjani? |
| Alhaji ibrahim: | Ya yi mini laifi, ni wallahi yayi mini laifi idan ina da niyyar taimako sai ya zo ya fa]a min. |
| Malam Jibo: | Ni ban ga laifi ba anan "sai wawa sai mahaukaci shi ke raina asalin sa" inji Alhaji Mamman Shata. |
| Alhaji ibrahim: | To, nine mahaukaci ke nan? |
| Malam Jibo: | Ina fa zaka zama mahaukaci? |
| Alhaji ibrahim: | To, me kake nufi? |
| Malam Jibo: | Allah shi yayi sanadin arzi}in ka Alhaji Shehu yayi sanadin arzi}in ka, Allah shi ya taimake ka Alhaji Shehu shi ya taimake ka Alhaji Shehu shi ya taimake ka. To mene ne? ni ban ga laifin Tijjani ba? |
| Alhaji ibrahim: | To shi kenan kuma don ka taimake mu yun kai kuma ka karya mutum kai kuma ka karye, sai kuma ka zama mishi laura? |
| Malam Jibo: | Yaya larurar duniya? Shin da ya me yasa baka ]auki wani abu ka ba shi ba ko kuma ka aike shiya kaima Alhaji Shehu. |

Alhaji ibrahim: Kai ma na lura bakin ku ]aya da Tijjani.

Malam Jibo: Ban isa gaya maka gaskiya ba ne?

Alhaji ibrahim: Wannan ni ba gaskiya ka fa]a min ba. Banji da]in wannan maganar ba Malam Jibo.

Malam Jibo: To shi kenan, ni dai kaji inda na tsaya.

Alhaji ibrahim: Ai ni da nasan kaima haka za ka yi min da ban zo wajen ka ba.

Malam Jibo: To shi kenan, sai anjima ni dai harkarmu ba za ta lalace da kai ba (ya tsaya nan yana ta mamaki sai daga }arshe ya shiga gida).

**Fitowa ta Biyar**

(Gidan Alhaji Ibrahim)

(Hauwa {anwar Alhaji Ibrahim ta yi sallama ta shigo, ta taradda matar shi a cikin gida suka gaisa, ta zo wajen ]an' uwanta ne don ya taimaka ma ta)

Hauwa: Ina yaya?

A'isha: Aiko yayanki ya fita bai dawo ba.

Hauwa: Gaskiya yaya ya zo ya taimakamana a wannan halin da muke ciki. Wai shin ke a matsayinkin na matarshi wai shin kina fa]a mai gaskiya kuwa? Don in gida ya gyaru mace ce, in kuma ya baci ma ita ce. Don inkin ha]a kanmu da shi sai muji da]i.

A'isha: A'a Hauwa na kwabeki, ki dai na irin wannan maganar, ki saurara da kyau kiji, nifa ban iya shiga tsakanin hanta da jinni ba, nima yaya na karke zamana da shi.

Hauwa: Ai, ashe kema a defane ki ke?

Alhaji Ibrahim: (yayi gyaran murya ya shigo) Hauwa ce yau a gidan namu?

Hauwa: Ey, nice (ta gaishe shi)

Alh. Ibrahim: Me ya kawo ki kuma? Shekaranjiya fa ki ka zo gidannan.

Hauwa: To ai ko da na zo shekaranjiya ban same ka ba.

Alh. Ibrahim: To lafiya?

Hauwa: Lafiya lau. Amma na zo neman taimako ne, don muna cikin wani hali.

Alh. Ibrahim: To wai ni waye ya taimake ni, wai ni ubanwa ya taimakeni. Kai kuna so ku maidani mahaukaci fa wallahi. Arzi}i fa Allah ke ba da wa fa Hauwa, ni inda na san haka ne da ban ro}i Allah ya bani arzi}in nan ba wallahi, sai abar zaune kan tabarmata wallahi, sai in huta.

Hauwa: A a yanzu sai ka rarrabar da arzi}in ka huta.

Alh. Ibrahim: To karki }ara tako min gidana gaya miki in dai neman taimako zaki rin}a zuwa. Karki }ara takomin gida.

Hauwa: Ina ce dai gidanka ka ce in bari ba duniyar ba, gadanka dai yanzu zan barshi.

Alh. Ibrahim: Wa naji ki fita min daga gida.

Hauwa: To, ]an {aruna sai anjima.

A'isha: (ta tafi sai ta kira ta Hauwa! Hauwa!! Ita kuwa ta}i dawowa)

Alh. Ibrahim: Don Allah ki ri}a korarsu, ba dole ba ne sai sun zo kowa ya zo ki hana ki ce na ba da doka.

A'isha: A a Alhaji ka daina cewa in dinga korarsu. Yanzu ma ban kore su ba irin maganar da Hauwa take gaya min, ina ga nace kar su shigo wannan gidan?

Alh. Ibrahim: A a duka-duka fa ba'a wuce sati biyu (2) ba da ta zo gidan nan na ba ta Naira ]ari (#100).

A'isha: Ni dai shawarar da zan baka ka rin}a kyautata ma su don in ba ka kyautata mu su ba to wa zai kyauta ta masu?

Alh. Ibrahim: Dukkan dukiya ta zan kwashe in ba su? Ko ya ya ki ke so na yi?

A'isha: Ni dai ban ce ka kwashe dukiyarka ka ba su ba. Amma dai ka rinka kyauta ta ma su.

Alh. Ibrahim: Ba zan yi ba fa arzi}i na Allah ne, Allah mutum yake ro}a ya yi mishi arzi}i. Saboda haka sai su je su ro}i Allah ya ba su na su.

A'isha: (cike da mamaki, a yayin da ya fita ya barta a tsaye) Allah yasa ka gane.

**Fitowa ta Shida**

(A gidan mai unguwa)

(Alhaji Shehu ya zo gidan mai unguwa don ya bayyana masa abin da Alhaji Shafi'u ya yi ma shi)

Alhaji Shehu: Wato abin da Shafi'u ya yi min ba zan manta ba har abada a nan gidan duniyar, ya wula}antani ya wula}antani irin maganganun da ya fa]a wa yarona ma, da ya zo kasa fa]a min yayi...

Mai Unguwa: Wato saboda abin yana da nauyi ba zai iya fa]a wa mahaifinsa ba.

Alhaji Shehu: Sai har yana cewa da ni "wa]anda na ba arzi}i suna nan wai har yana kiran Iron, ai su ka taimakawa, ban da shi ma ka taimaka wa dubbai me yasa ba zaka je wurinsuba". sai na kwantar da murya nace ka yi wa Allah ka taimaka don na ji an ce kana taimakawa, sai ya taso min da fa]a.

"ba zan yi ba, ba zan yi ba". Sai na ba shi ha}uri,, ha kan na taso ba nauyi.

Mai Unguwa: To ai baka ji ba kana dai jin yin fa]a ne kawai, don kuwa ya fa]a maka gaskiya ne. don kuwa ba shi daga cikin wa]anda ka taimakawa.

Alhaji Shehu: To ai don na ji yana yi ne shi yasa na je wajensa.

Mai Unguwa: To haka ne amma ba wajibi ba ne ya taimake ka, da abin da ya kamata ka yi sai ka je wajen Ibrahim.

Alhaji Shehu: Shi Alhaji Ibrahim ]in wai?

Mai Unguwa: Ey.

Alhaji Shehu: To ni yanzu ina zan ganshi?

Mai Unguwa: Ai wannan mai sau}i ne (ya kira wani daga cikin gida) Yusha'u!

Yusha'u: (Yusha'u ya amsa ya shigo) Gani Baba.

Mai Unguwa: (ya ci gaba da tambayar Alhaji Shehu) wato yanzun ko ha]uwa ba kwayi da shi ke nan? Don naji kana tambayar wai ina zaka ganshi?

Alhaji Shehu: Ni abin da yake bani mamaki da mutanen Arewa ]an'uwa yana da arzi}i, amma 'yan uwan shi sai kaga wani sakar zana yake yi, wani Allah-Allah yake yi kaka ta yi ya tafi kalar gya]a, wani ruwa yake ]ebowa ya sai da don ya samu abin da zai ci. Amma na nesa sai kaji an zo ta hanyarka yin godiya saboda wane ya yi min abu kaza.

Mai Unguwa: Wannan al'ada ce ta mutanen Arewa, wanda ya zama dole mu ajiye ta gefe guda, mu so namu. Tun da yanzu idan 'yan uwanshi masu arzi}i suka zo aka ce musu wannan ]an uwanshi ne, zai ji da]i?

| | |
|---|---|
| Mai Unguwa: | Yusha'u yi maza ka ce wa Ibrahim ya zo ina kiranshi. |
| Yusha'u: | To Baba. |
| Baba Sidi: | Sun yi ma ku]i mugun sabo, saboda zaka ga ha}}in Allah ma ba ya fitowa daga cikin dukiyoyinsu, wai duk don kada ku]in su }are. |
| Mai Unguwa: | To wa ya ba shi ku]in? Ai dole a cire ha}}in Allah a ciki. |
| Baba Sidi; | Kuma ha}}in ne na Allah ma ba a biya ba balle a yi zumunci. |
| Mai Unguwa: | Mutane ya kamata su san abin da suke yi, da ha}}in ma}wabta, da ha}}in 'yan uwa ba a yi wasa da shi saboda gaba. |
| Yusha'u; | Baba ga shinan ya iso. |
| Mai Unguwa: | Yusha'u wane nace ka kira min? |
| Yusha'u; | Ibrahim ka ce Baba. |
| Mai Unguwa: | To wannan da nake gani fa su wane ne? wani da kulki, wani da sanduna wani da adda… |
| Alhaji Ibrahim: | Ey Baba, *siquritina* masu kariya gare ni ne Baba, don na lura Baba yau }asar nan in ba wani mu}ami gareka ba, ba za a baka kariya ba, wai don kana da arzi}i. To, don gudun kada wata rana in je in sha kashin banza, shi yasa nake tafiya da irin wa]annan }attin. |
| Mai Unguwa: | To, yanzu dai abin da nake so da kai shi ne, wa]annan wa]annan ba ka yarda da kariyar Allah ba sai ta su to ni ba na son ganinsu kai nake son gani. |
| Alhaji Ibrahim: | Kai }aura! Goje! Ku jirani a waje (suka ce to suka fita). |
| Yusha'u: | Baba ni ma zan shigo gidan. |
| Mai Unguwa: | To! |

Mai Unguwa: To! yau kai Ibrahim wannan wane ne?

Alhaji Ibrahim: Alhaji Shehu ne.

Mai Unguwa: Yaushe rabonka da ganinshi?

Alhaji Ibrahim: Ey tun kwanaki da ya yi mura, mun ha]u da shi a bakin kasuwa mun gaisa.

Mai Unguwa: Wato ba ma gidan ka je ba ke nan? Ina so in nuna maka cewar Alhaji Shehu lokacin da yake cikin ganiyar arzi}insa, yana da dukiya sosai kuma ni nasan ya taimakawa mutane. Kuma kai da kanka ka zo nan kana so in ha]a ka da Alhaji Shehu don ya taimaka maka ya saka ta hanyar da yake ]auko kaya. Amma kaga halin da Alhaji Shehu yake ciki kuma ko gida ka ce ba ka zuwa sai dai ku ha]u a hanya. Kai sai ma an ce maka ka je ka gaida shi, ko kuma ka yi ma shi wani abin alheri?

Alhaji Ibrahim: Wato, wallahi Baba ba ni da lokaci ne.

Mai Unguwa: Har kai yanzu wani mai ku]i ne nan ina su Dan Karuna? Kuma komai ku]inka yau, kai ina Sayyadina Abubakar ne? wanda yake shi taimakon jama'a kawai ya ke yi.

Alhaji Shehu: Randa ya ganni a kasuwa, ina cikin buhun dawa ina ce zai biya min, amma sai cewa ya yi shi kenan ni na tafi. Ban ma }ara sani abin da ya ce ba sai ya yi gaba, nima ko da naji an ce an sallama maka sai nai gaba saboda ba ku]in biya.

Mai Unguwa: Ba wai ya zo ya kawo }ara ba ne, a a abin daya kamata ace mutum ya yi ne aka fa]a maka. Amma abin da nake so ka yi yanzu ka ro}eshi gafara.

| | |
|---|---|
| Alhaji Ibrahim: | Alhaji Shehu ka yi ha}uri, don Allah ka yafe mani, kuma zan zo gida duk abin da ya kamata in yi zan yi kuma basussuka da duk ake binka zan zo duk in bibbiya su. kuma ni na san abin da zan yi. |
| Mai Unguwa: | Kuma banji da]i ba }anwarka ta zo jiya take gaya min irin abin da ka yi mata ka ce wai karta sake zuwa gidanka. |
| Alhaji Ibrahim: | Ta zo Baba wancan satin na ]auki ku]i har Naira ]ari (#100) na ba ta. |
| Mai Unguwa: | A yanda kake kai mai arzi}in nan mene ne naira ]ari. Idan baka taimaki 'yan uwanka ba to suwa zaka taimaka? |
| Alhaji Shehu; | To ko za a taimake ni ya fara ba ni a nan kada ya fita daga nan ya mance dani. |
| Mai Unguwa: | Ai zai baka tunda ya ce zai baka. |
| Alhaji Shehu: | To shikenan. |

## Fitowa ta Bakwai

(A gidan Alhaji Ibrahim)

(Sarakuwarsa Hajiya ta yi sallama ta shigo)

| | |
|---|---|
| Alhaji Ibrahim: | Hajiya sannu da zuwa. |
| Hajiya: | Yauwa, agurguje nike abin da ya kawoni shi ne, idan zaka kyautata wa 'yan uwanka ka kyautata musu tsakaninka da su kar ka go ga wa yarinyar nan ba}in jinni kasan dangin miji yadda suke kuwa? Kullu yau mun zasu ce ita matar nan ita ta hana ka. Kana so ka rin}a jawo mata ba}in jinni bakin gwargwadon abin da Allah ya |

hore maka ka dinga taimaka musu don Allah. Ni dama abin da ya kawoni ke nan.

Alhaji Ibrahim: To Hajiya na gode, kuma in sha Allahu zan gyara. Hajiya ki gai da gida.

A'isha: To Alhaji ka dai ji abin da ta ce.

Alhaji Ibrahim: Ey naji don Allah a yafeni, Baba ma ya kirani duk maganar da yake fa]a min kenan. Ni wani lokaci sai in dinga tunanin in ku]in nan suka }are yaya zan yi, ina zan samo wasu? Ni kinji abin da yake hanani sakin ku]i kenan.

A'isha: To ai in ma ka ba su Allah zai fi bu]a maka (Allah na gode maka, yanzu ya gane. Masu hali irin nashi, Allah yasa su gane suma su daina.)

To Jama'a nan muka kawo maku }arshen wannan wasa namu da muka sa wa suna: "Rayuwa" a cikin shirin mu na Duniya Buduwar Wawa sai kuma wani mako idan Allah ya kai mu za ku ji mu da wani sabon shirin.

**(iv) Wasan "Jahilci Ciwo". A Wasan Duniya Budurwar Wawa**

**'Yan Wasa**

Adamu: - Adamu [an Juma Kinafa

Isah: - Isah Garba Tinau

Usman: - Usman Jabo {ofar Kibo

Dattijo: - Balarabe Chiroma

Malam: - Abdulmumini Isah Kanoma

Malam Zube (Mai Gida): Jibrin Yahaya Kurunga

Iro: - Ibrahim Abubakar Faskari

Shafi'u: - Shafi'u Magaji Usman

Sidi (Baba Sarki): - Sarki Aliyu Deeni

Balarabe: - Adamu Muhammed

A'isha: - Adamu Aliyu

Salamatu: - Salamatu Sleiman

Safiya: - Safiya Muhammad

Wanda ya rubuta: - Usman Baba Fataigi

Wanda ya shirya: - Musa Ibrahim

Wacce ta ha]a shirin: - Aganas Silvanus

Mai gabatarwa: - Ibrahim Abubakar Faskari.

**Fitowa ta [aya**

(A gidan kaka)

Salamatu: Assalamu alaikum.

Kaka: Wa'alaikumussalam.

Salamatu: Kaka ina wuni ina gajiya?

Kaka: lafiya lau. (gaisuwa)

Salamatu: Kaka na zo muki da wani labara ne na san baki sani ba.

Kaka: Wani ne ya mutu?

Salamatu: Ai gara mutuwa da shi?

Kaka: Subhanalillahi!

Salamatu: Ba wani abu ba ne sai dai tsakanin Ai'sha da mijinta domin tuntuni zaman banza suke yi, ya saketa sau ]aya, ya saketa sau biyu ya saketa sau uku, kuma suna tare. Kuma a takaice yarannan biyu an haife su bayan an yi duk sakin ne.

Kaka: Subhanalillahi!

Salamatu: To ina gani bai dace ba shi yasa nace gara in zo in fa]a miki domin ranar lahira ba mu san abin da za mu ce ba.

Kaka: Subhanalillahi! Wannan wace irin tijara ce ]aki ba rufi ance sai bayan an yi saki uku sannan aka sake haihuwar yaran? Lallai shege baya tsakanin saurayi da budurwa sai dai tsakanin mata na aure da mijinta. Yanzu yaran nan biyu duk bayan da aka yi sakin ne aka haifesu?

Safiya: Guda biyu ba?

Salamatu: To ni kin san halin Baba yadda yake idan naje na fa]a masa ya lullu~e ni da fa]a da kuma tanbayoyi wanda zan zo ina dana sani ban je ba.

Kaka: Wannan amsar ba ta da gaskiya ki tafi idan ya yi maki tambaya sannna ki ba da amsar, domin ni kaina da ki ka kawo wannan maganar gurina bani da abin da zan iya yi a kan wannan maganar saboda haka ki yi mishi bayani ina mai tabbatar miki da cewa zai saurareki domin ya yi maganin wannan abu.

| | |
|---|---|
| Safiya: | Ni fa…! |
| Kaka: | Wannan ba komai a kai |
| Safiya: | Ita kuma ta yarda saki ne ya yi mata amma yafi }arfinta a kan dole shin ba uku ya yi mata ba, to sai ta kaurace masa daga haka. |
| Kaka: | To za a yi maganin abin insha Allahu tafi ki samu Baba ki gaya masa. |
| Safiya: | To bari inyi in tafi |
| Kaka: | Ki saki jiki ki same su Allah kuma ya kyauta wannan bala'in domin wannan bala'i ne. |

**Fitowa ta Biyu**

(A Gidan Baba)

| | |
|---|---|
| Baba: | Ni wannan yaron kullum idan na tashi fita sallar asuba na bu]e }ofar gida na kan tashe shi }arfe biyar domin ya yi sallah amma ba zai tashi ba sai }arfe goma na safe yake tashi to wai mene ne dalilin da yasa yake haka ne? |
| Baba Sarki: | Ga kuwa kiran sallah an yi. |
| Baba: | Ina yi maka wannan abu tun muna da rai, idan ban yi maka wannan abin ba mai za ka ce tsakanin ka da Allah. |
| Adamu: | Baba wallahi ban dawo wa da wuri ne |
| Baba Sarki: | Kai Adamu ka tuna kana bauta wa Allah mu tsakaninmu da ku tarbiya da ilimi mun ba ku ilimi da tarbiya ku yi aiki da shi idan kuka }i za mu sa muku ido a kan abin da kuke yi tun muna da rai. |
| Adamu: | Wallahi ban dawo wa da wuri ne idan nayi hira da daddare na dawo na kwanta sai naji na makara. |

Baba: Duk wani yaron arzi}i daga sallar magariba zuwa sallar isha har zuwa }arfe goma sai mutum ya dawo gida.

Adamu: Baba in sha Allahu na daina ba zan }ara ba.

Baba: Idan ma ba ka bari ba ni na san abin da zan yi.

Adamu: Na gode Baba.

Baba Sarki: Kar ka bi yaudaran samari fa, akula fa.

Salamatu: Salamu alaikum.

Baba: Wa'alaikumusslam.

Salamatu: Sannun ku Baba.

Baba da Abokinsa: Yauwa sannu Salamatu.

Salamatu: Gidan lafiya?

Baba: Lafiya lau.

Baba sarki: Ina ganin Salamatu lafiya?

Salamatu: Baba abin da ya faru wata gagarimar Magana ce na zo da ita a tsakanin A'isha da mijinta ina son a taimaka mani ita wannan yarinyar a ta}aice dai ya yi mata saki uku, da kansa da yara uku sannan da ga baya suka haifi yara biyu to wa]annan yara biyun an haifesu ne bayan an yi saki nan uku.

Baba: Wato yara biyun?

Salamatu: Ey wato ni kuma abin sai ya kasance yana damu na har kasa barci na ke yi sai dai banci barawo, sai na gaya wa kaka, sai ta ce na zo na gaya maka ni kuma ina jin nauyin gaya maka sai ta ce in zo in gaya maka don a san abun da za a yi saboda duniya nan gidan banza ce domin idan sun kasance a haka gobe kiyama mai za su ce wa Allah?

Baba: To amma mai yasa ba a gaya min ba tun farko?

Salamatu: To, ni abin ne naga ya dameni kuma ma yayanmu dai naga kamar sun sani ko ba su sani Allahu ya'alamu.

Baba: Nasan irin wannan abin shi yake damunki domin da zarar mutum ya zo, in ya wuce gaisuwa to shi kenan zan tsaida shi daga nan domin bana son jin wani magana tsakanin shi da mijin shi to shi ya kawo wannan abun yanzun insha Allahu zan dunga sauraron abun da ya kawo mutum don ai gyara irin wannan.

Salalmatu: Ya kamata. Don irin wannan abun ya ta~a faruwa Baba, wata rana wani yaro ne Babansa na alwala sai suka yi hanu da wani mutum ya gama wanke }afar dama ke nan bai gama ta hagu ba sai ya ga mutumin nan zai bace mashi sai ya shafa da gudu ya bi shi, sai yaron nan ya shiga gidan da gudu ya ce "mama-mama kin ga Baba ko bai gama alwala ba ya bi wani mutum da gudu" sai ta kwa~e shi ta ce "Don Allah kar ka dameni da surutu wuce ka bani wuri", har akai barci Uba bai dawo ba sai a ka tashi yaron sai ya mai maita abin da ya fa]a to har yau uban nasa bai dawo ba. Saboda haka a dunga sauraro idan mutum ya kawo jawabinsa.

Baba: To, na gode ai }inji na ce na daina daga yau.(ya yi kira) Isa zo. Don Allah zan aike ka maza kaje wurin Ibrahim kace ina kiran shi ku dawo tare.

Isa: To!

Baba: Allah shi kyauta, lallai ni ne ke kwa~on ku in kun zo ince ba na son jin wata magana, amma yanzu in Allah ya

| | |
|---|---|
| | yarda tun da ga abun da ya faru zan zan ri}a sauraro }ila akwai wani abu na gyara. Na yi kuskure a gaskiya. |
| Ibrahim: | Sannu ina gajiya. |
| Baba: | Lafiya lau. |
| Ibrahim: | Salamatu ne? |
| Salamatu: | Ey. |
| Baba: | Kasan Salamatu yaya ce wajen matar }anin ka? Ta kawo min wani labari a tsakanin A'isha da Mijinta ka ga mu ba za mu fahimci abin da ke tsakaninsu ba. |
| Ibrahim: | Ey, haka ne. |
| Baba: | Tsakanin A'isha ne da mijinta Usman. Da farko ya saketa, ya kuma sake sakin ta kai har ya yi mata saki uku kuma bayan saki uku da ya yi mata har sun haifi 'ya'ya biyu, shi yasa wannan abu ya dameni. |
| Ibrahim: | Baba kace akwai shegu guda biyu bayan ukun na halas? |
| Baba: | An zauna ne kamar ba a a yi ba. |
| Ibrahim: | Ke! ya tuntuni ba ku fa]a ba? |
| Salamatu: | Tsoron Baba na ke yi. |
| Baba: | Shi yasa nace yanzu zan dunga tsaya wa inji bayanin da yara suka zo min da shi. |
| Salamatu: | Kuma abin har hanani barci ya ke yi. |
| Ibrahim: | Subahanallahi! |
| Baba: | Ina son ka bincika da kyau ne don kaji duk abin da ya ke faruwa a tsakaninsu. |
| Ibrahim: | Ai babu aure a tsakaninsu ke nan. |
| Baba: | Ka tafi duk yadda za a yi yarinya ta kwaso kayanta ta dawo gida. |

Ibarahim: Subahanallahi! Subahanallahi!!

Baba: Wannan abu dai babu kyau.

Ibrahim: Kai?

Baba: Allah dai ya kyauta.

Ibrahim: Na gode Allah shi kyauta, ke kuma sai ki tafi gida.

Salamatu: *To Whom It May Concern*: Baba na tafi.

Baba: Allah ya yi maki albarka.

**Fitowa ta Uku**

(Adamu da abokansa wajen hira)

Adamu: Lokaci ya yi ni fa zan wuce gida.

Balarabe: Haba yaushe daren ya yi ballantana a fara?

Adamu: Kai ni dai gaskiya dare ya yi mun.

Balarabe: A gurin wa?

Adamu: A guri na.

Balarabe: Mu yanzu muka fara ma.

Adamu: Ni dai gaskiya a'a.

Balarabe: Idan kaga na bar wurin nan asuba ce ta yi.

Adamu: Kai kenan, ni dai gaskiya bazan iya zama a irin wannan wurin ba, kuma *daddy* ma ya yi mun fa]a, kuma naga gaskiya ne Saboda haka ni ba zan iya zama har irin wanann lokacin ba.

Balarabe: Kasan da kafin ya zama tsoho kasan irin hirar da ya yi ne?

Adamu: To, ai wannan lokacin shi ne.

Balarabe: Ba wai dole ne in ya gaya maka ka ]auka ba zancen sallah ne duk lokacin da ka tashi ka yi.

Adamu: Kai, Balarabe idan har ya kasance ban saurari maganar mahaifi na a wannan lokaci ba, sai ya mutu sannan in zo in yi da na sani.

Balarabe: Idan ya mutu, abin da ya fa]a maka ka tuna.

Adamu: A'a ba haka ba ne, kai, Balarabe ni za ka bar ni in tafi gida ko ko a'a?

Balarabe: Idan ka ce ka matsa za ka tafi, to ban naira ]ari (#100) na da ka baiwa yarinyar nan shekaran jiya.

Adamu: Abin ma gori ne?

Balarabe: Ey, an yi ma.

Adamu: Idan batun naira ]arin da ka bani ne to gobe da safe zan ba ka. Allah ya shirye ka naira ]ari dai ko?

Balarabe: Ey.

Adamu: To, ba shi ke nan ba.

Balarabe: To, ai akwai haraji a ciki ]ari biyu zaka ba ni.

Adamu: To, ga shi ni idan ba za ka amsa ba to shikenan ni dai zan tafi.

Balarabe: Allah ya shirye ka.

Adamu: Ni ka ke cema Allah ya shirya ni? Ko kai zan cewa Allah ya shirya ka domin ni ya rigaya ya shirya ni.

Balarabe: To, tafi abinka waye baya sallah, in an ba ni Aljanna ka ri}e riga ta, ka ga yadda zan naushe ka wallahi.

Adamu: Don Allah bani guri.

Balarabe: To, na ba ka.

**Fitowa ta Hu]u**

Ibrahim: Salamu alaikum

| | |
|---|---|
| Usman: | Amin wa'alaikumussalamu |
| Ibrahim: | A a, Usman. |
| Usman: | A a, Alhaji Ibrahim barka da zuwa. |
| Ibrahim: | Yauwa. |
| Usman: | Lafiya dai an tashi masallaci ina ta magana ba ka jini ba. |
| Ibrahim: | Ey haka ne. |
| Usman: | Sannu. |
| Ibrahim: | Yauwa. |
| Usman: | Lafiya dai? |
| Ibrahim: | Ya tsakanin zamanka da kai da matarka? |
| Usman: | Babu…Ba komai muna zaune lafiya sumul. |
| Ibrahim: | Ba ka sake ta ba? |
| Usman: | Maganan saki bai taso ba, wani irin saki? |
| Ibrahim: | Usman ka saki matar ka saki uku, amma kuma har yanzu kana tare da ita, kuna zama zaman zina, kuma ance wa]annan yara biyu na 'yan shekarun nan, }anana }ananan nan bayan saki uku ne aka haifesu. |
| Usman: | Wani shege ya gaya maka? |
| Ibrahim: | Ubanka ne ya gaya min kaji ko, idan ni zaka yi wa tashin hankali ba za ka ijiye mana shegu a cikin gida ba wallahi (cikin fushi) |
| Usman: | Ibrahim, kwantar da hankalin ka. |
| Ibrahim: | (cikin fushi) Mu za ka kawo wa iya shege kana son ka ijiye mana shegu a cikin gida kana kiran yaro yana cewa *"I dey come"* to mu ba mu gaji irin wanann iskancin ba wallahi. Yarinyar nan kuma zata kwashe kayan ta wallahi tallahi, kawai kuna zaman zina, da yarinya ka saketa saki |

|  |  |
|---|---|
|  | uku, kuma ka dawo kana zama da ita har a ka haifi ‘ya’ya biyu to Allah ya tsine ma halinka wallahi, da wa’azi na ke yi, da mutane sun shiga uku duk shegen da ya yi mini tambayar banza na buge shi. |
| Usman: | Yaya ka kwantar da hankalinka (cikin sanyin murya) |
| Ibrahim: | Ka ga ]an iskan banza! |
| Usman: | Ka yi ha}uri! |

**Fitowa ta Biyar**

| | |
|---|---|
| Malam mudi: | Assalamu alaikum |
| Ibrahim: | Wa’alaikussalamu, Malam Mudi. |
| Mudi: | Ibrahim ni zan wuce na ji kana ta… lafiya dai ko? |
| Ibrahim: | Allah bai tsine wa shegu ba da kuma wanda ya ajiye su? |
| Mudi: | Duk tsinannu ne. |
| Ibrahim: | Mutun ne ya saki matarsa saki uku bayan sakin uku nan sai suka ci gaba da zama har suka haifi yara biyu. |
| Mudi: | ‘Ya’yan zina ne kawai wa]annan. |
| Usman: | Malam kada ka bi ta nasa fa, ka zo ka same shi yana bambami. |
| Ibrahim: | (ya fusata) Uwarka ce take bambami, ka zo ka tara mana shegu a gida. |
| Mudi: | Bai dace ba. |
| Usman: | Idan zai yi bincike ne, sai ya hauni da fa]a kamar wani ]an sa. |

| | |
|---|---|
| Mudi: | To, da kai da shi wane ne ke gaba da wani? Kuma kasan ance babban wa uba. |
| Usman: | Da iyalina da komai yake zazzare mani ido, shi waye? |
| Mudi: | Iyalinka aka ce ka sake su? |
| Usman: | Ha]a mu aka yi don anga muna zaune lafiya da shi shi yasa ake son a ha]a mu. |
| Mudi: | Ibrahim ka yi bincike sosai a kan wannan lamarin. |
| Ibrahim: | Wannan lamari gaskiya ne, kuma sai ta bar gidanmu. |
| Mudi: | A to gaskiya barin ta gida shi ne gaskiya. |
| Ibrahim: | Ina nan gidan zaki ha]a kayan ki. |
| A'isha: | Na ha]a kaya na, dama shi ne ya hana ni tafiya.  Ai na gaya masa ba aure ya ce sai na zauna in zan fita ya kalallameni da da]in baki.  Ni ga akwatina nan duk na zuba kayana duka a ciki. |
| Usman: | Na sake ta ne? |
| Ibrahim: | Ey, ka sake ta, jahilcin banza da wofi. |
| Mudi: | Saki uku? |
| Ibrahim: | E, saki uku.  Kuma ya hana ta tafiya. |
| Mudi: | Ai ko garin da ba ilimi ba a wannan. |
| Ibrahim: | Kuma haihuwa biyu gare su bayyan saki uku |
| Mudi: | bayan saki ukun kuma suna zaune tare? To Allah shi kyauta. |
| Ibrahim: | Amin! |
| A'isha: | Idan na }aurace masa ya hauni da duka. |
| Ibrahim: | Zo ki hau gidan gaba. |
| A'isha: | To! |

## Fitowa ta Shida

| | |
|---|---|
| Ibrahim: | A'isha. |
| A'isha: | Na'am sannu |
| Ibrahim: | Yauwa sannu. Saboda Allah da Annabi wannan bawan Allah har saki nawa ya yi miki? |
| A'isha: | Saki uku ne kuma ya hanani in tafi. |
| Ibrahim: | Innalillahi, tafi ki fara kwashe kayan ki. |
| A'isha: | To. |
| Usman: | Mata ta ce. |
| Ibrahim: | Baka isa ba. |
| Usman: | Mata ta ce, kuma ba ka da iko da ita sai dai ni. |
| Ibrahim: | Bari insa a nemo miki akori kura ki kwashe kayanki ki tafi. |
| A'isha: | Ai na gaya maka zama ya riga ya }are na gaya maka amma ka }i ji. |
| Usman: | Kin san yaya idan wani lokaci iska ya buga, haka yake yi. |
| A'isha: | Bawani iskar da ya buga, to ni ba zan zauna ba ni kuma zan tafi gidanmu ne yanzun. |

## Fitowa ta Bakwai

| | |
|---|---|
| Usman: | Assalamu alaikum. |
| Malam Shehu: | Wa'alaikumussalam, kai da gidan ka sai ka tsaya kana ta sallama. |
| Usman: | Haba wannan mahaukacin ne yake neman ya ~ata mani rai. |
| Malam Shehu: | Wai gamo ka yi? |

Usman: Ibrahim, ai gara in yi gamo, da dai wannan haukan da ya yi mani wallahi gara in yi gamo.

Malam Shehu: Wani Ibrahim ka ke magana?

Usman: Ibrahim dai shi yayan nawa.

Malam Shehu: A a.

Usman: Muna zaune lafiya da mata ta in ]an abu ya taso ya ce wai… Ya ji a gari ana cewa wai na sake ta saki uku wai mun ci gaba da zama da ita. Shi ne ya zo ya dunga yin mini hauka, kuma ni duk lokacin dana saki yarinyar nan inna huce sai in ce na dawo da ita. Sau uku, amma duk da haka wai nayi laifi saboda Allah fa?

Malam Shehu: Usman ina ganin kayi gamo

Usman: A a.

Malam shehu: Ey, ai ina jin ka yi gamo Usman. Gaskiya kai gamo, mene ne naka na cewa har sau uku ka saki matarka, kuma ka dawo da ita. Mahaukaci ne kai Usman?

Usman: Ey… Ashe bakinku ]aya ne?

Malam Shehu: Shin ya buge ka? Ai Ibrahim sakarai ne, wallahi in da ni ne sai na buge ka saboda na tabbatar baka da hankali saboda babu yadda za a yi ka saki matar ka saki uku ka ce ka dawo da ita. Yaushe ne ka sake ta saki uku?

Usman: Abu ya riga ya da]e.

Malam Shehu: Subhanallahi, ya da]e yanzu yara nawa ne?

Usman: Guda biyu ne bayan mun yi saki uku mum haifi 'Ya'ya biyu da ita

Malam Shehu: Subhanallahi la'ilaha illallahu.

Usman: Wannan abu fa ya da]e ba yanzu ba ne kuma ance idan kayi abu ya da]e ana yafewa mutum shi.

Malam Shehu: Usman an sa mu makaranta, ba mun girma ne kawai ba mun yi makarantar allo ko ba ka yi ba ne?

Usman: Mun yi.

Malam Shehu: To, mai ya kai ka yin aiki haka, don Allah gafara ka ba mu wuri sakaran banza.

Usman: A a, lallai bakin ku ]aya ne.

Malam Shehu: Ey, sakaran yaro kawai ka nemi ka ~ata mana gida kawai Allah shi kyauta, saki uku, kuma sannan kana tare da matar. Ibrahim ma ya bani haushi da bai sa ice ya buge ka ba ]an iskan yaro kawai.

**Fitowa ta Takwas**

(A gidan Baba sarki)

Usman: Salamu alaikum Baba.

Baba sarki: Wa'alaikumussalam Usman lafiya ko?

Usman: Lafiya amma ba lau ba.

Baba sarki: To, mai ya faru?

Usman: Na zo ne na ro}i wani arzi}i a wurinka, saboda kasan kai abokin Baban mata ta ne, shi ne nace bari na zo na gaya maka wani abu.

Baba sarki: Wani abu ne?

Usman: Dama maganar mata ta ce wata rana na ta~a mata saki uku sai muka ci gaba da zama, shi ne wai sai nake ji a gari wai muna zaman zina ne, to wai shi ne yayye na suka zo suna ta yi mini fa]a.

Baba sarki: Yanzu ka zo ne ka gayamun na shiga cikin wannan haram ]in. Yanzu idan shi Uban matar ta ka yaji wannan saki uku, sai ya ce wa yarinyar ta tattara kayanta ta koma gidanka, dana bar }ara magana da shi har abada to ko da gaya mun haka, to ba matarka ba ce.

Usman: To, Baba ance wai idan mutun ya sayi tunkiya domin gyara wai malamai suna gyara auren.

Baba sarki: Da tunkiyan,da kuma malamin da zai yi gyaran duk wuta za su. Baka zuwa makaranta ne? Kuma ka tafi ka bani wuri.

Usman: Babu wani abu da za'a yi?

Baba sarki: Babu.

Usman: To, shi kenan.

**Fitowa ta Tara**

(A Gidan Usman)

Usman: Assalamu alaikum A'isha! A'isha!! A'isha!!! (yaji shiru) Wato ta bi maganan wannan mahaukacin ta kwashe kayan ta, A'isha ko ta shigo kicin ne? wannan abu fa ya zama da gaske ni da na ]auki abun kamar wasa, (yana mamaki).

Ibrahim: Ai'sha ta bar gidan, kuma wallahi kada ka kuskure ka sake zuwa wurin da yarinyar nan take kaji ko? Idan ka }i zamu ha]a ka da 'yan sandan shari'a tunda kai baka zuwa makaranta. Ina halas 'ya'yan zuriyar mu ka zo ka da]a

| | |
|---|---|
| | mana su da 'ya'yan haram saboda Allah da Annabi jahilci hauka ne Usman? |
| Usman: | Yanzu dai ta tafi shi kenan? |
| Ibrahim: | Ey, ta tafi shikenan, ka tafi ka samu shegun ba kaniken da zai gyara wannan auren in gani. Kawai ka tashi ka ha]a mana 'ya'ya da 'ya'yan zina Allah ne ka]ai ya san matsayinsu, idan baicin kai ]an Uwana ne, sai nace maka Allah ya isa! |
| Usman: | Ka yi ha}uri! wato ]an hakin daka raina shi kan tsole ma idanu. Wato ni na ]auki wannan abu ba wani abu ba ne to gashi dai yanzu, masu hali irin nawa Allah ya shirye su. Ni kuma Allah ya yafe mun. |

**Fitowa ta Goma**

(A Gidan su Salamatu)

| | |
|---|---|
| A'isha: | Sallamatu. |
| Yaya: | A'isha ne? |
| A'isha: | Ey, sannu yaya. |
| Salamatu (yaya): | Ya mutan gidan? |
| A'isha: | Lafiya lau, yaya na zo ne na yi miki godiya yadda ki ka ceto ni daga wannan halin. Allah ya yi miki sakayya. |
| Salamatu (yaya): | Amin. |
| Maigida: | A'isha ce ta zo nan gidan? |
| Salamatu (yaya): | Ey, ta zo ne tana godiya a kan abin da nayi mata. |

Maigida: A gaskiya abin da ki ka yi sai dai muna fata Allah ya yafe masu kura-kuran da suka yi, aure kada ku yi tunanin sake mayar da wannan don ba ku da aure har abada ko kun yi wani auren kin fito ba za ki sake auren shi ba. Yara kuma Allah shi raya su, ana yin kura-kurai daban-daban a kan haka wani mutun ance ya saki matarsa har kusan san bakwai amma suna tare da ita.

Salamatu (yaya): Wai sai a ce za a taru a yi addu'a agyara to wai akwai wani gyara ne wanda ya wuce na Allah?

A'isha: Babu yaya.

Salamatu (yaya): Shi fa ya fa]a duk wani mijin da ya saki matarsa saki uku, to babu aure a tsakaninsu.

A'isha: Haka ne yaya kullun idan nayi masa maganan wannan aure fan a haramun ne, sai ya ce ya zo wajenku ya yi magana ance an gyara.

Salamatu (yaya): Haka abokinsa ya yi, uwarsa ta }i sai ya kawo ku]i dubu biyu ya bata da ta}i kar~a sai ya makata a kotu aka yi shara'a sai da aka ci tarar ku]i daga wajen uwar.

Maigida: Kana ganin wannan magana ba wani wasa, aure a tsakanin ku bashi, domin duk wanda ya auri mace tana cikin idda to ba shi da aure.

A'isha: Ai ba zan koma gidan shi ba! Ai ba zan koma gidan shi ba!!

Salamatu (yaya): Ke kuma kiyi ta istigfari.

Maigida: Kullum!

Salamatu (yaya): Kuma kiyi addu'a Allah ya ba ki nagari.

A'isha: Kuma masu hali irin wannan Allah yasa su gane.

Salamatu (yaya): Amin, kiyi ta istigfari Allah kuma zai yafe miki, ki kuma gai da su Baba.

A'isha: Na gode yaya na tafi.

To jama'a masu sauraronmu yau kuma nan muka kawo maku }ashen wannan wasa na mu da muka sawa suna JAHLCI CIWO daga nan gidan Rediyon Tarayya na Kaduna a huta lafiya.

**(v) Wasan "Mutuwar Zuciya". A Wasan Duniya Budurwar Wawa**
**Abokan hirar mu a yau sune:**

| | | |
|---|---|---|
| Gwamna Iro: | - | Ibrahim Abubakar Faskari |
| Pamsec: | - | Shehu na Madina Paki |
| P.A: | - | Adamu Danjuma Kilafa |
| Shafi'u: | - | Shafi'u Magaji Usman |
| Moda: | - | Tijjani Haladu |
| Mallam Jibo: | - | Jibrin Yahaya Kuriga |
| Dattijo: | - | Balarabe Chiroma |
| Baba Sidi: | - | Sarki Aliyuddeen |
| Haladu: | - | Haladu Garba |
| Mallam: | - | Abdulmumini Isah Kanoma |
| Usman: | - | Usman Shu'aibu Kofar Kibo |
| Isah : | - | Isah Garba Liman |
| Hauwa: | - | Hauwa Abubakar Gamawa |
| Safiya: | - | Safiya Muhammad |
| Hauwa: | - | Hauwa Garba |
| A'isha: | - | A'ishatu Aliyu |
| Zuwaira: | - | Zuwaira Dalhatu |
| Salamatu: | - | Salamatu Suleiman |
| Salamatu : | - | Salamatu Katsina |
| Wanda ya Rubuta :- | | Usman Baba Fategi. |
| Wanda ya Shirya: | - | Musa Ibrahim. |
| Wanda ta Hada Shirin :- | | Victoria Duru. |

Sai ni da na Gabatar : Ibrahim Abubakar Faskari
A madadin Sashin Hausa Rediyo Nijeriya na Kaduna
Nake Cewa a Huta Lafiya.

**Fatowa ta [aya**

(A gidan Shafi'u)

Shafi'u: Assalamu alaikum

A'isha: Ni ni wallahi na gaji, kullum zaka gidan Gwamna kuma kullum haka kake zuwa zikau haka kuma kake dawowa zikau.

Shafi'u: To mene ne na tashin hankali? Ke baki tsayawa.

A'isha: Haka masu zuwa ganin Gwamnan suke dawowa gida?

Shafi'u: To da in da nake zuwa da ya wuce nan wurin ne eye?

A'isha: To ni banga zahiri ba!

Shafi'u: Banga… bangane abin da kike nufi ba!

A'isha: Au baka gane ba?

Shafi'u : Ey…

A'isha: To zaka gane ba na ce da kai ne daga yanzu duk lokacin da kaje gidan Gwamna ka dawo da leda da nauyi ba maganar kenan.

Shafi'u : To nauyin da da nake baki kina nufin daga ina nake samo su ba daga gidan Gwamna ba. Ni fa bani son tashin hankali ey…He ban son irin abubuwan da kike mani bana so, na gaya maki ey hey. Idan ina harkana bana so mutum yasa man ido. Yanzu iNda kuma nike neman ku]in nan ban son mutum na samin ido abubuwan dana keyi.

A'isha: To shake nan na daina sama ido na shirya sai mu tafi tare.

Shafi'u: Ina ?

A'isha : Nace tare zamu tafi

Shafi'u: Ai ba mahaukaci ba ne ni, kin taba ganin an ]auki mace an je wurin Gwamna da ita?

A'isha: Nace tare zamu tafi da kai.

Shafi'u : nace ina zamu da ke ?

A'isha : Gidan gwamna in gani idan Gwamna yana baka maka in gani idan ma baya baka maka in gani, idan kuma kaucewa kake yi kana wani wuri da shi to kaga duk zargin da na ke maka ya kauce. Ko ba haka ba?

Shafi'u : Au Abin ya zama 'yar kure ne, rainin har ya kai nan ? To wallahi karya ki ke yi.

A'isha : To, }afarka }afa ta.

Shafi'u : A a haba A'isha, yanzu saboda Allah meye naki na haka?

A'isha: (Dariya) yauwa-yauwa. Ai wallahi kai mai gidan wani lokaci idan ba na ]an bu]e wuta ba, ba ma daidaitawa.

Shafi'u : Amma kuma kar ki zarce, ba a zarcewa ki kwantar da hankalinki, can muke ta abubuwanmu, ko ba gaskiya ba, kuma ai al'amarinku na mata ku dai ku zauna a gida ku yi ta yi mana

addu'a kawai in zamu fita sai ku ce Allah ya ba da sa a. Ey, kar ki damu, maganan da na fa]a ita ce. Yauwa!

A'isha: Yau cefane na mai lafiya zaka kawo mun.

Shafi'u : E, in Allah ya yarda.

A'isha: To a dawo lafiya.

Shafi'u : Amin! Amin!!

A'isha: Allah ya sa a dace.

Shafi'u : Amin.

A'isha: Kaga Mallam ba don ina bu]e masa wuta ba, haba wa...

## Fitowa ta Biyu

(A gidan Mallam)

Malam: (Kwas-kwas-kwas (na tafiya) tari! Ukhum, Ukh! da gyaran murya) Kai Alhamdu lillahi, kaga garin Allah ya waye kuma Allah ya kawo abin da za'a ci a sha a yi sutura a kuma a taimaka ma wani. To...

Shafi'u: Salamu Alaikum.

Usman: Salamu Alaikum.

Malam: Wa Alaikumussalam.

Usman: Malam na ciki?

Malam: Ei, ina ciki.

Shafi'u: Allah ya gafarta Mallam.

Malam: Mallam Usman dama kana nan? Ba'a ko ganinka

Usman : Mallam ina nan gefe ]aya.

Shafi'u: Shi dai wannan ba'a ko maganan shi domin ko ganuwa ba ya yi, inka gan shi nan ta baci.

Usman: (Dariya)

Shafi'u: A'a, kar kayi mun mugun hukunci.

Usman: Ashe gara ni ina le}owa.

Mallam: Ai gaskiya ne.

Shafi'u: Ai to gara ni muna ha]uwa a masallacin juma'a

Malam: Yauwa.

Shafi'u: Usman ba ni da lokaci, kai ka san yadda al'amuran suke

Usman: Ei, haka ne lallai.

Shafi'u: Allah gafarta Mallam.

Malam: Almajiri dai.

Shafi'u: Gaskiya dai al'amura ne suka cabe na yanayin siyasan nan ne. To mu dai mun saba yadda muke zuwa muna 'yan harkokinmu

muna samun na cefane da na kashewa, nan gidan Gwamna a gidan gwamnati wajen 'yan siyasa.

Malam: Ei, kwarai-kwarai.

Usman : Kafin a yi zabe ba, ka fa]a masa.

Shafi'u : To Allah cikin ikonsa

Usman : Kafin a yi zabe.

Shafi'u : Ai ya san komai.

Usman : Duk inda muka tafi, muka sami abin da muke so.

Mallam : Na'am!

Usman : Mu ciko aljihunmu a wajen 'yan siyasar nan har muma mu wadata wasu.

Mallam: Wannan gaskiya ne.

Usman : To amma tun da aka ce an gama komi na bangaren siyasar. To haka muma an gama da mu fa! yanzu haka muke tsaye cik.

Mallam : Wato kun gama aiki kenan. Subahanallah, Allahu akbar.

Usman : Yanzu haka muke tsaye cik komi ya tsaya mana.

Shafi'u : Kasan wani abun mamaki ne ?

Mallam: To amma kuma kuna zuwa gidan Gwamna?

Shafi'u : Da ana ganin, ganin Gwamnan shi ne aiki to yanzu sai ka ganshi haka haka nan kuma zaka tashi.

Usman : Ba wani bayani?

Shafi'u : Sai ka ganshi to amma ba wani abu.

Mallam : Ido da ido?

Shafi'u : To abun mamaki. Mu dai mun rasa abin da ya faru. Ko dai wani ne ya shiga gabanmu?

Usman : Kuma duka wani wanda ka sani. In dai dan siyasa ne muka ce salamu alaikum zai miko mana hannu har mu samu, amma yanzu sai dai ]aga hannun daga nesa.

Shafi'u : E! akwai wani wanda yake neman takara a lokacin sahun gada yake zama in an zo sallah a masallaci amma yanzu sahun ba yake zama don kar mutane su ganshi ta yanda da an yi sallama daga sallar sai ya saka takalminshi yayi gaba.

Mallam: Allahu Akbar.

Usman: Ko addu'a ma baya tsayawa yi.

Shafi'u: To yanzu dai Mallam, so muke a roka mana Allah ya zamanan…

Mallam: Na dai fahince ku.

Usman: Kowa muka tunkara yasa hannu a aljihu ya ciro ku]i ya ba mu.

Shafi'u: Yauwa, kwarai kuwa, an saba kuma abin amma…

Mallam: To amma Shafi'u da Usman tun da Allah yayi ku ya kaddara samunku da rashinku, abinda yayi nufin zaku samu babu wanda ya isa ya hana, babu kuma wanda zai baku abinda ba'a kaddara maku ba.

Shafi'u: To amma ai ance a yi addu'a ko?

Mallam: Ei, kwarai kuwa Addu'a tana da amfani kwarai da gaske.

Shafi'u: To amma na ji kana karya mana guiwa ne.

Mallam: A' a a a, ai ita addu'a ana so ka dunga yi ne, ba sai kana cikin matsala ba.

Usman: To yanzu dai Mallam me ake biya abin hasafi na addu'a?

Mallam: A'a ya zan fadi? Ni nake biyan bukatan ? ai bani nake biyan bukatan ba. To ni dai zan gaya ma Allah don shi ne ke biyan bukata.

Shafi'u: To ba aiki muka saka ba?

Mallam: To in an sani aiki ai ba ni nake biyan bukata ba, ni iyaka ta da ku alkawarin da na ]auka naku zan gaya ma Allah don in sauke.

Usman: Wato kai dai baka yanke abinda za'a baka kenan.

Mallam: To ya zan yanke? Inda zan yanke da sai ince ku je wurin wane ya ba ku kaza.

Shafi'u: Kwarai da gaske. Mallam amshi wannan, ba'a fa nema da sanya.

Mallam: Kwarai da gaske, Mallam don Allah a taimaka mana.

Mallam: A'a ba komai in Allah ya yarda ba ma ni ka]ai zan nema Mallam Nasiru da Mallam Bala, domin mu taru mu gaya ma Allah, duk wanda kuka tunkara bama gidan Gwamna ba ko wane ne.

Shafi'u: Kwarai Mallam Dubu dari, Dubu Dari Biyu.

Mallam: Har ma Dubu Dari Biyar insha Allahu.

Shafi'u: To madalla, Allah ya saka da alheri amin.

Mallam: To Allah ya rufa asiri (Tafiya).

**Shiga ta Uku**

(A ofishin Gwamna)

Gwamna: To ina jinku Dattijo.

M. Bala: To abin da ya zo da mu mai girma Gwamna, mun zo ne domin ina son in yi maka tuni ne, don kasan lokacin da ake neman alfarma wajen jama'a lokacin zabe kenan. To ni ne nake wakilcin mutane a wannan shiyyar namu. To gashi yanzun an gama komai an zauna kuma kasan lokacin da kake neman wannan takara ka yi ma jama'a alkawura cewa zaka yi masu

kaza da kaza, to yanzu sun sa ido kuma kasan in wani abu ya taso mu za'a nufa da shi.

Gwamna: *Yes.*

M. Bala: To sai aka ga duk alkawuran da aka yi babu wanda aka duba, shi yasa mutane suka fara damuwa, nace to in Allah yaso zan zo in same ka in tuna maka, in an yi alkawari to fa kaya ne ko da shekara nawa to alkawarin na nan, wannan ne yasa nace bari in yi maka tuni ka cika ma mutane alkawuran da aka ]auka, dama wannan ne ke tafe dani.

Gwamna: To Sidi fa?

Sidi: Ya mai girma Gwamna, to duk tafiyar ]aya ce, domin duk yanayin da ake bi baya ne, domin duk lungu-lungu da aka bi da ni aka bi, dama ai duk fatawar iri ]aya ce zancen alkawuran da aka yi wa mutane.

Gwamna: To abin da ke tafe da ku kenan? To abin da nake so ku gane shi ne: ku]in da ake samu a wancan lokaci babu a wannan siyasar na biyu, sannan abin da aka samu a da babu shi a yanzu, kuma ni na shiga siyasa ne wato abin da ake cema "Tun ran gini tun ran zane" amma ni ba na so, domin sai ka yi karya a siyasa.

M. Bala: Lallai kuwa, kwarai da gaske.

Gwamna: Dole sai ka yi alkawarin da ba za ka iya cikawa ba, don na tabbata wasu alkawuran da nayi ba zan iya cikawa ba domin in baka yi karya ba, baka yi alkawarin da ba za ka iya cikawa ba, wasu burikanka ba za su cika ba.

Sidi : Mutane ba zasu saurare ka ba, ba za ka samu kuri'un jama'a ba

M. Bala: To amma Yallabai, wannan ai kun ]aure kanku ne, ya kamata ku dunga cewa in Allah ya yarda, kaga in bai yiwu ba dama sun san cewa kace in Allah ya yarda.

Gwamna: A a dama ni na kan ce da izinin Allah a zuciyata, in na yi-na yi sai ince da izinin Allah.

M. Bala: To shike nan Yallabai.

Gwamna: To yanzu dai sai a yi hakuri lokacin da Allah yasa ku]i suka zo za mu duba muga muhimman abubuwan da ya kamata, aje dai a }ara hakuri don Allah.

M. Bala: Sai kuma Magana ta biyu Yallabai.

Gwamna: Ei, ina jinka.

M. Bala: Koda yake naji bayaninka yanzu, amma abin da aka saba yi to ni dai naji shiru kwana biyu.

Gwamna: Ai kaji Dattijo, shi ne abin da na yi maka bayani, abin da ke akwai da yanzu babu su, babu kudi.

M. Bala: Ai mu muna ganin an yi shigan farko da na biyu ba'a bukatan na uku shi yasa ba'a waiwaye mu ba.

Gwamna: A a, zargin da kuke ke nan?

Sidi: Allah ya sani haka muke zargi, don mutane suna cewa da kana da sauran bukatan da ka waiwayesu.

M.Bala: Suna ganin shi yasa aka rike hannu.

Gwamna : A a, wallahi ba haka ba ne, abin da ake samu da, yanzu ba shi kada ku yi wannan zargi.

M. Bala : Amma duk da haka ya kamata abin da aka saba yi mana a yi mana.

Sidi : Kwarai sai an daure.

Gwamna : P.A !

P.A : Na'am !

Gwamna : Don Allah ka kira mana *PAMSEC*.

P.A: To Yallabai, (Tafiya), (ya dawo)Yallabai ga yi nan.

PAMSEC: Ranka ya da]e gani.

Gwamna: Don Allah akwai ku]i wurinka?

PAMSEC: Ei, akwai.

Gwamna: To, kaba Dattijo Naira Dubu Hamsin

PAMSEC: Mallam Balarabe?

Gwamna: Ey, ka ba Baba Sidi Naira Dubu Talatin.

PAMSEC: To Yallabai.

Sidi/M. Bala: To Yallabai mun gode, Yallabai mun barka lafiya.

Gwamna: To Madalla.

**Shiga ta Hu]u**

(ofishin PAMSEC)

PAMSEC: Mallam Balarabe ga Naira Dubu Hamsin ya ce a baka sai tukuici. Sidi ga Naira Dubu Talatin ya ce a baka sai tukuici. Ka san yaba kyauta tukuici.

M. Bala: To ai ni ban gane ba don na riga na yi godiya

PAMSEC: A'a wancan shi kayi wa godiya amma wannan ni zaka ba wa nawa tukuicin.

M. Bala: Au to! Daga bangarena ga Naira Dubu Biyar.

Sidi: To ni kuma ga Naira Dubu Biyu.

PAMSEC: To na gode Allah ya saka da alheri, Allah ya saka da alheri, to shi kenan.

Sidi: Muna godiya (Tafiya).

M. Bala: Kai baka fahimci abinda suke ciki bane domin su ma'aikatan nan albashinsu baya isansu don na fahimci kana son wani bayani shi ne nace bari in maka. Shi ma'aikaci ba wani abu yake samu fiye da kai, don albashinsu baya isansu, ana cire masu harajin ku]in gida, ku]in ruwa da sauransu. Daga }arshe sai kaga basu da wani abin da ya kamata, to irin wannan 'yan buge-bugen da bin na gaba shi ne zasu samu su ]an warke.

Sidi: Yauwa, haka ne? Allah sarki.

M. Bala: Ai kaga ya nuna irin bukatarsa akai, wannan shi ne abin da ke jawo haka don haka suke fama da shi, ka gani.

Sidi: Allahu Akbar, Allah ya }ara wadatamu amin.

M. Bala: Amin ! Amin !!

Sidi: To ni Mallam Bala zan tafi.

M. Bala: To madalla a huta lafiya

Sidi: Amin! Amin!! (Tafiya)

**Shiga ta Biyar**

(A gindan mangwaron gidan Gwamna)

Moda: Mallam Isah naji baba Khaladu yana nema ya fadi wata Magana?

Mal. Isah: Ei,kai ka sani gani yayi gari-gari.

Moda: Gaskiya duk wata hudda da ake yi a gidannan ta tsaya.

Mal. Isah: A'a to ai baka sani ba, sha'anin rayuwar ne ga yadda take, idan kana maganan zafi ne to an kusa ruwa.

Moda: Ka ji ka! Ana maganan zafin aljihu, kana maganan zafin gari, aljihu duk ta tsotse hujewa ma yake yi.

Mal. Isah: Inbanda abin Baba Haladu ba! Muna nan, nan ne fa muke ci muke sha.

Moda: Kwarai da gaske.

Haladu: Su mutanen da suke zuwa mu samu a hannunsu sun daina zuwa, ni sai inga kamar ma ranar Lahadi ne gashi kuwa ranar aiki ne, ko ba haka ba ne Mallam Isah?

Moda: To mai mutum zai zo ya yi, inda ka fito babu, inda ka dosa babu. Mu ]innan da muke gindan mangwaron nan sai dai mu bar ma Allah, in Mangwaro ya fa]o mu ]auka.

Mal. Isah : A a in Allah ya yarda zamu samu ba}i kwanan nan.

Haladu: Kai, Allah ya raba mu da babu, ai babu gaskiya ba ta da da]i. Allah ya kawo mana baki ]aya na alheri amin.

Wasu: Salamu Alaikum.

Moda: Mallam Jibrin Barka da zuwa.

Mal. Jibo: A a Moda barka da rana.
Mal. Isah: A a sannu da zuwa, (kirari) A a ko a kwara sai an danna. Ko a kwara sai an danna kwa]o.
Moda: Dole!
Mal. Jibo: Ai in dai baka ga Moda a gidannan ba bashi garin ne.
Moda: Ai ni in har dai kaga bananan ai dare ne, ko kuma wannan gwamnan bayanan, amma muddin yana nan ko ana ruwa da bakin kwarya ina nan.
Mal. Jibo: Haka yake Moda!
Mal. Isah: Moda a yi masu iso.
Shafi'u: To mu fitar da abin da ke tafe da mu mana.
Usman: Abin da ya kawomu shi ne so muke muga *His Excellency*.
Moda: To ai baka sani ba, saboda sabon da na yi da *S.S*, da *Police* da *Security* na gidannan da na tunkaro sai a bani wuri.
Mal. Isah: Sai a bu]a ma motarka, ba'a tare ta ba.
Moda: Ai na riga na zama ]an gida.
Mal. Jibo: To don Allah muna so muga mai girma *Excellency*
Moda: To don Allah ku ]an yi hakuri ku jira ni.
Haladu: Ku bari ya je ya isar da sa}on kun zo.
Shafi'u: A a dama ai mu muna jira ne.
Mal. Isah : Kai yi sauri kaje ka dawo.
Usman : Amma mun da]e ba mu sadu ba fa (Tafiya)
Moda : Ranka ya da]e ka wuni lafiya?
PAMSEC : A'a Moda! Moda!!
( A ofishin PAMSEC)
Moda: Ranka ya da]e ko *Excellency* yana ciki?
PAMSEC: Ey, yana ciki.
Moda: To don Allah ina son ganinsa ne.
P.A: A a, ka shiga mana.
Moda: To madalla, (Tafiya)
Moda: (gyaran murya), Allah ya taimake ka!
Gwamna: Na'am Moda.
Moda: Allah ya }ara maka sutura, Allah ya }ara maka Imani.
Gwamna: Amin! don nabiyyirrahmati.
Moda: Ranka ya da]e ai ba}i ne suka zo ganinka shi ne nace to bari nayi masu iso, wasu wa]anda aka yi harkokin siyasa dasu ne, suka zo, to shi ne nace su tsaya in sanar da kai cewar su na son ganinka su yi gaisuwa.
Gwamna: To sai ka zama zaginsu.

Moda: To ranka ya da]e duk ba}on da ya zo wurinka gidannan in ban masu iso to mene amfanin zamana a gidannan? Ai ba shi da amfani ke nan.

Gwamna: Wai Moda kai wai me yasa ina ganin kamar kana da hankali, amma baka dashi?

Moda: Ya aka yi ranka ya da]e.

Gwamna: Kullum baka da burin zucci, kullum kana nan kana takama da ni, kullum kuna nan gidan in ba}i sun zo ‘yallabai, ranka ya da]e, Allah ya taimakeka, ‘Yallabai ya sanyi! ‘Yallabai ya zafi? Da sun zo. Yallabai a sauka lafiay har gindan moto. Shin wai baka tunanin wata rana Moda? Shin in ba ni gidannan ya zaka yi?

Moda: Ranka ya da]e wannan ai daban ne.

Gwamna: In gari yawaye kaje ka samar ma kanka abin da zaka yi ka ci da kanka ko kana nan gindana, to yau in aka ce ba wannan gidan ya zaka yi?

Moda: Wannan fa daban, amma ranka yadade tun da kana nan wallahi ba zan iya barinka ba, ai bani iya rabuwa da kai wallahi, indai kana gidannan kana gwamna.

Gwamna: To in bani Gwamna fa?

Moda: To sai in nemi wani hanyar daban.

Gwamna: Yau idan aka ce Allah ya dauki Gwamna Iro, zaka bishi ne?

Moda: A a sai mu yi maka addu’ar halin da ka yi nagari ya bika ya raka ka gidanka.

Gwamna: Moda don Allah a rage **mutuwar zuciya**.

Moda: To ranka ya da]e ya zamu yi?

Gwamna: Ka rika tsayawa kana nema, amma ina amfanin kullum ka rinka tsayawa nan, ni aikin da nake yi kuna hana ni, kullum kuna wannan wurin ga wannan yazi ga wancan ya zo, alkawuran da na yi wa jama’a baku bari ni na ida masu ba, kun hana ni inyi aiki, shin zan ji da kune ko ko da aikin da aka rantsar dani akai

Moda: E! to za kai aiki Yallabai amma jama’a kake ma aikin kuma jama’a suka zabe ka.

Gwamna: Je ka ce su shigo.

Moda: To, yallabai.

Gwamna: A’a mutane ku hana ni in yi aiki kullum wadannan su zo wancan *gruoph* su zo wancan gruph su zo.

Mal. Jibo: *Your Excellency* ranka ya da]e barka da aiki.

Gwamna: Mal. Jibo barka da zuwa, Shafi’u barka da zuwa.

Shafi’u: Ey ranka ya da]e ya aiki ya gwagwarmayar siyasa?

| | |
|---|---|
| Gwamna: | Alhamdu Lillahi. |
| Shafi'u: | Kai amma ranka ya dade na dade ban zo nan ofis ]in ba, mun kai wata shida ba mu yi ido biyu dakai ba sai dai in ganka a moto ka wuce. |
| Gwamna: | Tun lokacin da ku ka zo murna ke nan? |
| Shafi'u: | Kwarai da gaske. |
| Mal. Jibo: | Kasan gwagwarmaya da mu ka yi na Siyasa |
| Shafi'u: | Ai wannan ba a tunawa, shi ya sani, ya san komai game da yanayin siyasar da ake ciki da jama'a a yanzu, kar ma ka yi wahalar ba shi labari |
| Usman: | Lokacin wani marakunyar yaro ya kai mana saran a kwanta sannan na samu na sace akwatin |
| Shafi'u: | Kasan kuwa har lahira yai niyyar kaika |
| Usman: | Da shike dai da rabon shanruwa |
| Mal. Jibo: | Da muma ko lokacin bukatarmu ka sami wannan kujera kuma Allah ya yi ka zama Gwamna |
| Gwamna: | Allah sarki. |
| Mal. Jibo: | Har yanzu naga yaron sai na Harare shi. |
| Shafi'u: | Kwarai. |
| Usman: | Ya aiki ranka ya da]e? |
| Gwamna: | Aiki Alhamdu Lillahi. |
| Shafi'u: | Da ma gani nai mun da]e ba mu sadu ba ne shi ne muka ce bari mu zo mu yi gaisuwa. |
| Gwamna: | Allah sarki, na gode. |
| Mal. Jibo: | Gaisuwa ne kawai muka zo yi. |
| Gwanma: | Na gode, Kaman kwana biyu kuma kwa sake dawowa. |
| Shafi'u: | Musamman musamman muka zo gaisheka don mu kai wata biyu muna wannan ko}arin sai yau Allah ya yarda. |
| Gwamna: | Ey! Ban zauna ba ne wallahi, bayan kwana biyu ku dawo ku kewayo in sha Allahu. |
| Mal. Jibo: | To wai ranka ya da]e ba ko ku]in moto ne? |
| Gwamna: | Ai kaji, Mallam Jibo kace kun zo bara ne ba kun zo gaisuwa ba. |
| Shafi'u: | Yallabai to ai gaisuwan kenan. |
| Gwamna: | Kace gaisuwa da rokon iri kuka zo. |
| Usman: | Ai 'Balbela sai ta bi shanu sannan ta sami abinci'. |
| Gwamna: | Ai ko kare ta bi yana tada fari ta samu ta ci (kira P.A!) |
| P.A: | *Yes sir,* |
| Gwamna: | *PAMSEC* yana kusa? |
| P.A: | Ey, *PAMSEC* yana kusa. |
| Gwamna: | Yi mana Magana da shi (ya tafiya) |

| | |
|---|---|
| PAMSEC: | *Your Excellency* (gaisuwa) |
| Gwamna: | Akwai ‘yan sauran ku]i nan? |
| PAMSEC: | Ey, akwai. |
| Gwamna: | To don Allah ka samu ku]in mota ka ba su Mallam Jibo. |
| Mal. Jibo: | Mun gode, mun gode ‘yallabai. |
| Shafi’u: | Mun barka lafiya Allah ba da sa’a. |
| Gwamna: | A’a mutane kun hanani aiki. |

**Fitowa ta Shida**

| | |
|---|---|
| P.A: | *Your Execellency*, wasu mata ke jiranka. |
| Gwamna: | Kai billahillazi da Gwamnan kasuwa na tsaya kowa ya fito ya ganni a fili gani nan da ya fi. |
| P.A: | To ya zaka yi tun da Allah ya baka mukami, ha}uri zaka yi |
| Gwamna: | Kullum so suke *Hypertension* ya kama ni? Sun hanani yin ma mutane aikinsu, sai wannan *group* su zo wancan su zo? Na gaya maka wallahi idan da akwai gwamnar kasuwa to da shi na nema, kowane ]an iska yazo ya ganni kuru-kuru. Su wane ne kuma? |
| P.A: | Wasu mata ne. |
| Gwamna: | Ce masu su shigo. |
| P.A: | To ku shigo. |
| Mata: | Salamu Alaikum, Salamu Alaikum… |
| Gwamna: | Shugaba? |
| Shugaba: | Allah ya ja zamaninka ya biya bukata. |
| Gwamna: | Amin, yauwa sannunku, lafiya lau, aiki da godiya, na gode |
| Mata: | Allah ya taimake ka |
| Gwamna: | Shugaba ai kun yawa, da kun koma kun na]o guda ]aya (*you are too many*) |
| Shugaba: | Ai ba komai maganar ba mai tsawo ba ne |
| Gwamna: | To mene ne? |
| Shugaba: | Gaisuwa ne dai da rokon iri ranka ya da]e. |
| Gwamna: | Ai kaji, kash! |
| Shugaba: | Yallabai ya za’a yi |
| Salamatu: | Wato yanzu ne muka yi yawa ko? Amma ai lokacin zabe bamu yi yawa ba. |
| Shugaba: | Bai kamata ki fada mai haka ba, ai shi ba yaro ba ne ya san komai. |
| Gwamna: | Ai yanzu gwamnati nake ma aiki, nan ofishin Gwamna ne. Kai mene ne dai ko ko dai... |
| Shugaba: | Munzo gaisheka muna gaisheka da aikin da kake mana. |

Gwamna: To ai da gida kuka tarad da ni da yafi.

Shugaba: Yallabai ma je gida ga inda zamu sami 'yan ku]in moto, in mun je gida ai ba za mu samu ba.

Gwamna: Kai na gode fa ( kira P.A!)

P.A: *Yes sir.*

Gwamna: Don Allah kira mana *PAMSEC*

Salamatu: Allah yasa ba]i kai ne a wannan kujerar

Gwamna: A'a, ba amin ba. Na gaji wallahi.

Salamatu: To Allah ya raba ka da aikin gwamnati lafiya.

PAMSEC: Ranka ya da]e.

Gwamna: Akwai wani abu ne nan wurinka?

PAMSEC: Ey, akwai.

Gwamna: To lallai ka zo ka sallami su shugaba.

PAMSEC : Matan jam'iyya ne ? Sannunku da zuwa.

Mata : Mune gamu mune har da 'ya warda ne kwarai gashi har da bare-bari acikin mu.

PAMSEC : To gashi Gwamna ya ce a baku sai ku ]un]unka.

Mata : To madalla mun gode, kai amma fa tamfar tana da kyau.

Gwamna : *Oh ! God* wannan abu ya yi mini yawa, wannan ya zo wancan ya zo, wancan *grouph* su zo wancan *grouph* su fita, kai PA !

PA : *Yes Sir,*

Gwamna: Ka kiramana *PAMSEC.*

P.A: To ranka ya da]e.

## Shiga ta Bakwai

(A ofishin Gwamna)

PAMSEC: (Gyaran murya) *your excellency*

Gwamna: Mallam Shehu gaskiya na gaji abin nan ya ishe ni

PAMSEC: Ranka ya da]e

Gwamna: Kiranka na yi ka bani shawara an zabeni in yiwa mutane aiki amma mutane sun hanani yin aiki, kullum *grouph* su zo wancan ma su zo su fita, kuma ba da wani tunani sai dai *personal matter* nasu ba wai kan aikin da ya shafi mutane ba, to gaskiya abin ya yi mani yawa shi ne na kiraka a matsayinka na tsohon ma'aikaci ka ba ni shawara.

PAMSEC: To an bar shiri tun rani.

Gwamna: Assha! Assha!!

PAMSEC: An bar shiri tun rani wato tun lokacin da ake kanfen wanda suke binka sune wanda suka zama uwa da uba a wurinka domin su zasu kawo maka kujera, da suka kawota sai kaga bai kamata

ka barsu ba, kowane yana ta}ama shi ya fasa akwati ko shi ya sace akwati ko a gidan shi ne aka shirya yanda za'a yi, ko nine na tada fa]a a wurin don kada a yi zabe sai dare ya yi.

Gwamna: Kwarai duk su Mallam Jibo haka suke fa]i, to yanzu ya za'a yi a rabu da su?

Mal. Shehu: Ai zai yi wuya, ni fa ma'aikacin gwamnati ne ba ]an siyasa ba ne

Gwamna: Ai duk ina da labari, kwarai har da wannan mahaukacin Moda

PAMSEC: To ai da gaskiyanshi, shi da ake wani yaro yaso ya sare kanshi ta kan ya hana a fasa akwati.

Gwamna: To ai mune na gaban Gwamna! Ko kara muka gilma mai ba zai tsallaka ba haba! Haba! Ai abin ya yi yawa.

PAMSEC: To ai kai ka sake 'Yallabai.

Gwamna: To yanzu ina mafita, ya za muyi mu tsaida wannan abu?

PAMSEC: To na farko dai asa lokacin ganinka daga lokaci kaza zuwa lokaci kaza, kuma a wannan lokacin babu wani aiki da zaka yi in sun kai dubu minti ]ai-]ai, iyakaci ke nan kuma amsarka ey ko a'a, zan maka ko ba zan maka ba, sai kuma wa]anda kuka taso tare ko wa]anda suka ranta maka ku]i kayi kamfen. To wa]annan ko tataunawa zaku yi sai ku yi, amma ba…

Gwamna: To ni zan sa a buga a manna a baki }ofa.

PAMSEC: Amma ranka ya da]e kayi hakuri kar kace na zake, gaskiya in ba haka aka yi ba ba zai yiwu ba.

Gwamna: In maida ganina kawai ranar Juma'a daga safe zuwa lokacin masallaci

PAMSEC: In kuma ka sa haka kar ka canza, sai kuma in an yi ba}i daga wani wuri daban ba 'yan siyasa ba.

Gwamna: Sai in manyan baki ne, sai in karbe su in ba haka ba kuwa sai juma'a, juma'a.

PAMSEC: Da masu zuwa maka firar banza da wofi, da masu firar babu gaira babu sabab.

Gwamna: Zauna gari banza zaka ce.

PAMSEC: A'a zauna gidan gwamna banza dai, in basu ka dakatar ba, ba zaka huta ba, amma kayi hakuri fa!

Gwamna: A'a, ai haka za a yi, zan sa masu gadi su sare mani mangwaronrin gidannan

PAMSEC: To ai ita suke sha kafin ka fito ka sallamesu, da safe ai ita suke sha muna ganinsu ta taga

Gwamna: Mangwaron da safe? Subhanalillahi! To Allah wadan mutuwar zuciya

PAMSEC: In rana ta yi kuma su sha inuwa.

Gwamna: To na gode in Allah yaso haka zamu yi, zan yi *proper arrangement,* in Allah ya so haka zan yi, in manyan ba}i sun zo ga yanda zan yi, zan gyara wannan na gode fa.

PAMSEC: To ranka ya da]e, in dai ba haka ka yi ba ba za ka samu nasara ba har abada. Ko za ka sake shiga wani zaben ne nan gaba, to in ka gyara gaba ai sai baya tayi kyau.

To Jama'a a nan muka kawomaku }arshen wannan wasa namu da muka sa ma suna : **MUTUWAR ZUCIYA** A cikin shirin namu na Duniya Budurwar Wawa.

.

# GUDUNMUWAR SAMANJA MAZAN FAMA WAJEN BUN{ASAR WASAN KWAIKWAYO: NAZARI KAN WASU WASANNINSA.

**NA**

**RILWANU  TANIMU UMAR**

**SASHEN HARSUNA DA AL'ADUN AFIRKA,**
**TSANGAYAR FASAHA,**
**JAMI'AR AHMADU BELLO, ZARIYA.**

**JUNE,2011**